[8/1, 9:34 PM] Billy S Fari: *GONAR SHARRI...!*

*ƳAN TAGWAYE BIYAR*
(Batch C)

NA

*BILLY S FARI*💎
Da
*HAJJA CE*👈
Areewabook@billysfari

Page 1..

Tunda ta nufo cikin parlorn gabaki ɗaya hancinsa ya shaƙo masa lafiyayyun ƙamshin turarukanta masu matukar daɗi, gabaki ɗaya sai yaji tamkar bai shafa nashi turarukan ba saboda yadda nata ya yi bala'in yin tasiri a gabaki ɗaya wajan. Zaune Alhaji Sha'aban Sada yake akan 2seater hannunsa riƙe da wayarsa yana dannawa wanda shigowarta yasa shi ɗago kansa yana kare mata kallo mai cike da soyayya. Kyakkyawar mace ƴar gayu da kuma ƙwalisa da kallo ɗaya zaka yimata kasan don abun duniya ya tattara gareta, Murmushi suka sakarwa juna a lokacin da ta gama ƙarasowa inda yake yana ɗan matsawa can gefe alamar tazo kusa dashi ta zauna. Wani kallo tayi masa wanda yasa shi sakin ƙawataccen murmushi tare da maida kansa yana kallon side table ɗin da ya janyo zuwa gabansa wanda yake cike da tarin dukiya akai da alama amfani zai yi dasu. Zama Hajja Maimoon tayi tare da rungume shi tana kwantar da kanta saman kafaɗarsa cikin kulawa, hannunsa ta kamo cike da hikima da soyayya tana matsa su cikin nata. Sumbatar hannun tayi kafin ta ɗan ɗago kai ta kalleshi tana yatsina fuska kamar shagwaɓa take fadin.

"Ya Habiby shine ka gudo nan ko?" Murmushi Alhaji Sha'aban Sada ya yi yana dawo da kallonsa gareta, ta lumshe ido zuciyarta cike da tunanin mai zai yi da uban kuɗin nan haka dake gabansa? Matse hannunsu da ya yi ne yasa ta dawowa cikin hayyacinta. Cike da sanin yakamata domin Alhaji Sha'aban mutum ne da yasan kansa yasan kuma mutunci da karama na iyalinsa yake faɗin.

"Nan na taho ina jiran Irfaan ya ƙaraso." Murmushi ta saki tana sake kallan uban kuɗin dake gabansu, bataki a bar mata su ba gabaki ɗaya dan tsab zata iya ɓatar dasu a yau ɗin nan ba tare da ta jinkirta ba, tana mamakin yadda mijin nata yake da uban arziki amma kuma baya sakar mata su tayi yadda takeso. Sai dai duk abinda take buƙata yana batashi, takan tuna maganar ƙawarta da take cewa.

_"Kinsan fa ƴan kasuwa basu sakarwa matansu kuɗi haka kawai dole sai da dalili, ki dinga yi masa dabara kina kwakular rabonki idan ba haka ba babu abinda zaki tara a tare dashi."_

Murmushi ta sakeyi zuciyarta cike da tunanin yadda zata fisge rabonta kafin ta bari a fitar da su daga gidan. Yadda ta sauke numfashi a saitin kunnansa sai da yasanya Alhaji Sha'aban lumshe idanunsa yana jin wani irin abu a jikinsa zummm. Ta lura da yanayin da ya shiga dan haka ta sakar masa hannayensa tana jingina bayanta jikin kujerar da suke, da tsantsar kulawa take masa magana.

"Ya Habiby yauma aikin ladan za'a yi kenan?" Yace,

"Wannan aikin na wajibi ne Hajiya za'a kaiwa." Wani abu mai zafi ne ya daki cikin zuciyarta dama tun kafin ya faɗa tasan cewa Hajiyarsa za'a kaiwa, haushi da bakin ciki suka cika mata zuciya. A duniyar nan tana matukar kishi da matar nan saboda irin kulawar da Alhaji Sha'aban yake bawa Hajiyarsa a wajan Hajja Maimoon tayi yawa, gabaki ɗaya idanunta kullewa sukeyi ta manta da matsayin matar a wajan mijin nata. Shi kuma baya haɗa komai da mahaifiyarsa dan wani irin girma da soyayya mai matukar burgewa ce tsakanin su. Kasa haɗiye bakin cikin nata tayi, sai dai bata yi magana ta yadda zai gano akwai wani bad thing a maganarta ba tace.

"Ya Habiby kenan, Allah ya rabaka da Hajiya lafiya. Kana ji da ita matukar ji dan ni kam ban taɓa ganin namiji irinka mai ji da mahaifiyarsa ba. Amma Ya Habiby sai naga kamar kana cikawa Hajiya kuɗi bayan kuma baka barta da rashin ci ko sha ko sutura ba, ni sai naga kamar kuɗin da kike aika mata dashi is too much, kasan kuma ba wai ita ke amfani dasu ba." Tayi shiru tana fatan samun nasarar maganganunta suyi tasiri a gurinsa. Sai da ya juyo ya kalleta tare da sanya tausassun hannayensa ya kamota zuwa jikinsa yana sake shaƙar ƙamahinta da yake saukar masa da wata irin kasala yake faɗin.

"Basu yi yawa ba Madam, waɗannan ba komai bane da zan bawa Hajiyata, duk wani abunda zan bata bazan iya biyanta da abubuwan da tayi min ba. Za'a kai mata idan tace sunyi kaɗan Madam dole zan ƙara mata saboda komenene na zama a yanzu itace mutum ta farko da ta bani gudummawa ba tare da gajiyawa ko gori ba." Tunda ya furta idan Hajiya ta nemi ƙarin wasu kuɗin akan wannan na gabanta da za'a akaiwa Hajiyan, gabaki ɗaya hankalin Hajja Maimoon ya sake tashi. Ƙanƙance idanuwa ta shiga yi tana jin zuciyarta tamkar zata fito. Karan hancinta taji yaja tare da sumbatar saman hannunta da yake riƙe dashi yana cewa.

"Ko duka arzikin da Allah ya yi min Hajiya tace na bar mata su zan bata babu gaddama bare kuma ɓata rai." Duk yadda Hajja Maimoon take jin kamar zata mutu saboda yadda yake nuna kamar mahaifiyarsa tafi ta, sai kawai ta daure sosai tana sake shige masa take cewa.

"Masha Allah haka ake so ai Ya Habiby." Tayi shiru bata ƙarasa abinda ke ranta ba saboda tana son tayi amfani da damar itama ya wawuro wani abun a cikin kuɗin ya bata. Ta buɗe baki zatayi magana Irfaan ya fara knocking, Alhaji Sha'aban ya ɗan saisaita kansa yana kallan ƙofar tare da bada izinin a shigo. Cikin girmamawa ya gaishe su suka amsa Hajja Maimoon sai hararasa takeyi tana miƙewa tsaye, zuwan Irfaan tasan ba zata samu ko naira biyar ba, idan kuma an bata Irfaan yana komawa gida zai gayawa mahaifiyarsu. Ficewa tayi bayan ta ƙudiri aniyar

karɓar nata dan ba zata taɓa hakura ba.

———

Iya karfin ta take amfani tana dirzar tiles ɗin dake jikin bangon bathroom ɗin, gabaki ɗaya ta haɗa zufa tana yi hawaye masu zafi suna gangarowa saman fuskarta. Sai da ta tabbatar da cewa ya fita yadda duk bala'i ba za'a iya dawo da ita baya ba sai idan suna son kuma bata wahala, sannan ta saka bayan hannunta tana sharce gumin da yake tsatso mata a saman goshinta. Handshower ta janyo bayan ta kunna ruwa ya fito ta shiga ɗauraye tiles ɗin kafin ta sake ɗakko sosan da ruwan da ta haɗa kumfar taje tana sake dirzar cikin standard jacuzzi ɗin wanda yake fari ƙal dashi. Yadda taji an buɗe ƙofar an shigo ne yasa ta juyowa a firgice dan ba ƙaramin tsora taji ba. Wani kallo da take yi mata ne yasa ta sauke kanta ƙasa tana jin wani irin tashin hankali yana shigarta dan bata san laifin da za'a ce tayi ba yanzu. Cike da wulakanci da ƙaskanci take kallonta tana sake ƙarewa bathroom ɗin kallo.

"Yauma sai da kika sa na taso ko? Wai Jauhar me yasa baki da tunani ne na tashi da wuri kiyi mana abunda yakamata? Mtwww dallah can ki ɗauraye zan shigo nayi wanka ƴar ƙauye kawai." Tana gama maganar ta juya tana banko ƙofar. Da kallo Jauhar tabi Suhana wacce zata iya cewa kaf cikin yaran gidan tafi su saukin kai a hakan. Sauri tayi ta shiga wankewa tana sake wanke sink da shower tare da duk abin ya dace a wanke a cikin ɓanɗakin. Sai da ta gama sannan ta ɗakko towel ɗin da ake goge bathroom ɗin nan ma ta goge ko'ina ta saka bathroom freshener. Sai da ta kusan fitowa daga ciki tana riƙe da handle ɗin ƙofar ta sake kallon ko'ina, ita kanta sai da tayi murmushi ganin ya yi kyau sannan ta rufe. Jikinta ciwo yake sosai burinta ta zauna ta huta, kallon gadaje guda ukun dake jere a cikin ɗakin tayi tana kallan masu yin bacci akai. Ina ma ace itama tana da gatan ta zata ganta tana bacci so compartable koda ba a irin wannan gidan ba. Jiki babu karfi taje zata fita harta murɗa handle taji an kirata da sigar da tafi tsana wato.

"Ke..!" Ras kirjin Jauhar ya wani irin bugawa, zuciyarta ta harba tamkar zata yo waje. Ta daɗe tana kokawa da numfashinta yadda zata samu karfin zuciyar da zata jurewa abinda wacce ta kiratan zata yi mata. A hankali ta juyo tana kallon wacce take kwance a kan gadon tsakiya, yadda take haka ta juyo ta ganta bata motsa ba idanunta kawai ta buɗe.

"Zoki yi min tausa jikina ciwo yake mun." Jannat ta faɗa tana sake maida idanunta a hankali ta rufe tamkar ba ita tayi maganar ba tana sake bajewa akan ƙawataccen gadon nata. Hawaye Jauhar taji sun zubo mata wanda tana da tabbacin na bakin ciki ne, a girme tasan ta girmi Jannata dan ta bata shekaru biyu suna gidan akaiwa Jannat birthday ɗin 12 da 13years ita kuma yanzu haka 15years take dashi. Amma yadda ta rainata take kuma wahalar da ita tare da kyamatarta kaf gidan babu mai yi mata kalar na Jannat ɗin. Karasawa tayi wajan gadon tasa hannunta akan ƙafafuwan Jannat ɗin zata fara matsa mata kawai taji tana.

"Ahhh." Tare da ɗagowa ta hankaɗa Jauhar ɗin. Gabaki ɗaya tayi baya ta faɗa ƙeyarta ta buge da gadon Suhana. A gigice Jannat ta shiga cukuikuyewa a duvert tana sake sakin ihu tamkar wata wacce take ganin abin tsoro.

"Menene wai Jannat? Me tayi miki?" Sohana ta shiga tambayarta ganin yadda ta gigice. Kafin tayi magana Hajja Maimoon ta shigo cikin ɗakin.

"Meya faru?" Ta tambaya tana nufar Jannat dake takure. Jikinta ta janyo ta a ruɗe tana duddubawa ko zataga wani abun, ganin babu komai yasa ta sake tambaya.

"Jannat menene?" Cikin kuka Jannat ta fara magana.

"Gatacen daga cewa ta matsa min ƙafafuwa na kawai tazo tana shafa min ruwan hannunta, gashi hannun da mugun sanyi." Ta ƙarasa faɗa tana shigewa jikin Hajja Maimoon wacce tsabar ɓacin rai har kamanninta sun soma canzawa. Furucin Jannat yasa Jauhar saurin kallon inda suke zaune tana ware idanuwa jin sharrin da Jannat keyi mata. Yadda taga Hajja Maimoon ta ɗora Jannat a jikinta tana lallashi ne yasa Jauhar kasa yin magana sai hawaye da yake zubowa daga idanunta tasan yau kam ta shiga uku saboda ta saka shalelen gidan kuka. Suhana ce ta dafe kirji tana yin wulli da duvert ɗinta, sakkowa tayi daga kan gadonta ta nufi inda Jauhar ke duƙe a ƙasa ta fisgota da karfi. Jauhar ta kalli Hajja Maimoon dan ganin reaction ɗin ta, ga mamakin ta sai taga ta ɗauke kai tana kwantar da Jannat a hankali tamkar wata kwai da ba'a fatan ya samu matsala.

"Gaya mana muji aiki kika zo ko kuma kashe mana ƴar uwa? Kinsan ai tana fama da limoniya shine kika zo zaki ƙarasa ta ko?" Ko kafin Jauhar tace wani abun tuni taji an wanke fuskarta da wani gigitacen mari wanda yasa ta manta da kanta na tsawon sakanni. Muryar Hajja Maimoon ce ta dawo da ita cikin duniya da kuma hayyacinta inda taji tana cewa.

"Da alama bakin cikin ganinsu kike yi ko?" Kuka ya kwacewa Jauhar tayi saurin toshe bakinta da tafukan hannunta tana girgiza kai.

"Ƙarya kikeyi shegiya mayyar yarinya, to ina faɗa maki idanunki ya fita daga kan mutanan gidan nan domin su ba watsatsu bane ba kamar ke dan nasan ke kanki kinga alamar hakan. Idan kuwa kika sake ɓatawa wani rai a gidan nan ina tausaya miki Jauhar domin sai na lahira ya fiki jin daɗi. Kije kiyi warming hannunki sannan kizo ki mata abinda takeso kafin kiga ɓacin raina, ƙazama kawai." Ta faɗa tana yi mata kallo mai cike da tsana. Gabaɗaya tazame mata kadangare bakin tulu ta rasa yadda zatayi da ita, Banda kaddara ita kam bataga dalilin da zai sa taci gaba da ganin yarinyar nan a cikin gidanta ba. Da gudu Jauhar ta fice daga ɗakin, kitchen ta shiga tare da fashewa da wani irin kuka mai sosa zuciya. Gudun kada ta sake janyowa kanta yasa tayi saurin ƙarasawa ta kunna cooker gas, jikinta yana rawa bata dena kukan ba ta fara gasa hannunta, saboda hankalinta baya jikinta yasa ko zafin wutar bataji, kalmar watsattsiya yafi komai taɓa mata zuciya. Sam bataji motsi ba sai ji tayi an saukar da hannunta daga wajan wutar, tayi saurin ɗago fuska tana ɗora jajayen idanunta akan fuskarsa. Waigawa tayi ta kalli ƙofar shigowa ganin babu kowa yasa tayi saurin durƙusawa har ƙasa tana gaishe dashi. Kallanta yake cike da mamakinta kafin ya miƙa mata hannu alamar ta bashi nata ya ɗago da ita amma taki yadda.

"Bakya tsoron ki ƙone?" Taji ya faɗa cikin tattausar muryarsa.

"Ina son busar da hannu na ne." Jauhar ta faɗa tana fatan ya fita daga kitchen ɗin kafin azo a ganshi a ciki. Kallanta ya yi sosai yana son ya gano wani abun a tattare da ita. Ganin zai bawa kansa wahala yasa shi janye hannun yana zuba su cikin aljihunansa.

"Aikin gidan nan ya miki yawa ke kaɗai Jauhar." Ya faɗa cike da nuna kulawarsa agareta. Lumshe ido tayi tana jin muryarsa tana ratsa mata cikin kai, tunani ta shigayi ina ma ace yana da iko akanta tasan tabbas zai kaita duniyar da tafi ta yaran gidan nan, sai dai sanin hakan bazai faru ba yasa tayi saurin miƙewa dan kada tayi laifi, bata kalleshi ba kanta yana ƙasa tace.

"Zanje na ƙarasa aiki." Tana faɗa ta juya zata fita Suhana da ta shigo kitchen ɗin ganin wanda yake ciki yasa ta saki murmushi tana ƙarasawa wajansa.

"Uncle Irfaan." Tausassar ajiyar zuciya ya sauke bayan ya ɗauke idanuwansa daga kan Jauhar da yabi da kallo har ta fice yana cewa Suhana.

"Doughter kin taso baccin?"

"Eh Uncle Irfaan Ina kwana?"

"Lafiya kalau ina sarkin rigimar gidannan Jannat?"

Yaƙare zancen yana ficewa daga kitchen ɗin ba tare daya tsaya jiran jin amsa daga gareta ba.

#A heart touching story
#Gonar Sharri..
#Hajja ce
#Billy s Fari
#Ƴan Tagwaye
[8/1, 9:34 PM] Billy S Fari: *GONAR SHARRI...!*

*ƳAN TAGWAYE BIYAR*
(Batch C)

NA
*BILLY S FARI*💎
Da
*HAJJA CE*👈
Arewabooks@billysfari.

Page 2..

Da sauri Jauhar ta nufi cikin ɗakin tana gudan karta sakeyin wani laifin, sai dai duk da hakan sai da ta tarar da wani ɓacin ran dan tana shiga ta tarar da Hajja Maimoon tana yiwa Jannat tausa da kanta sai wani shafa mata gashi take tana yi mata hira. Nan da nan Jauhar taji wani abu ya taso mata tun daga ƙasan zuciyarta har saman harshenta, tsayawa kawai tayi tana kallon su kuka na shirin zuwa mata. Idan tace zuciyarta bata sosu ba tabbas tayi ƙarya, tana son ganin itama ana treating ɗinta kamar yadda ake yiwa ƴaƴa sai dai bata da wannan gatan, gatan ta ɗaya shine ta zauna a gidan nan taci gaba da bauta kamar yadda ta taso tun tana ƴar ƙaramar yarinya. Da sauri ta ƙarasa wajan ta durƙusa saitin kafafun Jannat tana ƙoƙarin yin abinda aka umarce ta, jikinta yana kyarma zuciyarya na rawa tace.

"Mommy kawo naci gaba da yi mata." Hajja Maimoon ta watsa mata wani banzan kallo ranta a matukar ɓace tace.

"Menace miki akan kirana Mommy?" Tasa hannu ta shaƙu wuyan Jauhar kamar zata kasheta dan ta tsani taji itama ta kirata da Mommy ji takeyi kamar ta kasheta. Jauhar ta shiga kakarin amai tana kuma ƙoƙarin kwacewa amma ta kasa. Hajja Maimoon kamar zata haɗiye zuciya tsabar ɓacin rai da yarinyar ke sakata ta, da kallon ki shiga taitayinki ta bita tana faɗin.

"Idan na sake jin wannan ƙazamin bakin naki ya kuma kirana da Mommy sai na fasa shi, sannan ki tashi kije kitchen Jannat zata wainar fulawa ta man gyaɗa." Jauhar ta mike jiki babu kwari tana haɗiye kukan da yake neman kwace mata. Idan tace bata nadamar zama tare da mutanan gidan nan tayi ƙarya, ji takeyi gwara rayuwar da ta baro dan ko babu komai wahalar da take sha a nan bata kai tacan ba. Kafin zuwanta gidan takan samu hutu tayi bacci da sauran wasu abubuwan na rayuwarta da takeyi. Amma nan ta rasa a wane situation zata saka kanta. Sohana ce tare da Uncle Irfaan a tsaye bakin kitchen ɗin hakan yasa ta kasa ƙarasawa, bata da matsala da Irfaan amma idan taje zata ratsa su tasan tabbas sai Sohana tayi mata abinda zai taɓa mata zuwa. Gefe guda kuma tsoran kar lokacin kiranta ta kawo wainar ya yi take, idan tace bata gama ba case, idan tane farawarta kenan shime ya zama case. Irfaan yana hangota ya kirata ta isa wajan cikin sanyin jiki. Shi fa yana mamakin yadda yarinyar take gidan nan amma bata gaba bata baya kullum jiya iyau, idan ya lura ma kamar kayanta kala uku ne dan sune zagaka tana ta sakawa. Sai da ta ƙaraso wajan ta durkusa har kasa kanta yana kallan tiles ɗin dake malale a wajan, ji tayi yana yiwa Sohana magana.

"Wai babu kayan da zaku iya bawa Jauhar ne a cikin naku?" Kallonta Sohana tayi kafin tace,

"Mommy ce take kyauta da tsofaffin kayanmu idan muka cire."

"To me yasa ba'a bata? Gida bai ƙoshi ba za'a kai waje? Ko kece bakya so Jauhar?" Yayi maganar yana kallon Jauhar da har lokacin kanta ke ƙasa. Da sauri ta girgiza masa kai, ita gaba ɗaya wannan tsare tan da yayi ba ƙaramin ɗaga mata hankali yake yi ba, sam zuciyarya

taki nutsuwa a wajan bare har ta fahimci irin karamcin da Irfaan ɗin yake shirin yi mata. Ganin kamar uzuri takeson yi a kitchen ɗin yasa ya bata hanyar da zata wuce, Jauhar tamiƙe jiki a sanyaye ta shige cikin kitchen ɗin ta soma haɗa kayan haɗin wainar fulawa ɗin wacce gabaki ɗaya hankalinta yana kan ganin ta shiga ta fara. Shi kuma palour suka nemi waje suka zauna da Sohana suna cigaba da firarsu wanda ko mintuna goma ba'a yi ba ta ƙwalawa Jauhar ɗin da har ta soma soya wainar fulawar kira. Da sauri Jauhar tafito taƙaraso wajen tana ɗan sinne kai take cewa.

"Gani." Ba tare da Sohana takalleta ba tace,

"Ki wanko mana fruit ki kawo mana ni da Uncle." Jin wani aikin take son bata yasa kirjin Jauhar ya shiga bugawa, ta rasa me suka ɗauketa tamkar wata inji kowa ya tashi bata aiki sai ya rufe ido ya kasa hango wanda takeyi a lokacin. Duk da tasan abinda zata furta bai zama lallai a karɓi uzurin nata ba, duk da hakan ta daure tace,

"Amma Jannat nake soyawa wainar fulawa kada ta ƙone, bari na ɗan ƙarasa sai na wanko nakawo maku." Da sauri Suhana tayi mata wani mugun kallo tace,

"Mene? Ni zan saki aiki ki tsaya kawomun excuse? Ke wace? har kin isa Jauhar?"

"Kiyi haƙuri." Jauhar tafaɗa tana juyawa tabar wajen. Suhana ta bita da tsaki ranta a ɓace. Kallonta Uncle Irfaan yai yace,

"Sohana me yasa ke bazaki tashi kije ki wanko fruit ɗin kisha ba idan kina ra'ayin sha? ko ni kinji nace miki inada ra'ayi ne? Wai neyasa bazaku ji tausayin yarinyar nan ba Sohana? Ko kun manta kuma mata ne za'a iya yi muku duk abinda kuka yimata ko yiwa ƴaƴan ku?."

"Tufar da yawun bakinka Irfaan, in sha Allah hakan bazata faru ga yarana ba, ko ka manta ba matsayinsu ɗaya da ita ba? Sannan kuma bazasu taɓa zama ɗaya ba saboda su suna da gata." Irfan yajiyo muryar Hajja Maimoon dake sakkowa daga stairs riƙe da hannun Jannat, Hajja Maimoon na faɗa ta bayansa. Juyowa yai yana kallonsu fuskarsa ba yabo ba fallasa har suka ƙarasa sakkowa daga stairs ɗin suka ƙaraso cikin palourn, Jannat ta taho da sauri tana shigewa jikinsa tana faɗin,

"Uncle Irfaan welcome yaushe kazo ban sani ba?" Sai da ya saki murmushi yana riƙe da ita yake cewa,

"Taya zaki sani kina can kina zubawa Mommynki sangarta, kar dai nace sai yanzu kika tashi daga baccin?" Dariya ta sakar masa tare da kallon Mommy dake zaune ta ɗora ƙafa ɗaya akan ɗaya tana wurgawa Irfaan ɗin wani mugun kallo mai cike da tsana wanda ba kowa ne zai iya fahimtar hakan ba.

"Mommy wai yanzu na tashi?" Jannat tafaɗa aɗan shagwaɓe tana turo baki. Murmushi Mommy

ta saki tana cewa,

"Ƙyale Uncle kin riga kowa tashi a gidan nan ciki kuwa har dashi." Dai-dai lokacin Jauhar tafito ɗauke da wani kyakkyawan tray daya ƙawatu da kalar gold sai ƙyalli yakeyi da fruit aciki ta kawo gaban Suhana ta ajiye ta juya gabanta na wani irin faɗuwa ganin Mommy da Jannat a wajen kasancewar bata kammala aikin da suka saka ta ba,

"Ke!" Taji Muryar Jannat tafaɗa cikin tsiwa. Jauhar tayi saurin rufe idanuwanta ɓacin rai yana sake wanzuwa cikin zuciyarta,

"Ina wainar fulawata baki soya mun ba ko?" Sanin Mommy na wajan, sannan Sohana ma tana nan yasa Jauhar sanyaya murya tace.

"Kiyi haƙuri saura kaɗan naƙarasa." Jauhar tabata amsa cikin marairaicewa tamkar mai yin magana da babba lokacin datake juyowa. Kuka Jannat ta saka tana buga ƙafafuwan ta nufi wajen Mommyn tasu tana cewa,

"Mommy zan mutu yunwa  fa nake ji." Wata uwar tsawa Mommyn ta dakawa Jauhar da tayi tsaye tana kallon ikon Allah. Hajja Maimoon ranta a ɓace tare da jan Jannat ajiki take cewa,

"Uwar me kika tsaya yi da bazaki je ki ƙarasa ba yanzunnan ki kawo mata?" Sum-sum Jauhar taja ƙafafuwanta tabar wajen tana share ƙwallor da suka zubo mata, Mommy tayi tsaki tana cewa,

"Shashashar yarinya kawai, sorry my Baby yanzunan zata kawo miki kici kinji ko?" Taƙarasa zancen tana ɗago fuskar Jannat ɗin tana share mata ƙwallar da ta fara ɓata mata fuska. Ƴar ajiyar zuciya Irfan ya sauke tare da kallon Mommy yace,

"Abunda yaran nan naki sukeyi yayi yawa fa, ke Sohana ina jin ke kika sata aiki amma kina ji anayi mata faɗa bazaki iya faɗar ke kika sa ta ajiye aikin da aka sakata ba tayi naki?" Yayi maganar yana kallon Sohana da take turo baki.

"Look Irfaan koma meye yakamata tasan aikinta da yadda zata iya aiwatar da kowane aka sata cikin lokaci, zata zauna gidan ubansu ne tana ci da sha mai kyau taki yimusu abinda suke buƙata? Impossible dole takoyi yin komai in time yadda ake buƙata koda kuwa duk yaran gidan sun sakata yin wani abun." Mamaki ya kusa kashe Irfaan jin abinda matar Yayan nashi take faɗa. Cike da ɗaurewar kai na kalaman ta yake cewa.

"Amma aikin ne naga kamar yayi mata yawa, suma mata ne is good ace suna koyar yin wasu abubuwan da kansu ba tare da anyi musu ba." Ran Hajja Maimoon ya soma ɓaci da yadda Irfaan ke nuna mata kamar bata iya wasu abubuwan ba, cike da isa da kuma iko take cewa.

"Me kake so kace min ne Irfaan? Nabar yaran nawa marayun Allah su shiga kitchen saboda ita?

Na kalli Habiby da wace fuska kenan bayan ga wacce ke aikin? Impossible wallahi dole kafahimci wutsiyar raƙumi tayi nesa da ƙasa domin akwai tarin banbanci sosai tsakaninsu da ita."

"Allah ya kyauta, amma hakan ba so bane, dan na tabbata idan mahaifiyarsu na raye wannan iskancin baza suyi ba kuma ta ɗaure musu ƙugun yin rashin mutunci."

Irfan yafaɗa yana jin ba daɗi aransa tare da miƙewa tsaye, hakan yayi daidai da fitowar Jauhar ɗauke da tray data ɗora plate ɗin wainar fulawa akai tare da yaji agefe da kayan miya da albasa data yayyanka akai. Cike da tausayinta yabita da kallo har ta ajiye plate ɗin akan side table ta janyoshi zuwa gaban Jannat dake zaune kusa da Hajja Maimoon ɗin da kalaman Irfan ɗin suka gama ƙona mata zuciya ta cika tayi fam kamar zata fashe. Yana ƙoƙarin fita muryarta ta dakatar dashi da take cewa,

"Me kace Irfan? Da mahaifiyarsu na raye kenan so kake ka nuna musu duk abinda nake musu bana sonsu tunda bani na haifesu ba?." Kamar ba zai waigo ba sai yaji yana so ya bata amsa, dan haka ya ɗan juyo yana kallanta yadda zatafi fahimtarsa yace,

"Ko ɗaya ban faɗi haka ba, yadda kike kula dasu tare da basu gata nasan zai yi wahala yaya yasamu matar da zatayi musu hakan, sannan kar hakan yasa kiriƙa mantawa da cewa ƴaƴa mata ne su kuma gidan wani zasu je, bawai ki ɗaure musu ƙugun ba ana wulakanta yarinya tare da bautar da ita sai wacce a girme sun girmeta idan aka ɗauke Jannat." Sallamar Yayan nasa Alhaji Sha'aban daya shigo cikin palourn yasa yakasa ƙarasa maganarsa haɗe da ɗan rissinar dakai yana yi masa sannu da shigowa. Kukan da yaji Hajja Maimoon tafashe dashi ya sashi kasa amsa gaisuwar ɗan uwan nasa tare da ƙarasawa ciki wajenta da sauri ya janyota zuwa jikinsa yana kallon Irfan ɗin yake cewa,

"Irfaan meke faruwa? Me akayi take kuka haka?" Har Irfaan ya buɗe baki zaiyi magana yaji Jannat na cewa,

"Dady Uncle ne yasa Mommy kuka wai ba itace ta haife mu ba shi yasa bata samu aiki."

"What?" Alhaji Sha'aban yafaɗa da karfi yana ɗago kansa daga kallon Jannat da yakeyi ya maida wajan Irfaan. Ransa a ɗan ɓace yake magana,

"Irfaan wannan wane irin shashancin ne kayi haka? Na ɗauka kana da hankali ashe sam ba kada wayau? Meye Maimoon bata yiwa yaran nan? Wallahi ko Hajiya Maryam mahaifiyarsu ke raye iya gata da soyayyar da zata nuna musu kenan! Bana son tashin hankali da damuwa acikin gidana kada kasake yin hakan kuma maza kabata haƙuri yanzun nan." Mamakin yadda Yayan nasa ya rufe ido yake faɗa ba tare da yaji ta bakinsa ba yake, cikin son kara kansa yace,

"Yaya nifa ba.." Bai ƙarasa ba Alhaji Sha'aban ya dakatar dashi,

"Bana son jin komai daga gareka kabata haƙuri nace maka." Alhaji Sha'aban ya yi maganar cikin ɓaci ran daya bayyana ƙarara akan fuskarsa, dan idan har yace kalaman ɗan uwan nasa basu ɓata masa rai ba to tabbas yayi ƙarya don bashi kadai ba hatta ƴan uwa da mutanen gari shaida ne akan soyayyar da Hajja Maimoon ta ke nunawa yaran nasa ta gaskiya. Ba tare da Irfaan ya ɗago kai ya kalleta ba yace,

"Kiyi haƙuri." Sannan yafice yabar gidan yana mamakin makirci irin na mace. Alhaji Sha'aban kuwa ɗakinsa yaja Mommy suka shiga ya zaunar da ita bakin gado ya shiga rarrashinta, daƙyar ya samu ta tsayar da hawayen dake fita daga cikin idanuwanta, reƙa fuskarta ya yi yakai hannunsa yana ɗauke mata ƙwallar yake cewa,

"Haba gimbiya keda ke fama da irin Jannat baki taɓa gajiyawa ba balle har zuciyarki tayi raunin da zakiyi kuka sai Irfaan? Shima fa har yanzu yaro ne bai kamata ace kin kula da maganganunsa ba." Lafewa tayi a jikinsa tana faman sauke ajiyar zuciya tamkar wacce aka ɓatawa rai da gaske, cikin sanyaya murya tare da son sake shiga cikin zuciyarsa take faɗin.

"Haba Habiby taya zai ce wai idan mahaifiyarsu Sohana na raye bazata barsu haka basa aiki ba, meye amfanin mai aikin da muke da ita da kuma arzikin da kake dashi idan har baza a tausayawa yaran nan ba su huta?."

"Kiyi haƙuri, nasan halin Irfaan bai faɗi hakan dan ya ɓata miki rai ba, shi da kansa yana faɗa min cewa ba ƙaramin sa'a nayi ba da Allah ya bani mata kamarki ba saboda yadda kike son yaran nan bakya nuna musu banbancin cewa yaron wata ne kin riƙe su da amana."

"Amma kuma gashi yana ganin laifina yanzu, ni dama nasan kawai baya sona sun riga sun tsaneni."

"Kidena wannan zancen babu wanda ya tsaneki acikin ƴan uwana duka suna sonki kamar yadda kike son su." Wayarsa ce dake gaban aljihu ta ɗauki ƙara ya fiddo ta tare da saurin ɗagawa ganin mai kiran, cikin girmamawa haɗe da russunar da kai tamkar yana agaban mai kiran yake cewa,

"Barka da rana Hajiya ya ƙarfin jikin?" Ta daga can ɓangaren ta amsa masa cikin kulawa da girmamawa,

"lafiya ƙalau alhamdulillah Ɗan albarka naga saƙo Irfaan yakawo. Nagode Allah yayi albarka ya ƙara buɗa maka."

"Amin Hajiya duk dai lafiya kuke ko?"

"Lafiyarmu ƙalau ya iyalin naka da sarakunan jin magana?" Ɗan murmushi ya saki tare da cewa,

"Duk lafiya ƙalau muke Hajiya, in sha Allahu anjima zamu shigo su gaisheki tunda yau weekend ɗin ke ƙarewa gobe kuma sai makaranta."

"To ba laifi Allah ya kaimu agaishesu."

"Zasu ji Hajiya, in akwai wani abu da kike buƙata kiyi magana da Irfan zai kawo muku." Cikin jin daɗi mahaifiyar tasa da ako yaushe takeyiwa Allah godiya daya bata ɗa tamkar da dubu da baya da buri irin yaga ya kyautata mata tare da sakata farin ciki tace,

"Bana buƙatar komai yanzu, amma idan hakan ta taso zan sanar masa." Da haka sukayi sallama fuskarsa ɗauke da murmushi ya ɗago kai yana kallon Hajja Maimoon data lula duniyar tunani jin duk uban kuɗin daya narkawa Hajiyar tasa ɗazu har sake tambayarta yakeyi ko akwai wani abu, iskan bakinsa ya hura mata fuska cike da kulawa dan Alhaji Sha'aban wayayyen mutum ne dake da son soyayya da kuma iya tattalin macce yace,

"Me kuma Gimbiya ke tunani?" Yaƙarasa zancen cike da kulawa. Murmushi ta ƙaƙaro zuciyarta cike da baƙin ciki tace,

"Ba komai Habiby, bari naje nasa su shirya muje wajen wankin kai da kitso."

"Muje sai na kaiku ko?" Ya faɗa yana miƙewa tare da riƙo hannunta suka fito palourn.

"Suhana, Jannat kuje ku shirya muje wajen wankin kan nan da wuri asamu ayi kitson ko? Oya a yi sauri muje da wuri karmu tarar da layi." Tayi maganar tana ɗaga Jannat dake kwance suka nufi sama dan su shiryo su fito su tafi tunda su kaɗai yake jira. Shi kuma ya zauna tare da ɗaukar remote yana canza channel ɗin cartoon da suke kallo zuwa ta labarai. Bayan kamar mintuna goma sai gasu sun fito gwanin burgewa suna sakkowa tana gyarawa Jannat ƙaramin mayafin dake kanta, idan kaga Hajja Maimoon da yaran bazaka taɓa cewa ba ita ta haifesu ba saboda yadda take basu tsantsar kulawa ta zahiri da kuma haɗini, da yawa mutane suna kallon kulawar tata ga yaran da wata manufa amma har ga Allah iya gaskiyarta take son su da kuma kaunarsu saboda soyayyar da take tsananin yiwa mahaifinsu..

#A heart touching story
#Gonar Sharri..
#Hajja ce
#Billy s Fari
#Ƴan Tagwaye.

*ƳAN TAGWAYE BIYAR*

*GONAR SHARRI*
Billy S Fari & Hajja ce

*IDANIYAR RUWA*
(Mai wuyar toshewa)
Ayusher Muhd & Jeeddah Aliyu

*WATA ALAKA*
Zee Bawa & Stylish bch

*BISHIYAR TSIYA*
(Wanda bai jiba bai gani ba ke girbar ki)
Umm Ashgar & Sadiya Dan.

*TSARIN ALLAH*
(Ba mai iya canzawa)
Asmy b Aliyu & Nana Diso

*ZAI IYA BIYAN*
GUDA 1 akan 500
GUDA 2 akan 800
GUDA 3 akan 1200
GUDA 4 akan 1600
GUDA 5 akan 2000

*BANK ACCOUNT*
8098456130
Opay digital services
Shaidar biya 08098456130

*KATIN MTN*
07065283730
Shaidar biya ta lambar.
[8/1, 9:34 PM] Billy S Fari: *GONAR SHARRI...!*

*YAN TAGWAYE BIYAR*
(Batch C)

NA

*BILLY S FARI*💎
Da
*HAJJA CE*👈
Arewabooks@billysfari

*Assalamu alaikum, a madadin marubuta ƴan tagwaye muna ƙara miko ta'aziyyarmu zuwa ga ahalin Yar uwar mu marubuciya Rahama Nalele, Allah ya jikanta ya kai haske kabarinta, haka kuma muna godiya ga yan uwa da abokan arziki da suka nuna mana kauna ta hanyar yimata addu'a Allah ya sakawa kowa da alkhairi, har ila yau muna rokon alfarmar dan Allah duk wanda yaga sakon nan daya sanyata cikin addu'a Allah ya sadata da Rahamarsa yasa aljanna ce makomarta.* Ameen suma Ameen mungode👏*

Page 3..

Murmushi yai yana hangosu tare da ajiye remote ɗin ya miƙe yana miƙa wa Jannat hannunsa ya riƙota yana cewa.

"Iyyee yarinyar Mommy wannan kwalliya haka, gyaran kai za'a je ko dai gasar kyau?." Dariya Mommyn tayi tana gyara mayafin jikinta take cewa,

"Duk wanda ka zaba Dady." Lokaci ɗaya kuma tana ƙwalawa Jauhar kira Jannat ko ta riƙe hannun mahaifin nata tana shigewa jikinsa cike da jin kunya. Mommyn bata rufe baki ba Jauhar dake kitchen ta ɗora abincin rana tafito da sauri ta duƙa gaban Hajja Maimoon tana cewa,

"Gani Mommy.." Tun kafin taƙarasa faɗa Hajja Maimoon ɗin ta buge mata bakin tana cewa,

"Uwar waye Mommyn taki? ban faɗa miki bana son kina kirana haka ba dan ubanki? Sannan waye kika barwa palourn nan ya gyara da kika tafi kika barshi haka baki kwashe waɗannan kayan da suka gama amfani dasu ba?" Cikin ruɗewa Jauhar take cewa,

"Kiyi haƙuri." Jauhar tafaɗa ɗage da bakinta dake mata raɗaɗi saboda zafin dukan data kai mata batare data sarar ba, dama tuni Alhaji Sha'aban Sada yayi gaba shi da yaransa zuwa katafaran compound ɗin gidan, dan haka Mommy taja tsaki cike da tsana tana kallon yarinyar kafin tabi bayansu. Da kallo Jauhar tabi ta har sai da ta dena ganin kyallinta kafin ta miƙe daga wajan jikinta duk a mace ta fara gyara parlorn.

A bakin wani katafaren wajen gyaran kai da suka saba zuwa Alhaji Sha'aban ya ajiyesu haɗe da juyowa ya kalli Hajja Maimoon yace,

"Ban sani ba ko akwai isassun kuɗi a hannunki, amma ga wannan ki riƙe ku ƙara kuyi amfani dashi." Ya mika mata rafar ƴan ɗari biyar sai sheƙi sukeyi. Amsa Hajja Maimoon tayi tana cewa,

"Kamar ka sani ba kuɗi a account ɗina Habiby gashi naso nima ayimun gyaran jiki, amma bari na bari sai bayan kwana biyu nayi nawa. Mungode Ya Habiby, Allah yaƙara maka buɗi."

"Amin, in sha Allah zan turo miki wasu ta account sai kema kije ayi miki koda zuwa jibi ne, yaushe kike tunanin zaku kammala nazo na ɗaukeku?" Ya tambaya cike da kulawa, dan yadda take kula da al'amransa kaɗai yakan tafiyar da ilaihirin tunaninsa.

"Eh zuwa la'asar dan Suhaila ma munyi waya daga school idan sun tashi lecture zata biyo tanan itama ayi mata, kasan halinta ita da ƙannen nata tamkar kishiyoyi suke."

"Eh to ina ga kuɗin nan baza su isheku ba, bari kawai nayi miki transfer ɗin yanzu." Ya faɗa cikin san ganin basu samu ko wacce irin tangarɗa ba da zata sa su wahala. Nan yaciro wayarsa yafara ƙoƙarin tura mata kuɗin, saurin dakatar dashi tayi tana cewa.

"Kabarshi tunda ni ba yau zanyi gyaran jikin nawa ba kaga sai idan katashi tura min ka haɗa min dana business ɗin da mukayi zancen dakai akan ina so nafara tunda dai yau hidimar tayi yawa ko kuwa?" Bai tanka mata ba har sai daya kammala tura kuɗin tunda dama yafara turawa sannan ya mayar da wayar cikin aljihu yana cewa,

"Ki duba na turo miki dubu ɗari uku da hamsin, dubu ɗari ukun naki ne na gyaran jikin da zakiyi, dubu hamsin ɗin ku ƙara na gyaran kan su Suhaila ɗin tunda har da kitso za ayi, alƙawarinki kuma ban manta ba zan baki ina sane dasu madam." Murmushi ta saki duk da ba haka taso ba a ranta idan ta tuna da tarin kuɗin da ɗazu aka kaiwa hajiyarsa, amma ko yanzu ba laifi tunda ta samu ta fazgi nata rabon ko banza yanzu account ɗinta ya ƙara yin nauyi. Sai data lumshe idanuwa cike da kissa sannan tace,

"Kuɗin nan fa Habiby sunyi yawa, duka nawa za'a kashe wajen gyaran kan nasu? Banda ma ba kuɗi a account ɗin nawa ai da ni ce nan zan biya." Kallanta ya yi itama shi take kallo cike da shagwaɓa ta kawar da kanta tana lumshe ido.

"Shiyasa ai naturo miki da ɗan dama ki samu kiyi saving wani abu a account ɗin, Iyalina kuma Gimbiyata ace account ɗinta empty yake?" Rolling eyes ɗinta tayi cike da jin daɗi dan Idan tana gabansa ji takeyi duk duniya babu wata macce sama da ita, haka ma tsintar kanta takeyi a yanayin ƙaunarsa marar misaltuwa a zuciyarta da bata taɓa yiwa wani mahaluki ita ba aduniya. Sanyaya muryarta tayi sosai haɗe da cewa,

"Godiya mukeyi Ya Habiby Allah ya saka da alkhairi ya tsare mana gabanka da baya ka."

"Amin." Ya amsa mata yana jin daɗin addu'ar tata kafin ya kamo hannunta ya sumbata sannan ta ɓalle murfin motar tafice tana ɗaga masa hannu haɗe da Allah ya kiyaye hanya bayan ta rufe masa ƙofar don tun ɗazu Jannat da Suhana suka wuce cikin shago saloon ɗin.

---

Jauhar kuwa basu daɗe da fita ba wani irin zazzaɓi ya rufeta, daƙyar tasamu ta kammala girkin tafito ta hau gyaran palourn tana yi tana tsayawa har ta kammala sannan ta hau sama ta gyara ɗakin Mommy da na su Jannat, tana sakkowa da niyar shiga nata ɗakin dake nan ƙasa gefen kitchen da ɗakin baƙi jiri ya ɗebeta tayi baya zata faɗi taji an tarota, jinta ajikin mutum yasa tayi saurin juyowa cikin ƙarfin hali tana ƙoƙarin ja ye jikinta. Cikin tsananin tausayawa Irfaan dake kallonta yace,

"Kiriƙa hutawa mana Jauhar, bakida lafiya ne?" Yayi maganar jin jikinta da zafi yana ƙoƙarin sake kai hannunsa a wuyanta don tabbatar da hakan, sai dai Jauhar tayi saurin janyewa dan bata saba da irin wannan kulawar ba.

"Sorry." Yafaɗa kafin yaci gaba da cewa,

"Ba kida lafiya ne Jauhar?" Yai maganar kamar zaiyi kuka dan ba ƙaramin tausayi ta bashi ba. Jauhar ta ɗaga masa kai hawaye na sakko mata a fuska dan ko magana ji tayi takasa yi. Juyawa ya yi yafice daga gidan yana cewa,

"Ina zuwa."

Bayan minti ashirin sai gashi ya dawo ya tadda ita anan bakin matattalkalar hawa sama  zaune ta ɗora kanta a jikin karfen stairs ɗin hawaye na saukar mata a fuska. Ita kam Allah ma yasani ta gaji da wannan kangin bautar da take ciki, da ace akwai inda zata iya guduwa daya fi mata zaman gidan nan tayi tafiyarta ta huta, iyaye garkuwa ne kuma rahama amma bata san wane laifin tayiwa iyayenta ba takasa samun wannan garkuwa daga wajensu suka zabi takure rayuwarta a haka tun tana ƙarama har kawowa girmanta. Bata san meyasa aka haifeta ta cikin iyaye marasa tausayi ba. Irfaan ya kwashe mintuna uku yana kallon kyakkyawar fuskar tata wacce yake da yaƙinin idan har ta samu kwanciyar hankali da nutsuwa kyawunta sai yafi haka fitowa. Kallonta yake yi sosai da yake ganin gaba ɗaya bata cancanta da zama cikin irin wannan rayuwar ba kafin a hankali yakira sunanta,

"Jauhar." Ta ɗago kai ta kalleshi ba tare da ta iya cewa komai ba. Irafaan ya miƙa mata maganin hannunsa daya siyo mata yana cewa,

"Karɓi ga magani kisha zaki samu sauƙi kin ji ko?" Ba musu ta miƙa hannu ta karɓa don tasan idan ma bata karɓa tasha ba tofa ko ciwo zai kasheta agidan babu wanda zai bata magani tasha, gorar ruwan dake a ɗaya hannunsa ya buɗe ya miƙa mata takarɓa ta jefa maganin abaki tasha ruwan sosai har sai data shanyesu tas, tana gama sha amai ya taso mata saboda tun safe bata ci komai ba, da gudu ta wuce ɗakinta ta shiga toilet ta amaye maganin da ruwan da tasha tas, a kasalance tasamu ta wanko bakinta tafito ta zube akan katifarta tana fashewa da kuka. Anya rayuwa zata ci gaba da yimata lamunin da zata iya ganin wucewar wannan ƙuncin da take ciki? Anya zuciyarta zata iya ƙarfafa mata iya rayuwa da wannan matar da akullum take hango rashin imani da tausayinta acikin idanuwanta?

Tambayoyin data shiga jefowa kanta kenan cikin tsananin ciwo da damuwa kafin kuma ta samu bacci yayi awon gaba da ita. Irfaan daya kasa matsawa daga inda yake tsaye har yadena jin sautin fitar aman nata ya sauke ajiyar zuciya tare da ficewa daga gidan zuciyarsa cike da tausayinta.

______

Mommy kuwa basu bar wajen gyaran kai ba har sai ƙarfe biyar na marece, cikin motar Suhaila suka nufi wajen kitso dan akwai matar dake yimusu shi yasa basu tsaya anan gidan saloon ɗin ba akayi kitson, wanda Jannat da Suhana kaɗai akayiwa dan Suhaila retouching tayi, sai bayan sallar magriba aka gama hi masu Mommy takira Alhaji Sha'aban ta sanar masa kamar yadda ya buƙata cewa idan angama takirasa. Ba'a jima ba ya iso wajen tunda dama ya san wajen kasancewarsa mutum mai kula da iyalinsa da ɓacin ran mahaifiyarsa bai haɗasu da komai ba shiyasa yake basu cikakken lokacinsa aduk sadda ya samu damar yin hakan. Da gudu Jannat tafito daga cikin gidan bayan ya iso tana nuna masa kitson da akayi mata hadda na gaba da jelolin suka fado mata a fuska kasancewarta mai tsawon gashi fiye da sauran ƴan uwan nata,

"Wow Masha Allah Mamana, anya wannan kitson basai naƙara kuɗi ba?" Nan su Mommy suka ƙaraso su Suhana suka gaisheshi  Mommy ta gaishesa itama yana cewa,

"Mommy da yaranta an kammala ko?"

"Eh Dady."  Ya kalli Jannat dake riƙe da hannunsa yace,

"Oya jeki wajensu Aunty zamu je gidan Hajiya." Sannan ya kalli Suhaila yace,

"Zamu fara tsayawa a ShopRite muyi siyayya kafin muwuce mu gaida Hajiya."

"OK Dad." Suhaila tafaɗa tana buɗe motarta suka shiga ita da Suhana. Jannat kuwa babu yadda Dady bai yi da ita ba taje wajensu Suhana amma taƙi hakan yasa Mommy yin dariya ta janyota ajikinta tana cewa,

"Barmun yarinyata Dady tunda bata son zuwa." Ta buɗe mata bayan mota ta shiga ita kuma ta buɗe gaba ta shiga. Juyowa Dady yai yana kallon Jannat data shige can cikin kujerar baya rike da wayar Mommy ta soma game yace,

"Mamana badai rigima ba ko?" Tayi murmushi kawai ba tare data amsa shi ba tana cigaba da latsar wayarta. Sai da Suhaila tayi reverse ta tada motar ta hau kan titi daidai sannan Dady yabi bayan motar tasu. Tafe suke Alhaji Sha'aban ya juyo yana cewa,

"Yau hidimar yaranki tasa kin manta dani ko abinci baki bani ba."

"Ayya Sorry, amma ina shegiyar yarinyar nan bata baka bane? Naboro ta fa ta ɗora abincin." Da yake yasan da wacce take dan ya saba da jin sunayenta kala-kala a bakin Hajja Maimoon ɗin.

"Ai ban koma gidan ba ne, nabiya campany ne acan nayi sallar magriba." Sai data ɗora hannunta saman nashi sannan tace,

"Sorry nasan muna isa gida ta kammala abincin dare sai muci ko?"

"Ba damuwa." Yafaɗa kafin su faɗa wata hirar har suka iso ShopRite ɗin. A gefen da Suhaila tayi parking motarta shima Dady ya yi suka fito gaba ɗayan su suka shiga yace kowa ya ɗauki abinda yake so. Kowacensu ta ja basket suka nufi ciki, ganin Mommyn tayi tsaye yasa ya kalleta yana cewa,

"Ya dai Mommyn Jannat?" Ta juya idanuwa tare da cewa,

"Kai nake jira muje tare na zaɓa mana namu." Murmushi ya sakar mata suka nufi wajen basket ɗin ta jawo ɗaya tana cewa su tafi. Ganin ya jawo ɗaya ya sata zuba mishi idanuwa tana cewa,

"Habiby wai ko ShopRite fin zaka saye mana ne? Wannan fa zai ishemu."

"Eh ke ki zaɓa mana, ni kuma zan zaɓawa Hajiya nata anan." Ya ƙarasa zancen yana wucewa gaba. Wani irin abu ne yazo ya tsaya mata a zuciya jin abinda yafaɗa kafin tayi saurin bin bayansa tana haɗiye abinda take ji adole. Turarukka masu matukar tsadar gaske agefen exclusive ya zabarwa Hajiyarsa da mayukan shafawa dana wanka, haka ɓangaren kayan ciye-ciye da yasan zata iya ci ko buƙata dan baiwa yara ko baƙi idan tayi duk sai daya kwasar mata. Ita dai Hajja Maimoon na biye dashi da idanuwa cikin wani matsanancin ɓacin rai wanda ita daƙyar ta iya haɗa musu nasu sannan suka wuce wajen payment ya biya inda kayan Hajiyarsa sai da suka kusan ninka duka kuɗin kayan da Suhaila, Suhana, Jannat da ita kanta Mommyn suka ɗauko. Juyowa yai bayan ya yi payment ɗin aka kwasar masu kayan su Suhaila sun wuce gaba an loda masu a mota yana kallon Mommy da tace,

"Waɗannan kayan da kika haɗa mana kina ganin sun isa bazaki ƙara wasu ba idan kina bukata?" Daƙyar ta danne zuciyarta ta ƙaƙaro murmushi haɗe da cewa,

"Sun isa Habiby kar kashe kuɗin suyi maka yawa, dubi bill ɗin da aka haɗa maka akayan Hajiya kaɗai ga kuma namu." Ta faɗa cike da kishi a cikin zuciyarta, gabaki ɗaya mantawa take da wacece Hajiya a wajansa.

"Karki damu, Hajiya ta ko nawa ne zan kashe mata banyi asara ba dan ta cancancesu, haka kuma babu faɗuwa ako nawa zan kashe muku saboda iyalina na kyautatama."

"Haka ne kuma. Muma in sha Allah sun isa Allah yaƙara buɗi." Ya amsa da amin sannan yawuce gaba tabi bayansa. Kamar yadda suka iso haka suka sake jerawa motar Suhaila na gaba ta Dady na bayanta har suka iso gidan Hajiya. Da gudu Jannat ta ɓalla marfin motar ta fice tun daga gate tana ƙwala mata kira.

"Kakata, Kakus.." Murmushi Hajiya dake zaune cikin wani katafaren palour daya gaji da haɗuwa ta saki lokacin da Jannat ta ƙaraso ta faɗo mata ajiki tana faɗin,

"Ja'ira ɗagani kada ki karya ni." Dariya Jannat ta saki haɗe da cewa,

"Kai gradma bani da nauyi fa." Bata rufe baki ba Alhaji Sha'aban Sada daya shigo ya ɗan kaimata ranƙwashi akai yana cewa,

"Ga Mommynki can je ki hau ƙafafuwanta kibarmun Hajiyata ta huta." Sai da Jannat ta ɗan turo baki kamar zatayi kuka kafin tace,

"Dady nima fa Mamanka ce ko Mommy?" Duk aka sa dariya kafin dukansu su shiga gaishe da kyakkyawar dattijuwar wacce da ka ganta zaka san hutu ya zauna mata ajiki bazaka taɓa cewa ita ta haifi Alhaji Sha'aban ɗin ba duk da kuwa ba shine ɗanta nafari ba. Da yake ƙasa take zaune ta mike ƙafafuwa Alhaji Sha'aban ya tankwashe nasa ƙafafuwan agabanta cikin girmamawa yana gaisheta yana mammatsa mata ƙafafuwan haɗe da cewa,

"Hajiya ya ƙarfin jikin?" Cikin kulawa ta amsa mashi da.

"Alhamdulillahi kafin tace,

"Ina kuka tafi Irfaan yace min gidan naku tsit ya isko yarinyar nan mai yimuku aiki ba lafiya?"

"Subhanallahi, bamu sani ba Hajiya ko dama batada lafiya ne Maimoon?" Dady tambaya haɗe da juyowa yana kallon Mommy. Mommy da jin hakan da tayi ko ajikinta yasa ta tace,

"Lafiya kalau muka barota Hajiya har ta ɗora girkin rana, bansan matsalar yarinyar nan sam bata son yin aiki ga shegiyar ƙarya da munafurci wallahi."

"Assha in haka ne kuwa bata kyautawa kanta ba Allah ya sawaƙe, ya ƙoƙari da yara Maimoon?"

"Alhamdulillah Hajiya ya jikin naki?" Mommy tafaɗa tana murmushi,

"Jiki alhamdulillah, Allah yai muku albarka yaƙara muku haƙurin zama da wannan rigimammiyar takwarar tawa, ga wata can miskila da bata son mutane itama." Hajiya ta ƙarasa zancen tana nuna Suhaila dake latsar wayarta tayi kamar bata jita ba. Hira suka ɗan taɓa tace mai aikinta takawo musu abinci duk suka ce sun ƙoshi, Dady ne kaɗai da Jannat suka ce zasu ci dan haka sai da mai aikin ta kawo musu abincin Hajiya takarɓa da kanta ta zuba masa ta tura masa gabansa da ruwan wanke hannu, tare da Jannat suka ci suka gama sannan Dady yamiƙe yana yimata sallama bayan tasa su Suhaila sun kwashe kwanuka sun kai mata kitchen. Har zata tashi Dady yace,

"Hajiya kiyi zamanki bari su Suhaila su kwaso maku sakonki su kawo maki, sai da safe."

"To Allah ya tashemu lafiya. Nagode Allah yayi albarka ya sake wadataka, yadda ka kula dani kaima Allah yasa naka ƴaƴan su kula dakai fiye da hakan." Ya amsa da amin sannan yafice suka bishi abaya.

"Sai da safe Hajiya." Hajja Maimoon tafaɗa itama sannan suka fice. Sai da su Suhana suka gama shigo mata da kayan sannan sukayi mata sai da safe tana sanya musu albarka suma tare da addu'ar Allah ya zaɓa masu mazaje nagari...

#A heart touching story
#Gonar Sharri..
#Hajja ce
#Billy s Fari
#Ƴan Tagwaye

*ƳAN TAGWAYE BIYAR*

*GONAR SHARRI*
Billy S Fari & Hajja ce

*IDANIYAR RUWA*
(Mai wuyar toshewa)
Ayusher Muhd & Jeeddah Aliyu

*WATA ALAƘA*
Zee Bawa & Stylish bch

*BISHIYAR TSIYA*
(Wanda bai jiba bai gani ba ke girbar ki)
Umm Ashgar & Sadiya Dan.

*TSARIN ALLAH*
(Ba mai iya canzawa)
Asmy b Aliyu & Nana Diso

*ZAI IYA BIYAN*
GUDA 1 akan 500
GUDA 2 akan 800
GUDA 3 akan 1200
GUDA 4 akan 1600
GUDA 5 akan 2000

*BANK ACCOUNT*
8098456130
Opay digital services
Shaidar biya 08098456130

*KATIN MTN*
07065283730
Shaidar biya ta lambar.
[8/1, 9:34 PM] Billy S Fari: *GONAR SHARRI...!*

*ƳAN TAGWAYE BIYAR*
(Batch C)

NA

*BILLY S FARI*💎
Da
*HAJJA CE*👈
Areewabook@billysfari.

Page 4..

Kwance Jauhar take ta rasa inda zata jefa ranta, duk da cewa yau masu takura mata basa gidan ta samu peace of mine, Sai dai zazzabin da tayi na yinin da kuma amai yasa jikin nata ya yi weak tun ɗazu bata iya ko motsawa daga inda take kwance ba bare ta iya mikewa. jin an buɗe gate yasa taji kirjinta ya wani irin bugawa tashin hankali ya shigeta har bata san lokacin da ta miƙe tsaye ta fito daga cikin ɗakin nata ba. Cikin sauri ta fice zuwa compound dai dai lokacin da suke ƙoƙarin yin parking ɗin motocin nasu. Ta cikin glass ɗin motar Hajja Maimoon ke hango Jauhar, tun kafin ta fito ta ɗaure fuska dan sai ran Jauhar ya ɓaci akan sanarwa Irfaan rashin lafiyarta, bataga dalilin da zai sa a dinga yi mata shisshigi a cikin al'amuranta ba. Rasa wanda zata fara tara tayi gashi ita ɗin ɗaya ce amma kowa a cikin su so yake ta bauta masa. Kai tsaye ta nufi motar su Hajja Maimoon kasancewar a dominta ne take tare da yaran gidan.

"Baki ga kaya bane Jauhar?" Cewar Suhaila da take fito da kayan da sukayo shopping na motar ta ganin tana ƙoƙarin wuce su. Kallanta Jauhar tayi tana ƙarfafa zuciyarta dan ita kaɗai tasan irin yanayin da take ciki kafin tace.

"Yaya Suhaila bari na fara zuwa wajan Hajiya sai nazo na ɗauka." Suhaila ta riƙe ƙugunta cike da mamakin Jauhar ɗin, duk da taji yes ya kamata a fara zuwa wajan Mommyn tasu amma yadda takeji da isa akan Jauhar ɗin yasa ta juya tana tafiya take cewa.

"Ke kika sani, idan kinga dama karki kwaso ki barsu anan wajan." Suka shige ciki ita da Suhana daga su sai handbag babu wacce ta ɗauki koda leda ɗaya a cikin su. Sauke numfashi Jauhar ɗin tayi tana kallon ledojin da suke jiranta kafin ta durkusa saitin ƙofar Hajja Maimoon tana jiran fitowarta. Jannat ce ta fito ta cillawa Jauhar ɗin handbag ɗinta batare da tace komai ba ta wuce abunta cikin wata isa. Cike da kasala Jauhar ta ɗauki handbag ɗin daga kan cinyarta ta riƙe a hannunta, babu abinda take jira sai fitowar Hajja Maimoon wacce ke cikin motar tana yiwa Alhaji Sha'aban rigima akan cewa idan suka shiga ciki karya ce zai yi wani aiki ko amsa waya, suna

cikin motar tasa ya yi switch off ɗin wayoyinsa duka yana cewa,

"A'a you wish Mommyn Jannat." ta sakar masa murmushi haɗe da rolling eyes ɗinta. Kusan a tare suka buɗe murfin, Hajja Maimoon har da buɗe ta gefenta duka ta yadda sai da ta bugarwa Jauhar a jiki wanda dama hakan ne burinta. Jauhar bata damu da sosa wajan ba ta shiga yi mata sannu da dawowa amma ko kallon inda take batayi ba tace.

"Ki ɗebo kayan cikin motar." Daga haka ta ƙarasa wajan mijin nata suka jera zuwa ciki. Kallansu Jauhar tayi tana jin hawaye na shirin zuwa mata, tana mamakin yadda duk wani cin kashi da za'a yi mata a gaban mai gidan uffan baya cewa duk da cewa farko yakan ɗan tsawatar da yaran nasa amma daga baya kuma sai taga ya dena, ta kasa gane dalili duk da cewa zuciyarta na gaya mata ƙila Mommyn ce ta nuna masa rashin jin daɗinta akan sassauci da yake ganin ya dace a bawa Jauhar ɗin. Ganin tana ɓatawa kanta lokaci a wajan yasa ta mike tana riƙe da handbag ɗin ta zaro ledojin. Ganin kayan da yawa yasa ta rataya jakar Jannat a kafaɗarta ta ɗauki nasu Hajja Maimoon ta nufi ciki. Tana shiga parlorn idanun Jannat suka hango mata jakarta a jikin Jauhar. With so much shock ta ware ido tana buɗe baki cike da mamakin Jauhar ɗin. Kamar zatayi magana sai kuma ta fasa ta kumbura fuska ta wuce ɗakin su kai tsaye tana tunanin hukuncin yimata, wata zuciyar ce ke faɗa mata kama da wane ai bata wane, ko babu komai tasan Jauhar harta mutu bazata iya mallakar kwatankwacin irin abubuwan da ta ke dasu ba dan haka zata ƙyaleta for today. Jauhar kuwa sai da ta gama kwaso duka kayan ta shigo dasu sannan ta ɗauki na yaran ta kai musu har bedroom lokacin Suhana tana bathroom tana wanka itama Suhaila ta shiga ɗaya toilet din, Jannat ce kawai ta bararraje akan gado tana ta danna waya dan har lokacin wayar Mommyn tana a hannunta.

Kallon kan Jannat Jauhar tayi, kitson ya yi kyau sosai har bata san lokacin da tasa hannunta ta shafo kanta ba. Tunawa kawai tayi rabonta da kitso irin haka na mutunci ba zata iya tunawa ba, zata iya rantsuwa tunda ta taso ta fara ganinta cikin duniya ba'a taɓa yi mata kitso mai kyau ba. Lokacin da ta fara girma ne take wanke kanta idan ta samu an bata damar yin wanka sai ta haɗa da kan ta wanke. Lokacin da ta fara sanin kanta a hannun Hajja Maimoon tana tunawa bata taɓa bar mata gashinta a kanta ba, yana fitowa zata sanya reza ta kwashe mata shi tasss sai ta maida kan tamkar saɗal sannan take barinta.

"Idan ke mayyace Jauhar haka zaki gama ki rabu dani." Jauhar taji Jannat ta faɗa wacce still idanunta yana kan game ɗin da take bugawa. Kanta ta ɗauke daga kallon dake shiga tsakaninta da Jannat ɗin kafin ta buɗe bakinta da kyar wanda ya yi mata mugun nauyi tace.

"Sorry kitson ne naga yayi kyau, ya burgeni sosai."

"Kinga kuwa har ki mutu bazaki taba ganin irinsa akanki ba koda a mafarki ne." jauhar tasan gaskiya Jannat ta faɗa dan haka ta basar da maganar ta hanyar cewa.

"Ga kayan na kawo."

"Okay handbag ɗina fa kin gama ɗanawa?" Jannat tayi maganar tana juyowa ta kalli Jauhar ɗin a yatsine kamar taga kashi.

"Ya za'a yi na ɗana jakarki Jannat? Kawai kaya ne suka yimani yawa shiyasa har kika ga..." Ƙasa ƙara sawa tayi ganin wani kallo da Jannat ɗin ta watso mata, dan yarinyar akwai tsaurin ido ta raina Jauhar da gaske ba kaɗan ba, ta ɗauketa tsantsar mai aiki shiyasa batayi mata komai da sauƙi. Gyara kwanciyarta tayi tana haɗe fuska take cewa.

"Ai zaki ƙara idan halinki ne, village girl, sannan wai ba zaki dena kiran sunana gatsal ba ko?" Yadda tayi maganar tamkar wata babba yafi komai bawa Jauhar haushi sai dai ko a fuska bata nuna ba gudun abinda zai je yazo.

"Mekike so nace miki?" Jauhar ta tambayeta tana kallonta.

"Hajiya ƙarama, karki sake kirana da Jannat saboda sisters ɗina ba zasu kirani da hakan ba kema kice zaki kira." Jauhar ta buɗe baki cike da mamakinta tana ɗan zaro idanuwa, wato tunda taji Mommy na kafa mata doka akan yadda take kiran sunanta itama kafa mata zatayi? Lallai ma to bazata saɓuba, Jauhar ta faɗa cikin zuciyarta don sam bata ji zata iya kiranta haka ba, babu sunan da zata canza mata bare ta kirata da Hajiya ƙarama. Ba tare da ta kulata ba ta juya zata bar ɗakin. Jannat da nata ran ya ɓaci jin shirun da Jauhar ɗin tayi dake tabbatar mata da cewa ba zatayi abinda take so ba ta bita da kallo. Sai da ta kusa fita dan har ta kusa rufe ƙofar Jannat ɗin ta kirata.

"Ke..!" Kamar ba zata amsa mata ba sai kuma ta dawo ciki tana jiran taji me zata ce.

"Faɗi muji." Da rashin fahimtar inda ta nufa Jauhar ɗin tace,

"Mene?"

"Kice Hajiya ƙarama."

"Bazan iya ba." Jauhar ta faɗa ba tare da ta sani ba, kawai dai tasan zuciyarta a toshe take ba komai zata iya bari ba a wannan lokacin. Suhana ta fito daure da towel a jikinta daidai lokacin kuma da Jannat ta tsaya gaban Jauhar wacce kansu ɗaya dan rashin kwanciyar hankali da tsangwama yasa sam bata wani girma shi yasa Jannat ke ganinta kamar wata sa'arta. Suhaila ma a lokacin ta fito dan tun tana cikin toilet take jiyo maganganunsu ƙasa. Kafin suyi wani abun dan a cikin su ba zasu ce ga wacce ta fara kaiwa ɗaya hannu ba kawai gani sukayi an hau kokawa. Maimakon su rabasu sai duka suka rufarwa Jauhar kamar dama haushinta sukeji. Ana cewa sarkin yawa yafi sarkin karfi hakan yasa suka riƙa jibgarta duk da tana samu ta ɗan rama akan Jannat data saki wata irin ƙara. Hajja Maimoon ta shigo ɗakin da sauri dan yadda sauttin ƙarar Jannat ɗin yakai mata a kunnuwa yasa ta kasa shiga wankan da take shirin yi a rufe ta ƙaraso ciki ɗakin nasu. Ganin yadda Jauhar ke ƙoƙarin ƙwatar kanta a yanzu ta hanyar kai duka ga duk wanda ta samu acikinsu dan tuni Jannat ta gudu yasa ta ƙarasa da sauri ta wani irin

fizgota da karfi ta kira mata mafita har biyu masu kyau tare da hankaɗata gefe. Jannat ta rugo tana kuka ta shige jikin Mommyn tana ɓoye fuskarta.

"Meye nake gani haka a cikin gidan nan?" Tayi maganar tana kafe Jauhar wacce ta buge da jikin bango da ko zafi bataji ba kamar yadda taji zafin abinda Hajja Maimoon ɗin tayi mata yanzu da idanuwanta da suka gama ƙanƙancewa tsabar masifa. Cikin kuka wanda da kyar muryarta take fitowa tace.

"Meye nayi da ba za'a soni kamar kowa ba? Me yasa ake son ganin na zama wahalalliya marar galihu acikin gidannan ake bautar dani? Bazan iya ba nagaji da hakan, Mommy ki maidani wajan Babana na zauna a gidansa kamar yadda suma suke zaune da nasu Baban." Habawa tamkar ta kunnawa Hajja Maimoon wuta a cikin zuciyarta, cikin sauri ta isa wajan da Jauhar ɗin take tare da fisgota, fita sukayi daga cikin ɗakin tana janta tamkar ba ƴar Adam ba. A kitchen ta direta tare da zuwa ta zaro wuƙa da ashana ta dawo wajan Jauhar ɗin dake yashe a ƙasa tana kuka. Cikin wani irin fushi da ɓacin rai Hajja Maimoon ɗin ta kyasta ashanar tana kai wutar saiti fuskar Jauhar, muryarta a kausashe take faɗin bayan ta saka mata wukar a wajen wuyanta.

"Maimata min ki sake gaya min cewa na maidake wajan Babanki ki gani idan ban ƙonaki da ranki ba. Dan ubanki ni zaki kalla kice na maidake? Waye uban naki a duniyar nan Jauhar? Waye shi? Nace wanene shi..!" Ta faɗa a tsawace tamkar kitchen ɗin zai tsage saboda tsananin masifa. Cikin tashin hankali ganin yadda take sake kai wutar wajan fuskarta yasa Jauhar ɗin fara bata haƙuri cike da tashin hankali tana cewa.

"Na dena Hajiya kiyi haƙuri dan Allah bazan sake ba, na tuba bazan koma cewa ki maidani ba wallahi." Cilli Hajja Maimoon tayi da tsinken ashanar ganin ya kusa laso mata yatsun hannu da take riƙe dashi sannan ta koma kai wuƙar wajen wuyan Jauhar ɗin tana ci gaba da cewa.

"Ubanki ba komai bane Jauhar shi yasa bakya gabansa, ni kuma da aka jonawa ke bana ƙaunarki bare na buɗe ido na ganki a inda nake rayuwata bisa baƙar ƙaddara nake zama dake dan babu yadda zanyi, kin zame min masifa, kin zame min bala'i a cikin rayuwata, dole ce ƙanwar naƙi yasa nake tare dake. Amma banda haka Jauhar da tuni ban sanki ba bare nasan inda kike. Karki sake kai ni bango irin haka idan ba haka ba zaki sha mamaki na wallahi tallahi. Banza kawai, ƙazama, sakarai shashasha. Sannan idan kika sake ɗaga wannan ƙazamin hannun naki akan ɗaya daga cikin yaran gidan nan kisan mezai biyo baya." Ta ƙarasa maganar tana wurgar da wuƙar hannunta gefe. Har zata fita daga kitchen ɗin taji Jannat na cewa.

"Mommy kice karta sake kiran sunana idan ba zata ce min Hajiya Ƙarama ba." Hajja Maimoon ta kalli Jauhar cikin ƙasƙantarwa tace da ita.

"Kinji abinda take so ko bakiji ba?" Da sauri Jauhar ta ɗaga kai tana kuma amsawa da bakinta.

"Toh Hajiya." Daga haka ta fice tabar Jauhar zaune a wajan tana kuka mai cike da ɗacin zuciya. Jannat ta zabga mata harara cike da jin haushinta take cewa.

"Kina zaune a gidan mu kina cinye mana abubuwa kice ba zaki yi abinda nake so ba? Toh Allah sai kinyi ko mu koreki mu sake wata." Tana kaiwa nan itama ta fice. Jauhar ta kuma fashewa da kuka tana tunanin wannan wane irin masifa ne? Me yasa Mommy takeyi mata haka? Shin da Babanta ya tashi bar mata ita cewa ya yi kar ta gatanta ta? Shin meyasa ma aka barta a wajanta sai kace ita kaɗai ce a cikin danginsu. Wani kukan ta sake fashewa dashi saboda rashin amsar tambayoyin nata da duk duniya babu inda zata iya zuwa ta samesu in ba abakin Mommyn ba, wanda ta tabbatar da yin hakan a wajenta tamkar gayyato ranar mutuwarta ne, Kasa tashi tayi daga wajan bare ta koma ɗakin da yake a matsayin nata. Kusan a kitchen ɗin ta kwana saboda yadda jikinta ya sake rikicewa, haka ta kwana tana masassara babu wanda ya sani daga ita sai Allahn da yasan manufar zamanta tare dasu..

________

Kwance yake akan gado hannunsa waya ce yana ta danne-dannensa, yadda cikinsa yake ta zafi yasan yunwa yakeji amma wayar ta hanashi zuwa ya samarwa kansa abinda zai ci. Kafin kace menene tuni cikin nashi ya wani irin murɗawa hakan yasa yai saurin kifawa kan gadon har wayar tashi tana sabulewa daga hannunsa. Murkusu ya somayi yana riƙe gefen cikinsa. Shigowar ɗan uwansa ɗakin yaga halin da yake ciki ne da sauri ya nufe shi yana kiran sunansa.

"Zain..! Zain..!!" Shiru ya kasa amsawa dan ko taɓashi ma da ake yi baya so."

"Mama.. Mama Zain zai mutu." Cewar Al'amin da yake ta kiran Maman tasu. Tana parlor suna cin gyaɗa tajiyo kiran, da gudu suka nufi ɗakin Zain ɗin dan ganin abinda yake faruwa. Ganin yadda yake a kife yasa tayi saurin nufarsa tare da ɗagoshi tana tambayar.

"Menene Zain?" Ya shiga girgiza kai yana sake dafe wajan da yake masa zafin.

"Cikin ka ne?" Ya ɗaga kai yana sake lasar lips ɗinsa.

"Kaci abinci kuwa?" Ta sake tambayarsa a karo na biyu tana ɗago fuskarsa.

"A'a Mama please ku kyaleni kawai." Ya faɗa a wahale yana son koma durkushewa.

"Wai me yasa kake neman janyowa kanka masifa ne Zain? Wannan ciwon naka bazai wuce ace ulcer ba ce, so kake sai kaje kayiwa kanka illah sannan hankalinka ya kwanta?." Ta faɗa tana ɗagowa tare da kallo ɗaya daga cikin ƴan matan nata tana cewa.

"Husnah oya jeki haɗo masa abinci yanzun nan, ke kuma Baby haɗo masa tea." Duk suka juya hankalinsu a tashe ganin ɗan uwan nasu a cikin wani yanayi zuwa aiken na mahaifiyarsu. Kusan a tare suka dawo kowa ɗauke da abinda aka ce ya kawo. A gaba ta saka shi ya ɗan sha tea sannan ya ci abincin suna ta yi masa sannu.

"Ka fito parlorn mana ayi hira dakai." Maman ta faɗa tana daukar cup ɗin da ya gama shan tea

ɗin.

"Mama bari na huta." Ya faɗa yana zamewa ya kwanta.

"Nasan ba fitowa zaka yi ba Zain, Allah ya kyauta maka sai kace wata mace kullum kana ɗaki." Bai ce komai ba ganin haka yasa ta fito daga ɗakin tana ɗan korafinta wanda inda da sabo yaci ace ta saba da wannan halin ɗan nata...

#A heart touching story
#Gonar Sharri..
#Hajja ce
#Billy s Fari
#Ƴan Tagwaye

*ƳAN TAGWAYE BIYAR*

*GONAR SHARRI*
Billy S Fari & Hajja ce

*IDANIYAR RUWA*
(Mai wuyar toshewa)
Ayusher Muhd & Jeeddah Aliyu

*WATA ALAKA*
Zee Bawa & Stylish bch

*BISHIYAR TSIYA*
(Wanda bai jiba bai gani ba ke girbar ki)
Umm Ashgar & Sadiya Dan.

*TSARIN ALLAH*
(Ba mai iya canzawa)
Asmy b Aliyu & Nana Diso

*ZAI IYA BIYAN*
GUDA 1 akan 500
GUDA 2 akan 800
GUDA 3 akan 1200
GUDA 4 akan 1600
GUDA 5 akan 2000

*BANK ACCOUNT*
8098456130
Opay digital services
Shaidar biya
07040402434 ko
 08098456130

*KATIN MTN*
07065283730
Shaidar biya ta lambar.
[8/1, 9:34 PM] Billy S Fari: *GONAR SHARRI...!*

*ƳAN TAGWAYE BIYAR*
(Batch C)

NA

*BILLY S FARI*💎
Da
*HAJJA CE*👈
Arewaboooks@billysfari
Page 5..

Haka Zain ya wuni a cikin ɗaki har mahaifin nasu ya dawo gaba ɗaya yaran suka tarbesa da murna da farin ciki. Bayan Mama ta kawo masa abinci da ruwa yaci ne ya kammala yake tambayarta,

"Ina yaron nan ne?"

"Al-amin?." Mama ta tambaya tana ƙoƙarin kwashe kayan abincin dake gabansa,

"A'a Zain dai, wane Al'amin daya bar wajen nan yanzu.!"

"Ai kasan halinsa da zaman ɗaki sai kace sabuwar amarya, yana ɗakinsa yau da ciwon ciki ma ya wuni duk da ina ganin ulcer ce."

"Subhanallahi bai fita wajen aikinsa ba kenan!?" Abban ya tambaya da ɗan ɓaci rai a fuskarsa. Sallamar Zain ɗin tasa shi ɗago kai yana ɗaure fuska, dan idan akwai abinda ya tsana aduniya bai fi yaji ance ɗan nasa bai fita wajen aikinsa ba. Ƙasa Zain ya samu waje ya zauna yana gaida Abban nasu, bai amsa masa ba sai dai yaji ya jeho masa tambaya cikin ɓacin rai.

"Wai me kake son zama ne Zain? Yanzu duk makudan kuɗin dana kashe wajen sama maka aikin nan baza ka tsaya ka maida hankalinka akai ba sai kayi sanadiyar da aka koroka kayi

zaman gidan mai dalili? Menene amfanin wannan rayuwar idan mutum ya rasa madogara? Kar ka manta kai ne madubina kuma madogarar ƴan uwanka tunda kana gani ba wani abinyi ne da ni ba da zan iya ci gaba da riƙeku kafin ta Allah yazo kaina, shi yasa na tsaya tsayin daka wajen ganin ka samu ilimin nan da kuma aiki dan kariƙa taimaka min, Shikenan kuma sai kazo kana wasa bayan kasan kuɗin upper ɗin aikin nan da muka ara aka siya har yau ba'a gama biya ba ko? Wannan wace irin rayuwa ce haka? So kake na fara surutai ni kaɗai ko ya ya?" Jiki babu kwari Zain ɗin yace,

"Kayi haƙuri Abba yau off muke shi yasa."

"Off kuma? Hmmm wai Off..! Shi wannan Off ɗin wai koda yaushe cikin zuwansa ake? Bafa nason ƙarya Zain."

Murmushi Zain yai yana ganin duk wannan faɗan da mahaifin nasa keyi laifinsa ne da bai zauna ya fahimtar dashi yanayin yadda aikin nasu na nurses yake ba, a yadda kuma mahaifin nasu ya wahala kafin sama masa upper dan fara aikin daya haɗa ƙaddarorinsa ya siyar har gonarsa ta gado daya gada iyaye da kakanni ko shine matsayinsa abunda zai yi  kenan koma yayi fiye da yadda yakeyi masa faɗan, saboda kusan dubu ɗari da hamsin mahaifin nasu ya siya masa upper kafin ya samu gurbin fara aiki a asibitin fedral medical center dake nan garin duk da kyan da result ɗinsa ya yi da zamaworsa overall best student of the year, haka yayita zama gidan har na tsawon shekara bai samu aiki ba saboda lalacewar ƙasar tamu har sai da mahaifinsa ya sai masa upper ɗin da kansa. Sanin dalilin yin faɗan Abban nasu yasa Zain sake sanyaya murya akan wacce yake da ita yana cewa.

"Abba ba karya nakeyi ba, ka'idar aikin mu na nurses idan ka kwana biyar kana aikin safe ko rana koma fiye da kwana biyar ɗin to za'a baka hutun kwana biyu kaje ka huta kafin ka ɗauki wani aikin, idan kuma kayi aikin dare na sati ɗaya ko kwana biyar shi kuma hutun sati ɗaya za'a baka batare da kaje aiki ba saboda ka samu karinka baccin da bakayi ba da sauran ƴan abubuwa da kake buƙatar yi, bayan wannan hutun kuma akwai anual leave shima duk shekara muke samunsa sau ɗaya, akwai kuma casual leave da un expected yake zowarwa mutum, kamar rashin lafiya tazo ma mutum ko kuma wani nashi da yazama dole ana buƙatarshi awajen, ko wani abun daban da zai jawo mutum yabar wajen aikinsa bisa dole ba tare da saninsa ba, sai abashi hutun da bazai wuce sati ɗaya zuwa biyu ba. Sai kuma maternity leave, shi kuma nurses mata kaɗai ake bawa shi, wannan yasa zaka ji akai akai ko nace duk sati sai nace maka off nake." Kalaman Zain ɗin sun sanyaya kusan kaso tamanin na zafin da Abban ya ɗauka, dan haka yace.

"Ikon Allah, to ai bayani kake mani tun farko Zain, yanzu inna fahimceka hutun sati ɗayan ne ka samu tunda kwanaki naga aikin dare kayi ko?"

"Eh Abba." Zain ya amsa masa yana murmushi ganin yadda fuskar Abban nasi ta washe. Murmushi Abban shima yai yana sauke ajiyar zuciya haɗe da cewa.

"Alhamdulillah ba laifi Allah ya taimaka yabada sa'a."

"Amin ya rabbi Abba nagode da, kulawa."

"To ya jikin naka naji ance bakaji daɗi ba? Gashi dai kasan illar ciwo amma sai karika wasa da lafiyata, kullum kana ɗaki riƙe da waya kana latsawa, Allah yasa ba haka kakeyi wajen aikin naka ba?" Sai da Zain ya gyara zamansa sannan ya kalli mahaifin nasa yana cewa,

"Alhamdulillah naji sauƙi Abba, ai wajen aiki daban lokacin latsar waya kuma daban saboda bazai yiwu na haɗasu lokaci ɗaya ba, kuma latsar wayar da nakeyi Abba shima wata hanya ce ta samun kuɗi nake amfani da ita, amma dai sai abun ya tabbata tukuna zanyi maka bayaninsa." Daɗi Abban yaji a ƙallah yaji farin ciki tunda riƙe wayar ma ashe kuɗi zai kawo.

"Allah to ya tabbatar da alkhairi."

"Amin Abba." Zain ya faɗa kafin su faɗa wata firar shi da Abban nashi. Zain shine babba awajen mahaifinsa malam Abdallah, shekarar data wuce ya kammala karatunsa na school of nursing, mahaifinsu ɗan kasuwa ne dake sana'ar kayan cosmetic acan cikin kasuwa yake da ɗan ƙaramin shagonsa wanda shine sana'arsa tun ƙurciya har zuwa yanzu da girma ya kamashi, kuma da haka yake ɗaukar lalurar duka iyalansa da kuma karatun ƴaƴansa ta yadda idan kaga family ɗin sai sun baka sha'awa. Husnah ke bi masa dake matakin karshe a Sakandire, sai Al'amin dake SS 1, sannan Khadija, Baby da yanzu ta shiga secondary aji ɗaya. Mahaifinsu mutum ne mai jajircewa akan yaransa haɗe da tarbiya daidai gwargwado kuma iya ƙarfinsa, duk da bashi da tarin arziƙi baza kuma akirasa cikin marasa ƙarfi ba kasancewarsa mutum ne mai zuciyar yi da kuma wadatar zuci. Wannan kenan.

---

Sati ɗaya Jauhar ta kwashe tana zazzaɓi a tsaitsaye wanda hakan baya hana Mommy sata duka aikin gidan kamar yadda ta saba, gabaki ɗaya bata ganin irin yadda ta rame ta fita hayyacinta, idan ma ta lura toh ta shafawa idanunta toka bata mata uzuri kamar koda yaushe. Yau ma tunda asuba take tsaye akan aikace aikacen gidan idan tayi wannan tayi wancan ta gama wannan ta haɗa waccan saboda zuwan yaran gidan makaranta kasancewar yau monday kowacensu da abinda zata ce tana buƙatar tayi mata. Ba ita ta samu ta zauna ba sai karfe tara dai-dai bayan ta tabbatar da kowacensu ta wuce school da abinda fa buƙata. Mintuna uku da zamanta taji sakkowar Hajja Maimoon da maigidan nata daga ɓangarensa sanadiyar firar da sukeyi suna dariya. Da sauri ta miƙe don gaba ɗaya ta manta data kammala haɗa breakfast bata kai kan dining table ta shirya ba. Kayan abincin ta shiga haɗawa a gurguje akan ƙaton tray tafice da sauri ta nufi wajen dining ɗin dasu tun kafin su ƙaraso, tana gama jerasu suna isowa ta koma gefe ta tsaya tana sunkuyar da kanta ƙasa tace.

"Barka da fitowa Mommy ina kwana?" Tafaɗa har lokacin kanta na ƙasa, Hajja Maimoon dake ji tamkar ta hamɓareta ta maka mata harara tana cewa,

"Ke zo nan." Ba tare data amsa gaisuwar tata ba. Gaban Jauhar is a ne yai wata irin faɗuwa ta ɗaga ƙafafuwanta daƙyar ta tako zuwa gabanta. Jawo ta tayi ta duƙar da ita haɗe da sakar mata wani mugun dundu a bayanta lokaci ɗaya tana kai mata ranƙwashi akai tare da riƙe kunnenta ta murɗe tana cewa,

"Wai ke wace irin mayya ce da bakya jin magana? Ban hanaki kirana Mommy ba?" Jauhar da tuni azaba ta gauraye mata jiki hawaye na sauko mata tace,

"Kiyi haƙuri Hajiya mantawa nakeyi."

"Ashe kuwa kin ɗaura aure da wahala dan kuwa daga yau zan fara fasa miki wannan mugun bakin naki mai kama da na munafukai, tashi ki fice min da gani kafin na sauya miki." Jiki na rawa Jauhar tamiƙe zata bar wajen Hajja Maimoon ta daka mata wata uwar tsawa wacce tasa Jauhar ɗin tsayawa cak.

"Wai ke wace irin daƙiƙiyar yarinya ce ne Jauhar da bazaki iya gaida mutane ba idan kin gansu? Ko ni kaɗai kika gani awajen?"

"Dady ina kwana?" Jauhar tafaɗa cikin rawar murya har tana tsittsinkewa saboda kuka. Tsaki Hajja Maimoon ta ja shi kuma Alhaji Sha'aban Sada ya amsa da,

"Lafiya lau, ina yaran sun wuce school ne?"

"Eh." Ta bashi amsa cikin sanyin murya haɗe da juyawa tabar wajen tana jin haushin yadda suke hanata kiran sunayen su kamar yadda kowa keyi, abin nan yana bata haushi matuka. Sai da Hajja Maimoon ta zuba masa abinda zai ci ya wuce office ta turo masa agabansa ya soma ci sannan ya ɗago kai yana kallonta.

"Wai menene matsalar yarinyar nan ne Mommyn Jannat? Naga keda ita sam bakwa jituwa waje ɗaya ko zaki canja ƴar aikin nan ne?" Sai d Hajja Maimoon takai haɗin yankan soyayyen bread a bakinta ta gutsura sannan ta kalli mijin nata cike da so tana cewa,

"Zan so haka Ya Habiby, but karka manta labarin yarinyar nan dana baka, ba tada iyaye garin nan kuma kasan ba ƴan garin nan bane kamar yadda na faɗa maka, matsalata ɗaya itace ina zata tafi idan na koreta daga gidannan? Na tabbatar komai daren daɗewa waɗanda suka tilasta min zama da ita zasu dawo su nemeta, wallahi Ya Habiby na tsani yarinyar nan fiye da tsammaninka, kallonta kaɗai idan nayi sai ya haifar min da damuwa saboda kwata-kwata bana son ganinta, shiyasa nace maka in har kana so na kadena tausayinta zai iya saka nima nazo nafara tausaya mata saboda soyayyar da nakeyi maka tafi komai a cikin zuciyar nan tawa. Kuma wallahi bata cancanci hakan daga wajena ba takowace irin fuska dan mahaifinta bashi da mutunci ɗan akuya ne da bai san darajar ɗan Adam ba." Taƙarasa zancen idanuwanta na kawo hawaye. Damuwa shima Alhaji Sha'aban Dada ya shiga ganin Hajja Maimoon ɗin acikin wannan yanayi saboda ba kaɗan yake jinta aransa ba, tun mutuwar matarsa data barmasa

ƴaƴa yayi tsammanin yai bankwana da farin ciki, amma shigowar Hajja Maimoon rayuwarsa da yadda ta riƙe masa ƴaƴansa yasa ya manta da duk wani raɗaɗin baƙin ciki daya shiga zuwa farin ciki kamar yadda ta ɗora shi, ta haska masa rayuwarsa shi da ƴaƴansa ta kuma basu farin ciki da kulawa marar misaltuwa, shi yasa baya son abinda zai taɓa mata zuciya ko kaɗan. Cike da kulawa yake cewa,

"Sorry Mommyn Jannat, a iya tunanina tunda hannunki ta taso yakamata ko meye kiyimanta kiyi hakuri ba dan iyayenta zaki yi ba please kiyi haƙuri.." Saurin ɗaga masa hannu tayi haɗe da cewa,

"Dan Allah kaima kada ka soma tursasa zuciyata abinda bazata iya ba akan yarinyar nan Habiby, zan so ko Irfaan kayi masa magana yadena shiga shirginta bana so, hakan ne kawai ke sa ina jin sassauci a zuciyata idan ina ganinta cikin kunci da damuwa, domin ta sanadiyarta nima na shiga fiye da irin wannan damuwa da ƙuncin da kuke ganin kamar tana ciki."

"Is ok." Yafaɗa yana ɗan sakata ajikinsa tare da bubbuga bayanta alamar lallashi. Sai da yaga ta koma masa yadda yake so sannan ya ɗauki spoon ɗin dake gabanta ya yanko omalet egg ya kaimata a baki yana cewa,

"Have your food sai ki rakani kada na makara." Ta buɗe baki yasaka mata soyayyen ƙwan yana jan karan hancinta. Sai da ta kammala ta rakashi har bakin mota ya buɗe ya shiga ya tayar yafice sannan ta dawo ta haye sama abunta ba tare da tabi takan Jauhar ba, don da gaske dole ke sa tana jurar kallonta ba dangantakar so ba.

Jauhar na ganin Hajja Maimoon ta haye sama ta dawo ta kwashe kayan takai kitchen ta tatattara sauran abincin da suka rage ta canye ta wanke kayan ta maida kowane inda yake, dama ta gyara kitchen ɗin dan haka ta ɗora girkin rana sannan ta wuce palourn ta gyara ko'ina, tana kammalawa ta haye sama ta gyara ɗakinsu Suhana ta wanke toilet ɗin, sai da ko'ina yayi tsaf sannan ta rufe ƙofar ta koma kitchen tana jiran Hajja Maimoon ta sakko dan ta samu ta shiga gyara mata nata ɗakin. Tana cikin soya miya taji Hajja Maimoon na kwalo mata kira kamar wacce ta rasa idanu cikin wata irin hargatsattsiyar murya dake cike da tashin hankali. Spoon ɗin dake hannunta ne data gama juya miyar ya suɓule ya faɗi ƙasa saboda gigicewa takai hannunta daƙyar ta rage wutar don kar ta kone ta sake shiga wani tashin hankalin sannan da sauri ta fice ta nufi stairs ɗin da Hajja Maimoon ke tsaye ta cika tayi fam sai wani hayaƙi ke tashi akan fuskarta tamkar haɗuwar baƙin hadari tsabar masifa. A gabanta Jauhar ta zube ƙirjinta naci gaba da faɗuwa duk da batasan abinda ke faruwa ba.

"Ina kika kai min gold ɗina?" Hajja Maimoon tafaɗa cikin kakkausar murya tana zare mata idanuwa, wanda hakan yayi daidai da ɗaukewar ji da ganin Jauhar na wasu mintuna kanta na juyawa haɗe da sara mata lokaci ɗaya jin kalaman na Hajja Maimoon da daidai suke da saukar aradu acikin kanta.

"Gold kuma Hajiya! Wane irin gold kuma?" Jauhar tafaɗa cike da ruɗewa tana juya lamarin a

ƙwaƙwalwarta, dan a iya saninta ko inda gold yake ajiye bata taɓa bi ta wuce ba in ba a wuyan Hajiyar ta gansa ba koma yaran gidan, to meye hadinta da shi da za'a tambayeta? fisgota ɗin da taji Hajja Maimoon tayi ta taso ƙeyarta zuwa gaba suna sakkowa ƙasa ya maido da ita daga tunanin da ta shiga yi,

"Na rantse da Allah sai kin fito min da gold ɗina ko nasa kiyi nadamar haihuwarki aduniya yau Jauhar dan bazan taɓa kyaleki ba ɓarauniya mai halin ɓeraye." Wasu zafafan hawaye ne suka samkowa Jauhar tana kallon Hajja Maimoon dake faman turota ƙasa take cewa,

"Wallahi ban ɗaukar miki gold ba Mommy, ban san ma inda kike ajiyewa ba in ba a jikinki na gashi ba.." Kafin ta rufe baki Hajja Maimoon ta kai mata wani wannan bugu a baki tana cewa.

"Ƙarya kikeyi munafukar yarinya duk gidan nan waye ke shiga ɗakunan idan ba ke ba? To wallahi nafison gold ɗin nan akanki dan haka maza muje ki fitomun da kayana." Taƙarasa zancen tana turota da ƙarfi har sai da taga ta shiga gangarowa daga stairs ɗin daya rage musu sauran hawa bakwai su sakko. Tuni goshin Jauhar ya fashe lokacin data ƙaraso ƙasa kanta ya bugi karfen dake jikin stairs ɗin wajen hawa. Cikin rashin nuna damuwa Hajja Maimoon ta sake fisgota daga ƙasan ta turata zuwa ɗakinta, kayanta tasa ta shiga ɗakko mata tana watsa mata su ɗaya bayan ɗaya tana neman gold ɗinta aciki amma bata samu ba, hakan yasa ta nufi wajen ƴar ƙaramar wardrobe ɗin dake jikin ginin ɗakin tana watso sauran kayan Jauhar ɗin da undies, nan ma bata samu komai ba tayo kanta tana faɗin.

"Ina kika je kika ɓoye shi? Muje ki fito da shi tun muna mu biyu Jauhar ko kuma na lahira yafiki jin daɗi acikin gidannan."

"Mommy wallahi ban ɗaukar miki ba.."

"Toh uban waye ya ɗauka Jauhar? ina ke kaɗai ce ke shiga dakina agidannan ko gold ɗin zai dauki kansa ne?" Hajja Maimoon ta katseta a hasale tana yowa kanta wanda hakan yasa Jauhar ficewa daga ɗakin aguje dan ta tabbata komai zata iya yi mata idan tariƙeta acikin gidan nan da suke daga ita sai ita kaɗai. Tana kawowa palour Irfaan na shigowa jikin Jauhar na rawa ta ruga ta ɓuya a bayansa tana neman ceto..

#A heart touching story
#Gonar Sharri..
#Hajja ce
#Billy s Fari
#Ƴan Tagwaye

*ƳAN TAGWAYE BIYAR*

*GONAR SHARRI*

Billy S Fari & Hajja ce

*IDANIYAR RUWA*
(Mai wuyar toshewa)
Ayusher Muhd & Jeeddah Aliyu

*WATA ALAKA*
Zee Bawa & Stylish bch

*BISHIYAR TSIYA*
(Wanda bai jiba bai gani ba ke girbar ki)
Umm Ashgar & Sadiya Dan.

*TSARIN ALLAH*
(Ba mai iya canzawa)
Asmy b Aliyu & Nana Diso

*ZAI IYA BIYAN*
GUDA 1 akan 500
GUDA 2 akan 800
GUDA 3 akan 1200
GUDA 4 akan 1600
GUDA 5 akan 2000

*BANK ACCOUNT*
8098456130
Opay digital services
Shaidar biya
07040402435 ko 08098456130

*KATIN MTN*
07065283730
Shaidar biya ta lambar.
[8/1, 9:34 PM] Billy S Fari: *GONAR SHARRI...!*

*ƳAN TAGWAYE BIYAR*
(Batch C)

NA

*BILLY S FARI*💎
Da
*HAJJA CE*👈

*BOJUWA HERBAL'S & SCENTS*
*Suna kawo Saiwowin sanyi da suke dagargaza sanyin mara da na jijiya.*
*Haka nan akwai dafaffen maganin ga wanda tafi son ready made.*
*Haka nan suna kawo Saiwowi daban daban daga Chad da Sudan, kuma marasa illah*
*Saiwowin tsumi*
*Saiwowin dahuwar kaza/tattabaru*
*Saiwowin matsi gangariya*
*Original gadalin mata*
*Ƴaƴan gadali na asali*
*Original gumba*
*Tsumin Saiwowi*
*Tsumin kwakwa da Dabino*
*Igiyar alkairi*
*Zumar goran tula*
*Hakkin daka na musamman na asali*
*Bayan haka suna dafa kazar amare da masu jego da ma uwayen gida*.
*Akwai bridal package*
*Mai jego package*
*Ƴar gata package*.
*Dukkan kayan kuma available ne for pickup or immediate delivery.*
*A Kano nake amma kuma nationwide delivery ne*
*Ku tuntubi Surayya Halin yau a wannan lambar dan samun naku cikin musulmin farashi*
*08032773332*
*Iyah Basiru na gaisuwa*😅

Page 6..

Kallon yadda jikinta ke rawa Irfaan ɗin yai kafin ya maido da kallonsa wajan Hajja Maimoon dake fitowa daga ɗakin. Tana ganin Irfaan ɗin ta ƙaraso ƙasa da sauri tana cewa.

"Alhamdulillah kazo a dai-dai Irfaan, kai da kake ɗaurewa shegiyar yarinyar nan ƙugu, ka faɗa min duk gidan nan waye zai shiga har ɗakina ya kwashe min gold idan ba ita ba? toh wallahi yau ko ni ko ke Jauhar agidan nan sai kin fito dashi duk gidan uban da kika kai shi." Kasa cewa komai Irfaan yai yana kallon Hajja Maimoon har ta dasa aya sannan ya juya ga Jauhar da har lokacin jikinta be dena rawa ba yana cewa,

"Jauhar ke kika ɗaukar mata?" Yanayin irin kallon da yake yi mata ya tabbatar mata da ɓacin ran dake cikin zuciyarsa, wanda shi bana komai bane illa na zallar bakin cikin ganin halin da ako yaushe idan ya shigo gidan yake ganinta aciki. Cike da tausayinta a zuciyarsa yake jin ina ma yana da inda zai kai ta da ya ɗauke ta daga cikin bala'in nan na gidan ɗan uwansa. Ita kuwa wani kukan ta fashe dashi tana ji aranta cewa shikenan shima ɗin dake ɗan tausaya mata ya

yarda cewa tayi sata, jin bata ce komai ba yasa a ɗan hasale Irfaan yake cewa,

"Ba magana nake yi miki ba?" Wata irin zabura ta sakeyi cike da tsoro ta shiga girgiza masa kai alamun ba ita ta ɗauka ba. Juyowa yai yana kallon Hajja Maimoon yace,

"Kin ji Hajiya ba ita ce ta ɗauka ba. Mai yiyuwa kin sauya mishi waje ne baki sani ba."

"Ahhhh lalai Irfaan! Karya zan yiwa Jauhar ko me kake nufi?" Gyara tsayuwarsa yai cike da gundura da kukan Jauhar ɗin da yake ji yace,

"Bance karya kike yi ba Hajiya amma kiyi tunani tukunna, me Jauhar zatayi da gold idan ta ɗauka tunda babu inda take zuwa? Kuma ga alama kin duba cikin kayanta baki gani ba kinga kuwa idan har ta ɗauka dole zaki gansa a ciki tunda ko nan da gate ba zuwa take yi ba." Wani mugun kallo Hajja Maimoon ta watsa masa haɗe da cewa,

"Yanzu ma dole zan ganshi idan taji ajikinta, idan kina son zaman lafiya acikin gidannan kizo ki faɗa min inda kika kai shi ko wanda kika ba ya ɓoye miki." Hajja Maimoon taƙarasa zancen tana ɗora ƙafarta ɗaya akan ɗaya daga kan kujerar da take zaune tare da ɗauke kanta gefe ganin irin kallon da Irfaan ɗin keyi mata dan dama da biyu tafaɗi hakan. Kallonta sosai yai tare da sakin murmushin takaici ya maida kallonsa ga Jauhar sannan ya juya yabar gidan zuciyarsa kamar zata fito.

"Zaki zo ne ko sai na sameki a wajen nan?" Jauhar dake tsoron ƙarasawa tuni ta shiga tittirjewa ta shiga haɗa hannuwa waje ɗaya tana cewa,

"Kiyi haƙuri Mommy wallahi ba nice na ɗaukar miki ba." Cike da jin zafin Mommyn data sake kiranta dashi Hajja Maimoon ɗin ta runtse idanuwa tana jin tamkar ta watsa mata wuta a fuska, ta taso a hasale tayo kanta ta shiga naɗa mata duka, bata ƙyaleta ba sai da taga bata motsi alamun ta suma sannan ta koma saman kujera tana haki tamkar wacce tayi tseren gudu, ganin mintuna biyar ba alamun Jauhar zata motsa yasa ta mike ta ɗauki ruwa mai shegen sanyi dan har ya soma sanyi a fridge ta tuttule mata a jikinta, duk da zata so a ce Jauhar ɗin ta mutu sai dai tasan za'a tuhumeta tunda Irfaan ya san halin da suke ciki. tamkar an fizgo numfashin Jauhar ta saukewa lokaci ɗaya tana sakin wata irin ƙara dake nuni da a firgice take tana ja da baya tana cewa.

"Bani ce na ɗauka ba wallahi Hajiya ban ɗaukar miki ba." Ta sake faɗa tana ƙoƙarin barin falon don tsira da ranta, don a yanzu kam ta yarda cewa tabbas Hajja Maimoon zata iya kasheta kamar yadda akoda yaushe take faɗa. Tasowa Hajja Maimoon ɗin tayi tana jan ƙafafuwan Jauhar ɗin har zuwa cikin ɗakin nata ta jefata tare da ciro key ɗin ta ciki ta kulleta ta waje tana cewa.

"Na fiki taurin kai Jauhar, ubanki ɗan iskan banza ke kuma ɓarauniya ko? indai baza ki faɗa min inda kika kai min gold ɗina ba babu inda zaki je koda kuwa mutuwa zakiyi." Daga haka tawuce

ɗakinta rai aɓace taci gaba da neman gold ɗin nata data ajiye bata gansa ba.

Jauhar kam tsabar kuka gaba ɗaya fuskarta ta suntule tayi jajir, tayi kuka tayi na bakin cikin haɗata da Hajja Maimoon, da haka bacci yazo ya ɗauketa saboda tsabar wahala, A ɓangaren Hajja Maimoon ko dole ita tafito ta ƙarasa girkin da kanta cikin rashin walwala ta jere akan dining don ta ɗau alwashin sai Jauhar ta fito mata da gold ɗinta ko da zata buɗeta.

Kasancewar ba wani damuwa da ita yaran gidan sukayi ba yasa koda suka dawo daga school babu wanda ya nemeta, musamman da duk wani abu da zasu buƙata Mommy ta tanadar musu shi, shi yasa har dare babu wanda ya nemeta acikin gidan, girkin dare da Mommyn ta ɗora da kanta ma Jannat na gani ta soma murna yau Mommy ce zata yi musu special abinci ba sai sunci jagwalgwalen Jauhar ba. Murmushi kawai Mommy ta sakar mata taci gaba da aikin kafin Suhaila data dawo daga school tafito ta sameta aciki,

"Sannu Mommy, Wai yau meke damunki ne?" Sai da Hajja Maimoon ta juye kayan miyanta a blender da zata markaɗa ta kunna sannan ta kalli Suhaila data ciro crackers daga cikin loka ɗin dake kitchen ɗin ta haye carbinant tana ci tace,

"Ba lafiya kam Suhaila, gold ɗina na nema acikin gidannan na rasa!"

"What!" Suhaila tafaɗa tana zaro idanuwa, sai data tura crackers ɗin acikin bakinta sannan ta sake cewa,

"Mommy are joking? Toh waye zai ɗaukar maki gold har cikin dakinki?"

"Tambayar da nayiwa kaina kenan Suhaila saboda Jauhar tace ba ita ta ɗauka ba, kuma kinga ita kaɗai ke shiga ɗakin nawa."

"Maganar banza, wallahi ita ta ɗauka Mommy kawai tafito miki da abunki ko taci ubanta acikin gidan nan, dama da ɓarauniya muke zaune Mommy?"

"Abunda nake tunani kenan, shiyasa na rufeta cikin ɗaki har sai ta gaji ta fito min da abuna." Hajja Maimoon tafaɗa tana kashe blender ɗin dan kayan miyan sun markaɗu, da haka kuma Mommy ta kammala aikin suna tayata fira. Tana gamawa tasa suka kwashe abincin suka kai kan dining ita kuma ta gyara kitchen ɗin sannan ta haye sama, wanka tayi tai sallar magriba sannan ta sakko ta samu yaran a palour zaune suna kallo, Jannat ce ta ɗago kai tana cewa.

"Mommy wai gold ɗinki aka ɗauke?" Shafa kanta kawai Mommy tayi haɗe da neman kujera ta zauna don gaba ɗaya ƙarfin halin yin komai takeyi, ɓatan gold ɗin ba ƙaramin tashin hankali ya sakata aciki ba daurewa kawai takeyi tana yin abubuwa. Kusa da ita Jannat ta koma ta zauna tare da ɗago kanta tana kallon fuskar Hajja Maimoon tace,

"Mommy sorry, Jauhar ce ta ɗauke miki ko?"

Kafin ta tankata sai ga Daddy ya shigo, da gudu tamiƙe ta nufi wajensa tana yi masa oyoyo ya rike hannunta suka ƙaraso ciki, sannu da zuwa Suhana da Suhaila suka yi masa ya amsa cike da farin ciki kafin yakai kallonsa ga Hajja Maimoon dake yi masa sannu da zuwa yana cewa,

"Yawwa Mommyn Jannat, yau nasan nayi laifi ayimun afuwa." Ya faɗi hakan saboda rashin dawowa gida dawuri da baiyi ba dan ba irin wannan lokacin yake dawowa ba, kullum ana gama sallar la'asar yake dawowa gida amma yau wani aiki ya riƙesa bai dawo ba sai yanzu. Murmushi ta sakar masa kafin tamiƙe ta nufi sashensa, tana jin Jannat na faɗa masa cewa Jauhar ta ɗaukewa Mommy gold, bata dawo baya ba tayi gaba abunta. Bai bi takan zancen ba har sai bayan ta haɗa masa ruwa yayi wanka ya saka doguwar jalabiya ya wuce masallaci yayo sallar isha'i ya dawo sun zauna cin abinci sannan ya kalli Jannat yana cewa,

"Jannat kika ce me? Me Jauhar tayi?"

"Gold ɗin Mommy ta ɗauke." Juyowa yai ya kalli Mommy dake ɗan tsakurar abincin dake gabanta dan ba da ɗinsa take ji ba yace,

"Mommyn Jannat wai da gaske ne?" Ajiyar zuciya ta sauke haɗe da cewa,

"To na nemesa na rasa Habiby, waye zai ɗauka idan ba ita ba tunda ita kadai ke shiga ɗakin?"

"Kin duba da kyau kuwa? kuma kin tambayeta ko ta sauya mishi wajen zama ne data je gyaran ɗakin?." Ranta a ɗan ɓace take magana,

"Na duba ko'ina fa Ya Habiby, na kuma tambayeta amma ta tsaya tana yi min musu wai bata ɗauka ba, dan haka wallahi ko mutuwa zatayi a gidan nan sai ta fito min da gold ɗina kafin na sake barinta ta shaƙi iskar wajen nan." Hannunsa ya miƙa ya ɗora saman nata ganin yadda ɓacin rai ya taso mata lokaci ɗaya haɗe da cewa.

"Calmdown Mommyn Jannat, Jauhar ɗin tana ina yanzu?" Sai data haɗiye wasu yawun bakin ciki da tun ɗazu suka tsaya mata a maƙoshi hawaye na sakko mata tunawa da makudan kuɗin data saka ta sayi gold ɗin da tsada dan shiga tsara amma wai ace yanzu ya ɓata sannan tace,

"Tana ɗakinta na rufe ta dan babu inda zata je ban sani ba kota haɗa kai da wani taje ta bayar a sayar min da abu."

"Kamar ya? Wai tun yaushe hakan tafaru ban sani ba?" Yafaɗa cike da mamaki jin wai ta rufeta a ɗaki sai kace wata dabba,

"Tun da kafita." Ta bashi amsa a takaice tana wani turo baki,

"Subhanallahi shine kuma kika rufeta? Haba Mommyn Jannat mutunce fa kuma ki tuna muna

da ƴaƴa, zaki ji dadɗi idan aka yiwa Jannat, ko Suhana ko Suhaila hakan? Look koma meye kiyi hakuri ki buɗeta abi abun a hankali kada azo a samu matsala yarinyar mutane tazo ta mutu a hannun mu." Kuka Hajja Maimoon ta saka tare da miƙewa tana cewa,

"Wallahi ni bazan buɗeta ba sai tafito min da gold ɗina, kasan nawa nasa na siyashi?" Goshinsa ya dafe haɗe da cewa,

"Oh my God! Kije ki buɗeta nace zamu yi magana daga baya Maimoon." Yadda yai maganar ya alamta mata cewa ransa ya ɓaci, ba dan ranta ya so ba ta shiga kitchen ta ɗakko key ɗin taje ta buɗe ɗakin Jauhar tana barin wajen aguje tana kuka. Da idanuwa Alhaji Sha'aban Sada ya bita yana kallo kafin ya maido kallonsa wajansu Suhana da ransu ya ɓaci ganin Mommyn na kuka yana cewa,

"Suhaila je ki kira yarinyar." Yafaɗa cike da damuwa shima. Wani kallon wulakanci Suhaila tayiwa Jauhar da tana jin motsin buɗe kofar a tsorace ta tashi ta takure waje ɗaya tana ƙanƙame jikinta acan kusuwar ɗakin,

"Munafuka, ki taso Dady nakira kuma sai kin fitowa da Mommyn mu gold ɗinta ko bakya so ɓarauniya kawai."

Jiki ba ƙwari Jauhar tamiƙe wani irin jiri na ɗibarta saboda yunwa da halin da take ciki tafito tana rabewa ajikin bango, tausayinta ne ya rufe Alhaji Sha'aban ganin yadda ta koma yace,

"Ƙaraso nan Jauhar." Sai data dudduba palourn taga Hajja Maimoon bata nan sannan ta saki jikinta ta iya ƙarasawa wajen ta duƙa ƙasa yaran sai harara suke aika mata da ita tamkar idanunsu zai faɗo. Cikin sigar rarrashi Alhaji Sha'aban yace da ita,

"A ina kika ajiyewa Mommynku gold ɗinta har tayita nema bata gani ba?" Ba tare data ɗago kanta ba tace,

"Ban ganshi ba Dady kuma wallahi bani na ɗaukar mata ba." Taƙarasa zancen hawaye na sakko mata akan fuskarta.

"A'a Jauhar kiyi tunani tunda kinga ke kaɗai ke shiga ɗakin yi mata gyara ko kin gansa kin sauya masa waje?." Sai alokacin ta ɗago kai tana kallon Dady har lokacin hawaye basu daina sakkowa akan koɗaɗiyar fuskar tata ba da gaba ɗaya tayi kama kalar aljanu saboda rashin kulawa duk ta dushe in ba ga wanda ya santa ba tun farko tana cewa.

"Allah Dady ban ganshi ba, za'a iya sake cajeni agani ko a sake duba ɗakina, wallahi ko kashe ni idan za'ayi Dady bansan inda Mommy ke ajiye gold ɗinta ba idan ba nagani a wuyanta ta saka ba."

"Shikenan, tashi kije." Dady yafaɗa tare da miƙewa ya nufi sama wajen Hajja Maimoon ɗin.

Wani irin mugun ranƙwashi Jauhar taji Suhaila ta sakar mata da zata wuce akai tana cewa,

"Barauniya kin dai ji kunya wallahi." Suhana ta bangajeta ita kuma daga inda take ta faɗi tare da wucewa abin ta. Jannat na zuwa itama tasa kafa ta takata ta wuce tana cewa,

"Beranya.."

Zuwa yanzu hawayen Jauhar sun fara ƙarewa, haka ma zuciyarta ta bushe da sam babu sanyin dazai sata tausasa har taba idanuwan nata damar zubo da ƙwalla, hakan yasa ta miƙe ta wuce ɗakinta ta rufo tana addu'ar Allah ya kawo mata mafitar barin gidan kota samu ƴancin rayuwa data rasa tun tana ƙarama.

Alhaji Sha'aban Sada kuwa a hankali ya tura ƙofar ɗakin Mommy ya shiga, tana zaune gefen gado ya ƙarasa ciki tare da tsayawa agaban madubi ya ɗan jingina yana kallonta yake cewa.

"Yanzu meye abun kuka Maimoon da har zaki bari waɗannan tsadaddun hawayen naki su zuba kuma agaban ƴaƴan ki? Ina gold ne dai ko? Toh kibari zan siya miki wani, kiyi hakuri kibi abun a hankali tare da saka mata idanuwa, idan har yana wajenta na tabbata zaki ganoshi amma to me I don't think yarinyar nan ita ta ɗaukar miki abu saboda na sake tambayarta ta tabbatar min da batasan ma inda kike ajiyewa ba, a yanda kuma nasan kina daraja duk abinda kike so bana tunanin zaki ajiyesa inda zata iya ganinsa." Ɗago kai tayi tana tsaresa da idanuwa kafin tace.

"Me kake nufi? kenan kana goya mata baya kenan ko? bayan ni da kai da kowa ma na gidan nan munsan ita kadai ce zata iya ɗaukarsa. Jannat, Suhana da Suhaila duka nasan wannan ba halinsu bane, be side ba abunda suka rasa daga wajen mahaifinsu balle suyi negative thinking irin wannan, but Jauhar fa? I don't trust her at all, bana tunanin zata wadata da abinda take dashi tunda ba tada gata irin nasu, asali ma da ita da babu duka ɗaya ne a wajen mahaifanta me zai hana tafara tunanin ɗauke-ɗauke." Iska Alhaji Sha'aban Sada ya ja ya furzar ta baki haɗe da cewa,

"Ba goyon bayanta nakeyi ba, nasan itama baki taɓa cewa kin nemi abunki kin rasa acikin gidan nan ba, zancen gata da kikeyi Allah fa shike gatanta wanda yaso, koda wannan ɗabi'ar ta Jauhar ce zan so ki ajiye duk abinda kike ji a zuciyarki da iyayenta suka yi ba dai-dai ba, ki janyota ajikinki tamkar ƴarki ki gatanta itama, hakan zai iya sa ta sauya kuma ta amfaneki nan gaba ta hanyar mayar da alkhairi agareki akan sharrin da iyayenta sukayi miki, ƙaramar yarinya ce ita Maimoon, mai yiyuwa bata masan abinda sukayi miki ba amma kina sauke fushinki akanta which is wrong, very very wrong." Wani kallo take jifan Alhaji Sha'aban ɗin dashi haɗe da miƙewa tana kallonsa.

"Over my died body Habiby bazan taɓa ɗaukar Jauhar a matsayin ƴa ba a wajena balle har na gatanta, yadda na tsani mutuwata haka na tsaneta da duk wani abu daya shafi rayuwarta, halinta kuwa idan zaifi haka muni Allah ya tabbatar mata dashi ya sake lunka mata da wanda yafisa, ni kuma akwai nau'ukan azaba kala-kala da zan tanadar mata har zuwa lokacin da zata

gudu da kanta tafice cikin rayuwata nima na huta." A yanzu ko kaɗan Alhaji Sha'aban Sada baya mamakin duk wasu munanan kalamai da zasu fito daga bakin Hajja Maimoon akan Jauhar, wanda hakan ke tabbatar masa da koma meye tsakaninta da iyayen yarinyar to baƙaramin abu bane, sai dai hakan bazai zama hujjar da zata sa ta ɗauki fansa akanta ba.

"Shikenan, what ever dai wannan damuwar ta wuce please in sha Allah gobe zamu je na siya miki wani gold ɗin kiyi hakuri kin ji ko?" Ya faɗa yana ƙarasawa yariƙota tare da janyota zuwa jikinsa...

#A heart touching story
#Gonar Sharri..
#Hajja ce
#Billy s Fari
#Ƴan Tagwaye

*ƳAN TAGWAYE BIYAR*

*GONAR SHARRI*
Billy S Fari & Hajja ce

*IDANIYAR RUWA*
(Mai wuyar toshewa)
Ayusher Muhd & Jeeddah Aliyu

*WATA ALAKA*
Zee Bawa & Stylish bch

*BISHIYAR TSIYA*
(Wanda bai jiba bai gani ba ke girbar ki)
Umm Ashgar & Sadiya Dan.

*TSARIN ALLAH*
(Ba mai iya canzawa)
Asmy b Aliyu & Nana Diso

*ZAI IYA BIYAN*
GUDA 1 akan 500
GUDA 2 akan 800
GUDA 3 akan 1200
GUDA 4 akan 1600
GUDA 5 akan 2000

*BANK ACCOUNT*
8098456130
Opay digital services
Shaidar biya 08098456130

*KATIN MTN*
07065283730
Shaidar biya ta lambar.
[8/1, 9:34 PM] Billy S Fari: *GONAR SHARRI...!*

*ƳAN TAGWAYE BIYAR*
(Batch C)

NA

*BILLY S FARI*💎
Da
*HAJJA CE*👈
Arewabooks@billysfari
*BOJUWA HERBAL'S & SCENTS*
*Suna kawo Saiwowin sanyi da suke dagargaza sanyin mara da na jijiya.*
*Haka nan akwai dafaffen maganin ga wanda tafi son ready made.*
*Haka nan suna kawo Saiwowi daban daban daga Chad da Sudan, kuma marasa illah*
*Saiwowin tsumi*
*Saiwowin dahuwar kaza/tattabaru*
*Saiwowin matsi gangariya*
*Original gadalin mata*
*Ƴaƴan gadali na asali*
*Original gumba*
*Tsumin Saiwowi*
*Tsumin kwakwa da Dabino*
*Igiyar alkairi*
*Zumar goran tula*
*Hakkin daka na musamman na asali*
*Bayan haka suna dafa kazar amare da masu jego da ma uwayen gida*.
*Akwai bridal package*
*Mai jego package*
*Ƴar gata package*.
*Dukkan kayan kuma available ne for pickup or immediate delivery.*
*A Kano nake amma kuma nationwide delivery ne*
*Ku tuntubi Surayya Halin yau a wannan lambar dan samun naku cikin musulmin farashi*
*08032773332*

*Iyah Basiru na gaisuwa*😅

Page 7..

Tabbacin data samu akan zai sai mata wani gold ɗin yasa zuciyarta yin wani irin sanyi, da haka ya riƙo hannunta suka sakko suna hira tamkar ba itace ta gama kuka ba har yana tsokanarta wai itama zata koma kamar Baby Jannat tafara saka mashi ciwon kai da rigimarta. Su Suhana dama sun wuce ɗakin su, kallonta yai tare da cewa,

"Muje kici abincin ki dan na lura baki ci komai ba."

"Na ƙoshi, bari nayi mata magana kawai tazo ta gyara wajen." Ta ƙarasa zancen tana nufar ɗakin Jauhar ɗin. Kwance ta hangota wani baƙin ciki ya sake tokareta na ganinta kaɗai da tayi kwance, gani tayi tamkar jin daɗi ne yasa ta kwanciyar saboda idan son samunta ne kawai ta buɗe idanuwa taga Jauhar cikin wahala da kuma aikin bauta da babu ranar tsayawa a huta aciki,

"Ki tashi kije ki gyara wurin can, amma ki sani bawai na kyaleki bane, inhar banga zinarina ba bazan taɓa bari kihutawa rayuwarki ba acikin gidan nan, saboda na dinga jefaki a masifa kala-kala har sai kin gaji kin fito dashi, nonesense!"

Daga haka ta wuce part ɗin Alhaji Sha'aban tana tunanin kalar ukubar da zata tanadar mata gobe. Jauhar kuwa miƙewa tayi da kyar tafito palourn don dama wata irin masifaffiyar yunwa take ji ta kwashe kayan takai kitchen ta dawo ta gyara wajen, abincin da aka rage ta tattara ta hau ci har sai data canyesu tas sannan ta wanke kayan ta gyara kitchen ɗin, tana fitowa Suhaila na sakkowa, tana ganinta tace,

"Ke.!" Lokacin Jauhar na ƙoƙarin shiga ɗakinta ta juyo tana kallonta ba tare data amsa ba,

"Ki haɗo min coffee ki kawo mun." Jauhar da jikinta ke tsami taji kamar ta fashe da kuka amma ba damar yin hakan sai kawai ta amsa mata da,

"Toh." Tana juyawa tare da komawa cikin kitchen ɗin ita kuma Suhaila ta juya takoma ɗakinsu. bayan mintuna biyar Jauhar ta kammala haɗa coffee ɗin ta nufi ɗakinsu ta kai mata, har zata juya tafita Suhana tace,

"Ki shiga toilet akwai undies ɗina cikin washing machine ki ƙara wankemun ki shanya." Jauhar ta amsa mata da,

"Toh." Tana sake ɗan tattaro karfin jikinta ta nufi toilet ɗin ta shiga wankin undies ɗin Suhana. Ba ita ta gama ba sai kusan ƙarfe sha biyu ta wanke toilet ɗin tas sannan tafito ta wuce ɗakinta, wanka ta shiga tafara yi ko jikinta zai saki sannan tasha ragowar maganin da Uncle Irfaan ya taɓa bata daga nan ta kwanta, kamar jira akeyi ta kwanta wani irin zazzaɓi ya taso ya rufeta,

take tafara rawar sanyi ta ja zannuwanta duka ta lulluɓa hawaye na sakko mata, bata san lokacin data fara kuka ba tana kiran sunan Abbanta ba dako kasheta za ayi bata san inda yake ba yanzu, kuma bata san duniyar da zata shiga wajen nemansa ba.

Yadda taga dare haka taga safiya ba tare data runtsa ba saboda yadda zazzaɓi ya rufeta. Tun tana jurewa har takasa tafara kuka ƙasa-ƙasa, duniya ta sake yi mata zafi wacce dama ba wai ta taɓa yi mata bane, haka ta taso bata san wani abu farin ciki ba ko kaɗan. Alhaji Sha'aban Sada ne da asuba daya fito zai tafi masallaci yaji kukan nata can ƙasa-ƙasa amma da yake har an tada sallah bai tsaya bi takai ba ya wuce masallaci, da kuma ya dawo sai ya manta ya shige part ɗinsa ba tare da ya tuna cewa yaji kuka kafin ya fita ba. Hajja Maimoon na zaune ta idar da sallah tana duba wasu kaya a wayarta da take son fara business ɗin su, kai ta ɗago ta gaishe shi ya amsa yana faɗin,

"Yau da wuri nake son fita saboda akwai bakin da zan gani ƙarfe bakwai, saboda haka ina tunanin bazan tsaya karyawa ba kawai haɗa min ruwan wanka dan bana so asamu matsala, mutanene masu muhimmanci da nake sakaran idan Allah ya daidaita tsakaninmu zan cika miki alkawarinki a cikin satin nan."

"Kamar kasan kayan da nake son fara business ɗin sune nake dubawa a wani group dana shiga na masu campany, duba kaga kalar designers ɗinsu." Ta miƙa masa wayar haɗe da tashi ta shiga toilet ta haɗa masa ruwan wankan tafito. Wayarta ya bata sannan ya miƙe yana cewa,

"Kayan sunyi kyau sosai idan har naga business ɗin ya karɓeki to nima zan saka hannun jari aciki sai na buɗe miki shago." Tana murmushi ta karɓi wayar tare da cewa,

"Zai ma karbeni in sha Allah, ai sana'ar kayan yara da turarukka da jakunkuna da kake gani ba ƙaramin samu akeyi ba, matsalar kawai idan mutum baida kuɗi da kuma isasshen jari, hala ka manta a cikin harkar ka ganni ka ƙyasa?" Ta kasara maganar cike da zolaya. Ya yi murmushi yana cewa.

"To ki ɗauka ba kida wannan matsalar gimbiya ta, bari na shiga wankan kar na makara." Alhaji Sha'aban ya faɗa yana ƙarasa shigewa cikin toilet ɗin ba tare da ya jira taje ta haɗa masa ba. Mintuna ashirin yafito ta taimaka masa ya shirya, tana cikin fesa masa turare wayarsa ta ɗauki ƙara lokaci ɗaya kuma sukaji ana buga musu ƙofa da ƙarfi ana kiran su,

"Dady..!, Mommy..! kufito Jannat zata mutu." Suhana dake buga ƙofar da ƙarfi tafaɗa cikin tsanani tashin hankali, kusan atare suka ƙaraso bakin ƙofar Mommy na faɗin,

"Me ya samu Jannat ɗin?"

"Ciwonta ne ya tashi." Tafaɗa hawaye na sauko mata dan tunda asuba da suka tada ita suka ga ta sake shigewa cikin bargo wai sanyi take ji, shine fa yanzu ko da suka ga lokacin zuwa school na ƙoƙarin yi bata tashi ba suka janye bargon suka ga ta kakkame a cikin bargon, shine Suhaila

ta tallabota zuwa jikinta tasa Suhana ɗin tazo takira su Mommyn. Already Dady ya riga da ya saba da ciwon Jannat dan haka cikin nutsuwa bayan yaje yaga yanayin da take ciki ya kira Irfaan a waya, bugu ɗaya ya ɗaga suka gaisa kafin yace yayi maza yazo gidan yana nemansa, dama jiya ba'a gidan ya kwana ba gidan Hajiya yayi tafiyarsa ya kwana acan saboda ɓacin ran abinda Mommy tayi masa da rashin iya jurewa ganin halin da Jauhar ke ciki da bazai iya ba.

Bayan mintuna goma sai gashi ya iso, lokacin an fito da Jannat nan palour, kallonsa Dady yai haɗe da cewa,

"Yanzu aka kirani akwai mutunen da zan gani urgent, ka ɗauki Jannat ka kaita asibiti ciwonta ne ya tashi, duk yadda ake ciki ka kirani kafin nazo.

"To Yaya." Irfaan yafaɗa tare da ɗaukar Jannat Mommy tabi bayansa ita dasu Suhaila da gaba ɗaya hankalinsu ya tashi. Har Alhaji Sha'aban ya shiga motarsa ya tayar suma sun shiga wacce zasu wuce asibitin ya saukar da glass ɗin motarsa yana cewa Irfaan.

"Yauwa Irfaan da kun dawo yarinyar nan ku dubata ku gani idan lafiya take saboda da asuba da na fito zanje sallah naji kukanta ƙasa-ƙasa na manta bamuyi maganar da Maimoon ba." Yana ƙarasa faɗar hakan yafice daga gidan bayan mai gadi ya buɗe masa gate. Irfaan kuwa yana Jin haka ya kashe motar, har yakai hannunsa zai buɗe murfin ƙofar Hajja Maimoon ta dakatar dashi,

"Ina kuma zaka je baka ga halin da yarinyar nan take ciki ba ne? Kana ganin fa yanda take kokuwa da numfashinta."

"Ita waccan ta cikin gidan ba mutum ba ce? Bazai yiyu abarta ita kaɗai ba har sai mun dawo tunda ba'a san halin da take ciki ba, ki je ki dubota in lafiya take sai mu tafi, I know Jannat will be ok in sha Allah ba abunda zai faru da ita." Tsabar ɓacin rai kasa magana Hajja Maimoon tayi ta ɗauke kai kawai zuwa can gefe, ganin haka yasa Irfaan ya ɓalle murfin motar yafita zuwa cikin gidan zuciyarsa duk babu daɗi. Kai tsaye bakin ƙofar ɗakin Jauhar ya nufa ya kwankwasa mata, jin shiru bata amsa ba ya sashi tura ƙofar a hankali. Adunkule ya ganta cikin zannuwan data rufa dasu har lokacin jikinta na rawar sanyi, sai kukan da takeyi wanda dan tsabar wahala ko fita baya yi sosai dan tayi kukan har ta gaji.

"Subhanallahi." Yafaɗa yana takowa cikin ɗakin tare da jaye zannuwan jikin nata, halin ɗaya ganta aciki ba ƙaramin tsorata yai ba yaciro wayarsa da sauri yakira Suhaila da itama ta cika tayi fam ganin yadda uncle ɗin nasu yake ƙoƙarin fifita mai aiki akan ƴar uwarsu. Kamar bazata ɗauka ba sai kuma ta ɗaga tana turo baki take cewa,

"Uncle ko naja motar kawai mutafi ne?" Tayi maganar cikin nuna shi tunda yana da uzuri bari su tafi.

"Short up Suhaila bake zaki sani yin abinda ya kamata ba, ai Yayan yasan kun iya mota amma

ya taso dani nazo. Kuyi sauri ku shigo ke da Suhana ina jiran ku, ki faɗawa Mommy yarinyar nan batada lafiya sosai." Ya ƙarasa maganar yana kashe kiran tare da kiran sunan Jauhar ɗin har sau biyu amma takasa amsawa. Cike da ɓacin rai Suhaila ke faɗin.

"Mommy wai kinji Uncle Irfaan yace Jauhar batada lafiya sosai."

"Wannan ba damuwar mu bace Suhaila, kije kifaɗa masa idan bazai kaimu asibitin nan ba ke ki dakko makullin motarki kizo mutafi kawai, ina ruwanmu da matsalarta? ta mutu mana."

"Mtss Allah Uncle Irfaan yacika matsala." Suhana tafaɗa tana balle murfin motar suka nufi cikin gidan. Saka su yai suka tallabo Jauhar wacce da daƙyar take iya tafiya suna faman kumbura fuska tare da riƙe numfashin su kamar sun riƙo kashi suna kauda kai suka shiga da ita cikin motar, dama Hajja Maimoon na gaba ta runtse idanuwa zuciyarta na tafarfasa haɗe da juyar da kanta gefe. Babu yadda zatayi ne amma da ba za'a taɓa yin tafiyar nan da Jauhar ba, kawai dan bata son a ɓata lokaci ne ba'a kai Jannat ɗin ba wani abun yazo ya sameta tasan sai tafi kowa damuwa saboda ta shaƙu da yarinyar fiye da sauran yaran.

Ba tare da Irfaan ya kulasu ba ya dakawa Suhaila tsawa data yi tsaye a bakin ƙofar motar ita a dole bazata shiga motar ba yana cewa,

"Suhaila karki bari na saɓa maki da sanyin safiyar nan, karki kai ni bango wallahi." Tana turo baki ta shiga cikin motar ganin yanayin yadda yai maganar ba wasa a fuskarsa ta ja murfin da ƙarfi ta rufe sannan ya buɗe ya shiga shima ya fizgi motar aguje suka nufi Fedral Medical center. Suna zuwa ya yi parking, Jannat kawai suka fitar dama tun a ciki sukayi ta mintsinin Jauhar wacce hawaye kawai take ta kasa bayyana kukan nata a fili. Ciki suka shige ganin haka yasa Irfaan yiwa ma'aikata mata dake cikin asibitin magana suka karaso wajan motar suka taimakawa Jauhar aka shiga da ita ciki emargancy dan gabaki ɗaya tafi Jannat wahala. Koƙarin yadda za'a duba Jauhar kawai Irfaan keyi hakan yasa ran Hajja Maimoon sake ɓaci tayi saurin ƙarasawa inda yake cikin fushi take faɗin.

"Irfaan hala ka manta wacce tayi sanadin fitowar mu ko? Naga gabaki ɗaya hankalinka yana kan wacce babu wata alaka tsakaninka da ita. Kaje kaji da Jannat ka tsaya nan wajan. Ni wani lokacin sai na kasa gane manufarka akan Jauhar wallahi." Jin kalmarta na ƙarshe-ƙarshe yasa Irfaan saurin kallanta ta jinjina masa kai alamar tabbatar da abinda yaji ta faɗa. Yaja ɗan guntun tsaki yadda ba zataji ba. Yana mamakin yadda take yi masa abubuwa bayan a girme ya girmeta dan shi yana da talatin da uku ita kuma tana da talatin. Gudun ɓacin rai yasa shi juyawa ya yi settling case ɗin Jannat aka bata ɗaki sannan ya koma kan Jauhar wacce fitowar Zain kenan wata nurse tana nuna masa inda Jauhar take a kwance kan bancin dake ajiye a reciption. Wajan ya ƙarasa tare da buɗe baki da kyar ya furta.

"HI." Jauhar dake kwance taji tsayuwar mutum a kanta ta buɗe idanunta da kyar suka sauka akan ƙafafuwansa dake sanye cikin black cover shoe ta kasa ɗaga kai ta kalli fuskarsa saboda yadda idanunta sukai mata nauyi. Durƙusawa ya yi saitin fuskarta tare da leƙawa suka yi ido

huɗu da juna. Da sauri ya miƙe tsaye ganin idanunta biyu yace.

"Tashi zaune." Jauhar ta shiga ƙoƙarin tashi amma ta kasa, sai dai tana karfafawa zuciyarta guiwa tana ta kokawar miƙewa sanin cewa jiranta ake yi. Hannunta da take dafa bancin ne ya goce tazo zata faɗi cikin sauri Zain yasa hannu zai taro ta Irfaan da isowarsa kenan ya tare ta. Da sauri dukkan su suka kalli juna ido cikin ido kafin Irfaan ya juya yana taimaka mata ta zauna sosai akan bancin, daga shi har Zain kallanta suka yi yadda albarkatun kirjinta da suka fara tasowa suka tsaya a cikin rigarta wacce babu bra a jiki. Da sauri Irfaan ya kauda kansa Zain rintsa ido wani mugun takaici yana taso masa tun daga can ƙasan ransa har zuwa saman harshensa...

#A heart touching story
#Gonar Sharri..
#Hajja ce
#Billy s Fari
#Ƴan Tagwaye

*ƳAN TAGWAYE BIYAR*

*GONAR SHARRI*
Billy S Fari & Hajja ce

*IDANIYAR RUWA*
(Mai wuyar toshewa)
Ayusher Muhd & Jeeddah Aliyu

*WATA ALAKA*
Zee Bawa & Stylish bch

*BISHIYAR TSIYA*
(Wanda bai jiba bai gani ba ke girbar ki)
Umm Ashgar & Sadiya Dan.

*TSARIN ALLAH*
(Ba mai iya canzawa)
Asmy b Aliyu & Nana Diso

*ZAI IYA BIYAN*
GUDA 1 akan 500
GUDA 2 akan 800
GUDA 3 akan 1200
GUDA 4 akan 1600
GUDA 5 akan 2000

*BANK ACCOUNT*
8098456130
Opay digital services
Shaidar biya
07040402435 ko 08098456130

*KATIN MTN*
07065283730
Shaidar biya ta lambar.
[8/1, 9:34 PM] Billy S Fari: *GONAR SHARRI...!*

*ƳAN TAGWAYE BIYAR*
(Batch C)

*BILLY S FARI*💎
Da
*HAJJA CE*👈
Areewabooks@billysfari

Page 8..

Da kyar Irfaan ya iya buɗe idanunsa yana kallan gefe, shi kam shaf ya manta da zasu taho bai yi tunanin ɗauro mata hijab ba akai kawai suka taho, asali ma shi bai wani kula da yanayin da take ba sai yanzu, kuma yanzun ma da ace babu wani a kusa da ita ya tabbatar ba wani lura zai yi ba. Ya saba ganinta cikin riga da zani na atamfa rigar kuma burmemiya ce yanzu kuma wata yaloluwar t-shirts ce hakan yasa abubuwan nata suka kusa tsone musu idanuwa lokaci ɗaya duk kuwa da cewa ba wani girma ne dasu ba kasancewar babu kwanciyar hankalin da zata samu natsuwar da har zasu iya taso sosai, ɗan tsaki ya ja tare da sake ɗauke kansa gefe. Shi kuwa Zain saboda yanayin aikinsu sun saba ganin ire-iren haka ga patient sai kawai ya maze tare da buɗe idanunsa yana kallan fuskar Jauhar tare da don kaucewa kallonsa ga kirjin nata, amma duk da haka da yake ido gulmammi ne sai da yaji sun sake sauka wajen, cikin sauri ya sake kawar da idanuwan nasa daga wajan yana cewa.

"Zo muje naji meke damunki ko akwai taimakon da za'a iya yimaki kafin Dr ya ƙaraso." Ya faɗa yana juyawa tare da shiga wani office dake nan kusa dasu. Ɗan ƙaramin tsaki Irfaan yaja ganin Jauhar ɗin ta mike tabi bayansa sai faman durƙushewa take alamar tana jin jiki sosai. Kallon inda su Hajja Maimoon suke tsaye ya yi cikin sa'a suka haɗa ido da Suhana ya kirata da hannunsa. Kamar ba zataje ba sai ta daure taje lokacin har Jauhar ta shiga cikin office ɗin. Hannun Suhana yaja suka zauna akan bencin da Jauhar ta tashi ya kalleta sosai sai kawai tasha jinin jikinta cewa akwai abinda tayi, mamakin irin kallan da yake binta dashi takeyi kafin tace.

"Uncle menene?" Irfaan ya sauke numfashi tare da lasar lips ɗinsa da suka soma bushewa yace.

"Yanzu abinda kukayi ɗazun kun kyauta? A ina ko koyo zuciyar rashin son taimako? Allah yaji ƙan Aunty yai mata rahama sam halinta ba haka yake ba" Jikin Suhana ne yai sanyi jin abinda ya faɗa kafin ta amsa masa da.

"Amin Uncle." Tana sinne kai ƙasa, sake kallonta yai akaro na biyu tare da sauke numfashi yace.

"Amin ɗinki ba zatayi mata amfani ba Suhana, kawai ki amsa Mani tambayar da nayi maki." Duk da tasan akan Jauhar yake zance da suka nuna ko oho da rashin son taimaka mata da zasu zo asibiti, hakan bi hanata yin tunanin me yasa zai kawo zancen mahaifiyarsu acikin zancen ba? hawaye taji ya tarar mata acikin idanuwa ta ɗago kai ta kalleshi tana cewa,

"Innalillahi saboda me zaka ce Amin ɗina ga mahaifiyata ba yada amfani Uncle? Wane laifi nayi ne?" Cike da damuwa dake kwance akan fuskarsa ya riƙo hannunta haɗe da cewa.

"Saboda baku da hali mai kyau dukkan ku Suhana. Gabaki ɗayan ku babu wanda yake faranta mata a nan duniya. Tana kwance a kabari abinda zai sanya ta farin ciki baifi a tashe ta ace tashi kiga abinda ƴaƴanki keyi aduniya mai kyau, amma na tabbata da wannan halin naku da kukeyi Suhana da akwai hanyar da Aunty zata fito ta gaya muku ku gyara da tayi, amma babu hanya sai dai kawai ta ganku ta kyale har zuwa lokacin da kukaje inda take." Hankalin Suhana ya fara tashi dan gabaki ɗaya taji cewa suna yin abinda bai kamata ba duk kuwa da cewar har yanzu bata tunanin abinda sukayi ɗazu ɗin laifine. A gigice take kallansa tana jin tamkar ta fashe da kuka take cewa.

"Dan Allah Uncle ka sanar dani me mukayi da har mahaifiyar mu baza tayi farin ciki damu ba?" Ganin anzo gabar da yake jira yasan ya shi cewa.

"Wulakanta ɗan Adam da nuna baya da daraja ta kowace fuska, wato Suhana Allah shi yasan dalilin da ya yo ɗan adam a mafifita darajar duka al'umma. Me yasa kuke yiwa Jauhar haka? Kuna tunanin da tazo aiki gidan ku hakan yana nufin Allah baya sonta ne? Please Suhana kuyi abinda Allah zai baku lada, kinga kece mai sauki a cikinsu, kece muke ganin kamar zaki ɗakko dabi'un mahaifiyarki amma wani lokacin sai ki karkace ki koma irin su, dan Allah ki riƙa tausayin Jauhar, yarinya ce kamarku dake bukatar kulawa irinta uwa da uba kamar yadda kuke samu amma tarasa saboda haka Allah ya tsaro rayuwarta zata kasance mata." Take hawaye suka fara zubowa daga fuskarta tasa hannu tana sharewa, dama duk cikin su itace mai sauki kuma batada weak point aduniya kamar na zancen mahaifiyarsu, dan haka maganar Irfaan ba ƙaramin tasiri tayi a zuciyarta ba. Murya a sanyaye take kallonsa haɗe da cewa.

"Insha Allah Uncle na bari kuma daga yau na dena takurawa Jauhar saboda bana so Mami taji haushinmu idan taga abinda mukeyi marasa kyau". Cikin ƙarfafa guiwa ya sakar mata

murmushi yana cewa.

"Insha Allah zatayi farin ciki dake Suhana duniya da lahira idan kikayi kokarin gyarawa. Kinga yanzu tana ciki ita kaɗai sai nurse ga jiki tana ji, ki shiga ko zata bukaci taimakonki kin ji ko?." Ɗaya masa kai tayi haɗe da miƙewa a hankali ta nufi cikin office ɗin jiki duk babu daɗi. Zaune ta tarar da Jauhar ɗin akan kujera ta ɗora kanta saman table ɗin da Zain ke rubutu bayan ya gama gwada BP ɗinta da kuma yi mata tambayoyi akan abubuwan da takeji. Shigowar ta Suhana yasa shi ɗan sakin murmushi, duk da shi ɗin ba mai yawan hayaniya bane, zamowarsa nurse kuma sai ya sake sashi kamewa musamman idan yana kan aiki kasancewar dole sai da natsuwa a aikin nasu, duk da wani lokacin yakan zama mutum mai sakin fuska da kuma barkwanci saboda ya ƙarfafawa marasa lafiyan da yake kulawa dasu guiwa.

"Ya akai? Ko so kike kiji abinda yake damun ƙawata?" Mamaki ya kama Suhana ta ɗan zaro idanuwa tana kallonsa tace,

"Ƙawarka?" Yace,

"Eh mana muna sirri da ita kika shigo ko tare kuke?" Ya tambaya yana tsare Suhana da ido. Lanƙwasa idanuwan nata tayi kafin tace

"Dama kasanta ne?" Yace,

"Eh yau muka ƙulla ƙawancen da ita gashi har allura ma zan yi mata." Jauhar dake jin abinda suke cewa ta ɗago da kyar tare da zuba masa ido jin yace wai ita ƙawarsa ce. Gira ɗaya ya ɗage mata hakan yasa tayi saurin juyawa ta kalli Suhana taga ko ta ganshi. Suhana ce tayi magana cikin kulawar da ta bawa Jauhar ɗin mamaki take cewa.

"Sannu Jauhar kin ji abokin naki wai allura zai yimaki, meke damunki ne halan?" Mamaki yai bala'in ɗaure ta dan haka da kyar ta iya girgiza mata kai tana cewa.

"Ba komai." Zain dake jinsu yana miƙewa tsaye yake cewa.

"A'a fa ƙawata jininki ya hau sosai kuma kin ƙi sanar dani meke cikin ranki taya zaki ce babu komai? Please ko zaki fadawa Yayar mu sai ta faɗa mani". Ya faɗa yana maida kallonsa ga Suhana, kafin ta bashi amsa ya nuna Jauhar da hannu yana cewa Suhana.

"Ki ɗan taimaka ki yafa mata ɗan kwalinki tunda bata sako hijab ba tana ƴan mata da ita." Murmushi Suhana tayi tare da zaro ɗankwalin material ɗin jikin nata ta ɗorawa Jauhar akan kafaɗunta. Kallansu ya yi tare da faɗin.

"Bari naje sai kun jira likita yazo muji wane irin taimako zai bata." Yaƙare zancen tare da ficewa tun kafin su bashi amsa. Kai tsaye Zain ya dinga duba mararsa lafiyan da aka kawo har yazo kan Jannat wacce ya tarar da ita kwance a kan gado Hajja Maimoon tana faman shafa bayanta

sai wani sake narkewa takeyi. Inda take ya ƙarasa yana sargafe hannayensa a kirjinsa. Jannat ta ɗago kyawawan idanunta ta zuba akan na Zain, ganin yadda yake kare mata kallo ne yasa ta turo baki tana cewa.

"Mommy kin ganshi ko?" Da sauri Zain ya ware ido yana cewa.

"Good girl, dama so nake naji kina magana ne ko bebiya ce sai na san ta inda zan fara dubaki. Da alama ma lafiyarki ƙalau kawai raki ne irin naki dan ki tayarwa dasu Momynki hankali ko?" Zabga masa harara Jannat tayi bata wani damu da girmansa ba tana sake shagwaɓewa cikin jikin Mommy take cewa,

"Mommy ki masa magana wai cewa yai ƙarya nakeyi." Hajja Maimoon ta kamo hannayenta cike da kulawa tace,

"Rabu dashi tsokanarki yake yi shima kansa in yasan aikinsa to tabbas yasan bakida lafiya" Hajja Maimoon tayi maganar tana wani mammatsa hannun Jannat ɗin a cikin nata. Cikin rashin nuna damuwa da kalaman na Mommy Zain ya shiga duddubata ya yana sake cigaba da tsokanarta ita kuma tana yiwa Mommy ƙorafi da taɓara, a haka likita yazo Zain ya gaggabatar masa da abubuwan da ya yi wanda aka sakawa kowa cikin files ɗinsa dan shine on duty yau a emergency ɗin.

Yaso a fara duba Jauhar saboda tafi Jannat buƙatar kulawa amma yadda su Mommy suka tsare komai ya sanya sai da aka kira su Jannat likitan ya yi mata duk abinda ya kamata kafin aka kirawo Jauhar, tana isowa likitan dake rubuce-rubuce akan folder din tata ya ɗago kai don ganin kowaye saboda yadda yaji tsamin kayan dake jikinta ya cika musu hanci. Irfaan kuwa gabaki ɗaya ya fara jin haushin Zain ganin yadda yake ta yi musu wani irin faran-faran duk da ya lura da cewa hakan yake yiwa mararsa lafiyan dake wajen gabaɗaya, wanda cikin ƙanƙanin lokaci yaga sunyi wani irin sabo shida Jannat ta yadda komai zai ce sai yaji yace mata 'Mommy's daughter' Ita kuma yaji tace 'likita'. basu wani jima ba aka gama duba Jauhar da Jannat, inda Doctor Habu ya sanar dasu cewa a kula da Jauhar sosai dan a wannan stage ɗin tafi Jannat buƙatar taimako da kuma kulawarsu, ganinta a yanayi irin na ƴan aiki yasa shi sake cewa idan baza'a iya kula da ita ba to a kaita wajan iyayenta zama tafi samun kulawa a wajan su sosai. Da Jauhar taji abinda Doctor Habu yace ba ƙaramin daɗi taji ba dan ko babu komai tasan zata huta da wannan masifar ta cikin gidan Alhaji Sha'aban Sada. Nan likitan ya miƙo takardun magungunan da za'a siya masu daya rubuta Uncle Irfaan ya karɓa suka fice, Har sun kusa shiga mota Jannat ta kasa yin haƙuri tasan idan har suka bar asibitin nan zai yi wahala ta sake ganin Zain gashi sosai ya burgeta lokaci ɗaya saboda yadda yayita kanta da wasa tana dariya. Hannunta ta zare daga cikin na Mommy tace.

"Mommy please aron wayarki." Hajja Maimoon ta miƙa mata, cikin sauri Jannat ta juya tare da shigewa reciption tana wurga ido dan gano inda zata ganshi. Tsaye ta hangoshi gaban wata mata yana taɓa goshin yarinyar dake kan cinyar matar da alamar dubata yakeyi. Waya kawai yaga ana miƙo masa, kallan wayar ya yi kafin a hankali ya ɗora idanunsa akan wacce take miƙa

masa ɗin. Murmushi yayi tare da miƙewa sosai yana kallon wayar yake faɗin.

"Mommy's daughter yae za'a yi? Duba maki wayr zanyi itama bata lafiya?" Dariya Jannat tayi kafin ta turo baki cike da salon rigima tace,

"Dama banda mutane har wayoyi kana iya dubasu in basa da lafiya?"

"Ban taɓa ba amma da alama rigimar Mommy's doughter zatasa nafara yau."

"Ni dai a'a i just need Your phone number please." Zaro idanuwa yai cike da mamakin rigimar Jannat yana naɗe hannayensa a kirji haɗe da lasar lips ɗinsa na ƙasa ba tare daya karbi wayar ba. Jannat ta sake shagwaɓewa kamar zatai kuka tace.

"Please take it mana kasa mani kada uncle yai mun fada." Jin abinda tafaɗa shima ga patient na jiransa ya sashi dan duƙowa saiti ita yana cewa,

"Wayar kice?".

"No ta Mommyna ce." Zain ya sake ware ido akaro na biyu yana miƙewa tsaye da ƙafafuwansa yake cewa.

"Toh ba ruwa na haka kawai Daddyn ki yaga sunan namiji a ciki, da alama so kike nayi kwanan police station Ko?" Sai da ta kuma turo baki wanda yasa Zain kai hannunsa kamar zai janyo mata shi sai kuma ya karkaɗa mata yatsunsa guda biyu yana cewa.

"Ba ruwa na." Haɗe da ƙoƙarin juyawa.

"Please dan Allah dan annabi kasaka min, kaga idan bani da lafiya kawai kiranka za'a yi aji ko kana asibitin." Lumshe ido ya yi yana jin girman Allah da ta roƙeshi ya tsaya masa a wuya, ya karɓi wayar tare da saka mata dama already taji yadda abokan aikinsa suke ta kiransa dan haka bata tambayi sunan ba ta juya tana saving fuskarta kunshe da farin ciki ba zaka taɓa cewa ita aka kawo ranga-ranga ba. Babu wanda ta kula kawai ta shiga motar ta zauna, wannan karon a can wajan glass suka bar Jauhar a cewar Suhalai iska zata fi ɗaukar warin da Jauhar ɗin keyi tana fitarwa waje ba sai sun shaƙeta ba.

"Ke kuma me kika koma yi ciki?" Irfaan ya jehowa Jannat tambayar ba tare da ya juya ya kalleta ba hankalinsa yana wajan tuki. Jannat dake karewa sunan Zain da ta gama saving kallo tayi murmushi kawai ba tare da ta bawa Irfaan amsa ba dan ita kanta ba ta san me zatace ba, kuma bata san dalilin da yasa taji nurse ɗin ya shiga ranta da wuri haka ba. Jauhar kuwa duk ta matsu suje gida zama tare da su a wannan yanayin yana sake ɗaga mata hankali saboda fargabar maganganun da suke jefa mata ƙasa-ƙasa dan ma Suhana bata cewa komai amma yadda take kauda kai zaka san cewa tsamin jikin Jauhar ɗin yana damunta. Suna zuwa kuwa ta ɓalle ƙofar ta fito tare da rakuɓewa tana jiran su wuce ciki sannan tabi bayan su.

Hannun Jannat Hajja Maimoon ta kama ba tare data kalli gefen da Jauhar take ba tana jin wani irin jiri na addabarta. Kallon su ta shiga yi tana jin kuka na shirin zuwa mata, ina ma ace itama za'a kaita inda za'a ji ƙanta a kula da ita a kuma yi jinyarta cikin kulawa. Sanin bata da wannan gatan ne yasa ta fara ɗaga ƙafa jin Suhana tana cewa tazo su shiga ciki. Har ta juya taji Irfaan ya kirata, ta juyo a hankali ba tare da ta kalleshi ba dan ba kaɗan ba takejin kunyarsa.

"Zanje na kawo miki magunguna sai ki samu kisha kinji ko?" Jauhar ta ɗaga kai alamar to sannan ta buɗe baki da kyar tace.

"Nagode Uncle." Tausayinta ya sake shigarsa yace.

"Ki samu ki kwanta saboda jininki ya dawo dai-dai. Please ki cire komai a ranki kiyi addu'a  kinji ko?." Kanta kawai ta ɗaga amma ita bata ma san wace irin addu'a zatayi ba saboda ba wani koyar da ita aka yi ba ballantana ta dinga yiwa kanta. So yake ya tambayeta shin bata da bireziya ne da bata sakawa? Amma sai ya kasa saboda girman maganar gashi kuma baya son girmansa ya ɓare a wajan ta. Ko a hospital yaso yiwa Suhana maganar amma ya kasa. Har ta shiga ciki bai ɗauke ido akanta ba, yana son ya taimakawa Jauhar kota wani irin yanayi ne koda kuwa Hajja Maimoon zatayi masa sharrin da har ya koma ga Allah ba zai yi mutunci a idanun duniya ba. Yana fita daga gidan kai tsaye gidan su ya nufa ya ɗakko atm card ɗinsa ya fito, pharmacy ya wuce already Jannat tun a hospital aka siya mata nata magungunan, Jauhar ce Hajja Maimoon taki siyawa shi kuma bai fito da kuɗi ba. Yana siyo magungunan ya biya ta wani boutique ya siyo mata bra wacce bashi da masaniyar zatayi mata dai-dai ko zatayi mata yawa, kawai ya siyo mata ne gwara tasa akan ta dinga yawo a haka tana saka mutane cikin yanayin da sai sunyi shahada zasu iya rike kansu. Ya siya mata harda su pant da skirt underwear sai wasu riga da skirt kala ɗaya dan bai san awonta ba karya jidar mata kaya a samu matsala.

******

Jauhar na shiga cikin parlorn ta tarar Hajja Maimoon tana tsaye tana jiran shigowarta, tunda ta hangota taji kirjinta yana bugawa tasan kawai wani bala'in kecin matar tunda a iya saninta babu abinda tayi wanda zai sa ayi mata irin wannan jiran. Suhaila da Jannat suna kwance akan soofa Suhana ta shiga cikin ɗaki da alama ko tsayawa batayi a parlorn ba. Kanta ta sake sunkuyarwa tana jiran taji da wane bala'in za'a tare ita, cikin zuciyarta tace mutum bashi da lafiya amma matar nan ba zata ɗaga mata ƙafa ba taji da abinda yake damunta. Abinda yake bata haushi kuwa tamkar bata santa ba batasan wacece ita ba da ta wofintar da al'amarinta ta fifita wasu akanta wanda duk matsayin su a wajanta ai basu kaita ba, kuma tare aka gansu bare ace a gidan ta tarar da ita a matsayin mai aiki.

"Wato saboda nayi maganar ki fito min da gold ɗina shine dan bakin munafunci kika fara rashin lafiyar karya ko Jauhar? Toh bari kiji na gaya miki ko asibiti ne gabaki ɗaya a jikinki sai kin amayo min da abubuwana dan ba zakici banza ba. A iya zamana dake tun lokacin da aka liƙa min ke kika zame min jaraba na taɓa nuna miki yadda ake sata?" Jauhar ta shiga girgiza kai

alamar a'a, hakan ya sake tunzura Hajja Maimoon ta ƙarasa inda take tsaye tare da shaƙo mata wuya tana cewa.

"Dan ubanki da ka nake miki magana da zaki dinga amsa min da kanki?" Jauhar da taji matsar tana shirin kaita ga mutuwa yasa ta fara ƙoƙarin kwacewa, jikinta babu karfi hakan yasa ta kasa har sai da Suhana ta taho da gudu wacce fitowarta kenan daga cikin ɗaki ta hango su. Da kyar ta iya kwace Jauhar daga hannun Mommyn tasu wacce takejin ko mutuwa Jauhar tayi ba zatayi nadama ko da na sani ba koda kuwa ace zata mutu a gidan gyaran hali ne.

"Na kusa sallamaki wallahi Jauhar, da kaina zanje wajan waɗanda suka liƙa minke su san yadda zasu yi dake ko kuwa aure ne suyi miki da ko uban waye nima na huta da kallonki da nakeyi kina manne dani ko na dena sakaki a cikin idanuwa na." Jauhar dake rakube a bayan Suhana tana jin duk kalaman da Hajja Maimoon ke gaya mata, ita da za'a kaita ɗin da taji daɗi koda auran ne ayi mata ko zata samu ƴancin kanta, amma zama tare da matar nan ba alkairi bane a tare da ita.

"Mommy dan Allah ki barta bata da lafiya fa." Suhana ta faɗa kamar zata yi kuka. Duk suka kalleta baki buɗe, bata damu da irin kallonta da sukeyi ba burinta kawai ta aikata abinda zai sa mahaifiyarsu ta samu sassauci a makwancin ta kamar yadda Uncle Irfaan ya tunatar da ita.

"Zoki wuce ki shirya mana breakfast." Cewar Hajja Maimoon tana dakawa Jauhar ɗin wata gigitacciyar tsawa. Jiki na rawa hankali a tashi zuciya a cunkushe Jauhar ta nufi kitchen tana share hawayen da yake yawo a kan fuskarta........

#A heart touching story
#Gonar Sharri..
#Hajja ce
#Billy s Fari
#Ƴan Tagwaye

*ƳAN TAGWAYE BIYAR*

*GONAR SHARRI*
Billy S Fari & Hajja ce

*IDANIYAR RUWA*
(Mai wuyar toshewa)
Ayusher Muhd & Jeeddah Aliyu

*WATA ALAƘA*
Zee Bawa & Stylish bch

*BISHIYAR TSIYA*
(Wanda bai jiba bai gani ba ke girbar ki)
Umm Ashgar & Sadiya Dan.

*TSARIN ALLAH*
(Ba mai iya canzawa)
Asmy b Aliyu & Nana Diso

*ZAI IYA BIYAN*
GUDA 1 akan 500
GUDA 2 akan 800
GUDA 3 akan 1200
GUDA 4 akan 1600
GUDA 5 akan 2000

*BANK ACCOUNT*
8098456130
Opay digital services
Shaidar biya
07040402435
08098456130

*KATIN MTN*
07065283730
Shaidar biya ta lambar.
[8/1, 9:34 PM] Billy S Fari: *GONAR SHARRI...!*

*ƳAN TAGWAYE BIYAR*
(Batch C)

NA

*BILLY S FARI*💎
Da
*HAJJA CE*👈
Areewabooks@billysfari

Page 9..

Koda ta shiga kitchen ɗin rasa abinyi tayi dan gabaki ɗaya komai na cikin kwakwalwarta tsayawa ya yi cak na wucin gadi. Suhana ce ta shigo kitchen ɗin ita sai yanzu take lura da irin matsin da ake yiwa Jauhar a cikin gidan wanda tasan da mahaifiyarsu tana raye tabbas ba zata

bari su dinga yin abunda suke yiwa yarinyar ba. A bayanta ta tsaya tare da yi mata magana cewa.

"Jauhar kije ɗaki kiyi wanka mana, bari na fara tayaki kafin ki dawo." Jauhar ta girgiza kai dan ba zata iya fita ba Mommy ta ganta tasan sai ta kusan kashe ta musamman idan tace mata wanka zatayi.

"Idan na gama sai naje nayi." Cewar Jauhar ɗin tana sake share hawayen fuskarta.

"A'a kije kiyi saboda kayan jikin ki ma suna buƙatar ki sauya su." Ganin yadda Suhanar ke yi mata magana cike da jin ƙai ita duk tsoro ma sai ya kamata, tun a asibiti ta lura da sauyi a wajanta sosai. Tsoro take karta saki jiki da ita daga baya tayi mata sharrin da zata kasa fitar da kanta tunda ba haka ta saba ganin tana yi mata ba tunda tazo gidan nan. Amma ganin ta dage akan sai taje tayi wankan yasa taje wajan sink tasa hannunta ta tsiyayo liquid soap ta juya zata fita Suhana da ke kallanta da mamaki tace,

"Meza kiyi da shi?" Kanta a ƙasa tace,

"Zanje ne na ɗan goga a jikina ne."

"You mean dashi zaki wankan?" Suhana tafaɗa cikin tashin hankali tunda yasan ba na wanka bane har tana turo idanuwa waje, Jauhar ta ɗan dago ta kalli yanayin fuska da Suhana ta koma jiki ba kwari take faɗin.

"Dan Allah kiyi haƙuri shi nake ɗan ɗiba na goga a jikina idan zanyi wanka, kingani ba da yawa na tsiyaya ba." Tayi maganar tana buɗewa Suhana hannun alamar ta duba ta gani dan a tunaninta ran Suhana ɗin ya ɓaci zata ce tayi masu sata. Karo na farko da Suhana taji mugun tausayinta ganin da abinda zatayi wanka, su suna can sabulu sai sun zaɓa kuma duk masu tsada amma ita Jauhar tana nan ta rasa yadda zatayi tana ta raɓe-raɓe da abinda zata tsabtace jikinta ko tsoron yayi mata illa bata yi

"Ina zuwa." Cewar Suhana tana ficewa daga kitchen ɗin. Jauhar tabi ta da kallo, bata san me yasa tace tana zuwa ba dan haka da sauri taje ta ɗauki sosan wanke-wanke ta juye soap ɗin a jiki tare da zuwa tayi saurin ɗakko kettle taje ta tara ruwa a sink ta ɗora akan gas. Tea spieces ta zuba sannan tayi saurin ɗakko roba mai ɗan faɗi ta ɗebo Irish a ciki tana ferewa, zuciyarta bugawa kawai takeyi duk a zaton ta Suhana taje ne ta sanar da Hajja Maimoon cewa da abun wanke-wanken su take wanka bayan kuma Hajja Maimoon ɗin taja mata kunne akan cewa karta sake ta ɗauki abun su idan har ba bata aka yi ba. Suhana ta dawo tare da miƙa mata sabulu sabo dal a cikin kwalinsa tace taje tayi wankan bari ta ƙarasa mata aikin. Baki a wangale Jauhar ke kallonta ta kasa karɓar sabulun saboda tsabar mamaki har sai da Suhana ta riko hannunta ta saka mata sabulun aciki.

"Angode." Jauhar ta faɗa hawaye yana zuba a cikin idanunta haɗe dasa hannu tana shafewa.

"Ba komai jeki yo wankan ki dawo."

Fitowa Jauhar tayi ta shige ɗakinta, jiki babu karfi ta cire kayan ta nufi banɗakin dake cikin ɗakin nata. Ba ƙaramin daɗi taji ba yau tana wankan ƙamshin sabulun yana sa taji kamar ta lashe jikinta. Tana fitowa ta ɗauki yagalgalallan pant ɗinta wanda ita kanta ba zata ce ga tsawon shekarunsa ba duk ya buɗe ya tale ya yi baki ya dafe robar ta buɗe sai dai ta ƙulleshi ta gefen kugunta ta sanya shi yadda zai zauna mata.

Irfaan ne ya shigo parlorn da sallamarsa babu kowa duk sun koma ɗakunan su tun ɗazu. Kai tsaye ya nufi ɗakinta dan yasan yadda bata da lafiyar nan zai iya kasancewa tana ciki a kwance. Sai da ya yi knocking sannan ya murɗa handle ɗin ya shiga a nan ya tarar da ita tana saka kaya.

"Sorry Jauhar." Ya faɗa yana juya bayansa tare da miƙa mata ledar hannunsa yana cewa.

"Ga kaya nan ki saka karki maida na jikin ki, sannan da magani a ciki idan kinci abinci sai kisha." Jauhar mamaki ya kamata ta isa inda yake da kyar tasa hannu ta karɓi ledar, bai jira me zata ce ba yabar ɗakin daidai lokacin da Mommy ta fito ganinsa yana fitowa daga ɗakin Jauhar yasa ta ware idanunta tare da kafeshi da idanun tambaya mai cike da zargi, hakan da Irfaan ya gani ne yasa zuciyarsa ta ɗan yi rawa sai dai ya karfafa kansa tunda yasan babu abinda ya yi a cikin ɗakin saboda yana ganin kamar akwai wata manufa a kallon da Hajja Maimoon keyi masa ya tsuke fuska yana ƙoƙarin raba ta gefenta ya wuce.

"Lafiya naga ka fito daga ɗakin Jauhar?" Tayi maganar tana haɗe fuska.

"Na kai mata maganin da likita ya rubuta shine na siyo."

"Ohh good! Toh Irfaan daga yau daga yanzun ina so ka fita daga rayuwar Jauhar babu ruwanka da ita bana so." Duk da Irfaan besan me yasa Hajja Maimoon ɗin tafaɗi haka ba sai da maganar ta dakar masa zuciya dan baisan ya take son rayuwar Jauhar ɗin tazama ba, Jauhar kuwa yana bata ledar bayan ya fita tazaro duka abubuwan dake ciki, ganin irin kayan yasa ta rintsa ido sunyi matukar kyau sai dai tasan bai zama lallai abar mata ba dan ansha bata kaya amma Hajja Maimoon sai ta kwace. Murmushi tayi lokacin da ta zaro bra ɗin ga wata kunya da ta lulluɓeta. Cike da jin nauyi tamkar ance mata Irfaan ɗin yana wajan. Da sauri ta rintsa ido lokacin da ta gama sakawa taga fitulun nata sun yi kyau a ciki duk kuwa da cewa ba wai manya bane suna kan fitowa. Duk kunya ce ta kamata a haka ta kammala saka komai sai ta dinga jin tamkar ba ita ba, zata so ganin yadda tayi a cikin kayan dan kuwa babu madubi a cikin ɗakin. Tunawa tayi da glass ɗin window tayi saurin juyawa ta fito daga ɗakin nata dan zuwa taga yadda tayi.

Karaf sukayi ido huɗu da Hajja Maimoon, baki buɗe take kallonta cikin kayan da daga gani masu tsada ne. Jauhar tayi cak ta kasa barin wajan da take tsaye sai hankalinta da ya tashi dan bata son ganin matar nan a cikin idanunta. Kallonta kawai Irfaan keyi daya fara kokarin barin

wajen yana ji zuciyarsa tana biya masa wani irin karatu akan Jauhar ɗin. Muryar Hajja Maimoon kawai sukaji tana tafa hannuwa tana kallon Jauhar da tayi ƙasa da kanta tana jiran jin yadda za'a yi da ita. Suhaila da Jannat suka fito da sauri yayin da Suhana ma ta baro kitchen ɗin duk suka zubawa Jauhar idanuwa bakin su a buɗe tamkar sunga abin tsoro.

"Wannan yana nuna cewar da ta sace min gold ɗina bayar dashi tayi sai ake siyo mata kaya ko?" Maido idanuwansa Irfaan yai jin kalaman dake fitowa bakinta masu kama da gugar zana yace

"Wait Aunty please dan Allah haba mana, wane irin gold ɗinki aka siyar? Me kika ɗauke ni ne? Kinsan ni ba matsiyaci bane, sannan bandogara da kowa ba ballantana kice sai an sammin wani abun nake iya gudanar da rayuwa ta ba. Enough is enough na kawowa Jauhar kaya ne saboda bai kamata dan tana matsayin mai'aki amma ace a yadda take jage-jage a gidan nan haka take rayuwa tare da ku ba. Bansan wane gold kike magana ba dan haka maganarsa ta tsaya iya nan." Ya faɗa yana juyawa zai bar wajan, cikin gadara da nuna isa Hajja Maimoon ta ƙarasa wajan Jauhar tana cewa.

"Iskancin banza zanyi lokacinka ne, ke kuma muje ki ciro su bazaki saka su ba dan baki cancanci irin waɗannan kayan ba, saboda rainin hankali za'a baki wannan kayan salon a kasa ware ki da yaran gidan? Ina son kowa ya tsaya a matsayinsa, Jauhar kayan nan ba kalar darajarki bane ba dan baki cancanci saka irin su a jikinki ba. Oya muje ki ciro su kafin ma ku saba dasu, ina nan ina jiran ki fito min da gold ɗina shine ke kina gefe guda kina zaɓar abubuwan da suka fiki mutunci da daraja." Kallanta kawai Jauhar keyi tana jin wani baƙin ciki yana mamaye mata zuciya. Kallan da takeyiwa Hajja Maimoon ne yasa ta buga mata wata uwar tsawa wacce tasa Jauhar ɗin shigewa cikin ɗaki da gudu. Wani irin gigitaccen kuka ta saki mai taɓa zuciya tana yi tana cire kayan daga jikinta, ita kam ta rasa irin ƙiyayar da Hajja Maimoon keyi mata. Idan ta gaji da ganinta ta kaita inda ba zata sake ganinta ba mana, ta kaita ayi mata auran da take ta faɗa koda zata samu sassauci daga zaman ƙuncin nan da takeyi yanzu. Ta gaji bazata iya jurewa ba dan kuwa babu alamar Hajja Maimoon zata ji ƙanta bare ta bata farin ciki dai-dai dana rana ɗaya.

"Ki gaya min gaskiya Jauhar me kike bawa Irfaan da har yake miki irin waɗannan abubuwan?." Abinda Jauhar ta jiyo Hajja Maimoon na faɗa daga bakin ƙofar zuwa shigowa cikin ɗakinta. Kafin tace wani abun ta ƙaraso ciki tasa hannu duk ta kwashe kayan, ta kalli Jauhar ɗin ta hango bra ɗin jikinta, da sauri ta ɗaga zanin da Jauhar ɗin tayi ɗaurin kirji dashi, nan ta hango sabon pant mai kyau. Gabanta ne ya faɗi ta zaro ido tana damƙo wuyan Jauhar ɗin cikin tashin hankali take magana.

"Harda waɗannan abubuwan ya siya miki?" Jauhar cike da tsoro tace,

"Dan Allah Mommy..." Kau...! Hajja Maimoon ta kwashe mata kumatu da mari mai zafin gaske.

"Kiyi hakuri Hajiya." Kallan juna suka yi Hajja Maimoon da ranta yake sake ɓaci tace.

"Ki gaya min ya akai yasan baki da kayan ciki? Naji wannan ya siya miki ne saboda baya ganin kina saka masu kyau, amma pant da bireziyar nan na jikin ki ko ki sanar dani yadda akai yasan size ɗinki ko kuma yanzun nan nayi gunduwa-gunduwa dake dan na kashe ki dan ubanki." Wani irin kuka ya kwacewa Jauhar take cewa.

"Allah kuwa babu abinda na bashi." Hajja Maimoon ta sake shaƙo mata wuya Suhana tayi saurin zuwa tana son kwatar Jauhar cike da tashin hankali.

"Mommy ki rabu da ita please." Cikin sauri Hajja Maimoon ta kalli Suhana tana cewa,

"Doughter kinsan abinda tayi ne? Ko kin gane abinda nake tunanin ta aikata Suhana?" Girgiza kai Suhana tayi alamar bata gane ba, Jannat dake bayan su ce tace,

"Ta fara canza ɗabi'a daga sata tana son fin karfinki Mommy." Hajja Maimoon taja tsaki jin babu wanda yake tunanin abinda take zargin Jauhar ɗin ta farayi. Cikin fushi ta ture ta tana faɗin.

"Wallahi baki isa ki janyo min wata masifa ba Jauhar, bazan ɗauki ɓacin rai da tashin hankali ba kamar yadda ubanki bai ɗauka ba son zuciya yasa da shaiɗanci baki rayu a hannunsa ba sannan ni kuma ki jefani a damuwa. Aure ɗaya tak nayi a rayuwata kuma bana son ganin wani abun yazo ya min shamaki a cikin sa. Ki kiyayeni Jauhar bake ba Irfaan da duk wani namiji ma. Babu ke babu soyayya dan kuwa baki da rabon yin ta a cikin duniyar nan." Kuka Jauhar ɗin keyi amma babu mai lallashinta, Suhana ma da taje zata tayar da ita hanawa Mommyn tayi. Tassss ta kwashe duk wasu abubuwan da Irfaan ya kawo har maganin bata bar mata ba. Jiki a sanyaye Jauhar ta maida kayanta masu dauɗa sannan ta dawo kitchen lokacin sauran kaɗan Suhana ta kammala soya dankalin. Kallonta Suhana tayi ganin yadda take kuka kamar ranta zai fita tace,

"Kiyi hakuri Jauhar ban san me yasa Mommy bata tausaya miki ta kowane yanayi ba. Shin wai ina ne garin ku Jauhar?" Jauhar ta share hawayen fuskarta tana cewa.

"Mommy ce komai nawa tun bansan wacece ni ba, ban san kowa ba sai ita. Kuma idan zataje can garin na mu bata tafiya dani sai dai muyi waya da Kakanni nawa idan taje. Lokacin da zasu yi aure da Daddyn ku a gidan da take zaune a nan ƴan uwan namu suka zo aka ɗaura a kuma ranar ne na gansu inda suka yi ta bani haƙuri suna cewa Allah zai saka min. Ban san me yasa basu jani wajan su ba suka barni a wajan ta kuma bata sona." Yadda tayi maganar ya matukar sanyaya jikin Suhana, cike da tausayinta take ce mata.

"Kiyi haƙuri dama haka Allah yake abubuwan sa akan bawa, mu ma kinga bamu rasa komai ba gashi nan amma mahaifiyar mu bata tare da mu." Cikin sauri Jauhar tace,

"Ni da ku ba ɗaya bane Suhana, ku ga mahaifin ku nan kuma kunsan inda mahaifiyarku take. Ni kuma ban rayu dasu ba, tun sanda naji Kaka na yana cewa. Allah bazai kyale iyaye na ba akan

zarafi na da sukaci na kan so naji me yasa suka barni? Idan nazo tambayarsu ina iyayen nawa? Sai Hajiya ta make min baki tace na fiye shegiyar tambaya sai kace in naji inda suke wani abun zasu tsinana min." Jauhar ta ƙarasa muryarta na daɗa karyewa.

"Kiyi hakuri." Suhana ta faɗa dan bata da wani abun sake faɗa. Suna kammalawa suka jera komai a dining table, su Suhaila kamar zasu mutu dan ganin yadda Suhana ke yiwa Jauhar ɗin. Jannat ta dinga yin kwafa tana ji a ranta bazai yiwu su bar Suhana ta dinga biyewa Jauhar ba, yau kawai sunga ta canza tamkar ba Suhana da suka sani a baya ba. Kujera Suhana ta janyo ta zauna duk da tana kallon yadda ƴan uwan nata suke harararta bata kulasu ba. Jauhar na gefe tun lokacin da suke aikin taji wata irin yunwa tana taso mata, nata yana kitchen wanda Suhana ta ɗibar mata tace idan ta kammala komai ta zauna taci. Tana son komawa kitchen ɗin amma tana tsoran juyawa ta bar gurin wata ta buƙaci abu aga bata nan. Fitowar Hajja Maimoon yasa Jauhar sake kama nutsuwarta kanta a ƙasa tana tsoran kallonta. Da hannu Hajja Maimoon ta nunawa Jauhar ɗin hanya alamar tabar wajan bama ta san ganinta bare har wani abun ya haɗa su. Hakan ba ƙaramin daɗi yaiwa Jauhar ba dan sai takejin tamkar an yaye mata wani nauyi da ya tsaya a kirjinta. Kitchen ta zauna ta janyo abincin da Suhana ta rage mata, zama tayi ta fara ci tana tunanin yaushe daɗi zai zo mata kamar yadda take ganin mutane cike da walwala Ali yaushe.

******

Kunnensa sakale da wayarsa yana magana a haka ya shiga bedroom ɗinsa, Hajja Maimoon ya tarar ta fito daga bathroom fuskarta duk ruwa da alama wanketa tayi. Murmushi ta sakar masa tare da ƙarasawa wajansa tayi hugging ɗinsa rightside dai-dai lokacin da ya sauke wayar bayan sunyi sallama da wanda yake wayar. Sosai ya janyota cikin jikinsa tare da janta suka isa wajan madubi yana cewa.

"Madam ki shirya zamuje wajan siyan zinarinki, sonake daga can ɗin a yau ɗin nan kiyi magana da mai kayan da kika ce zaki fara business ɗinsu. Kuɗi ne suka zo min so bana son kuma su tafi cikin harkokina ba tare da na cika miki alƙawuran dana ɗauka ba." Hajja Maimoon ta ware ido duk irin ajinta da kwalisarta sai da ta bayyana farin ciki tana yi masa godiya tare da addu'o'i na karin buɗi da kuma gamawa da duniya lafiya. Sake riƙo hannunsa tayi tana kallon fuskarsa take cewa.

"Ya Habiby me zanyi dan na biyaka kwatankwacin irin wannan farin cikin daka sani?" Kafin ya yi magana tace.

"Ka sanar da ni komenene I will definitely do it yadda ka sani farin cikin nan." Murmushi ya yi kawai shi a ganinsa wannan abun da zai yi mata ba komai bane ba, hasalima yana ganin tamkar hakkinsa ne ya yi mata shi musamman ma jarin da yake son ya bata. Kallonta ya yi yana matse kafaɗunta yake cewa......

#A heart touching story
#Gonar Sharri..
#Hajja ce
#Billy s Fari
#Ƴan Tagwaye

*ƳAN TAGWAYE BIYAR*

*GONAR SHARRI*
Billy S Fari & Hajja ce

*IDANIYAR RUWA*
(Mai wuyar toshewa)
Ayusher Muhd & Jeeddah Aliyu

*WATA ALAƘA*
Zee Bawa & Stylish bch

*BISHIYAR TSIYA*
(Wanda bai jiba bai gani ba ke girbar ki)
Umm Ashgar & Sadiya Dan.

*TSARIN ALLAH*
(Ba mai iya canzawa)
Asmy b Aliyu & Nana Diso

*ZAI IYA BIYAN*
GUDA 1 akan 500
GUDA 2 akan 800
GUDA 3 akan 1200
GUDA 4 akan 1600
GUDA 5 akan 2000

*BANK ACCOUNT*
8098456130
Opay digital services
Shaidar biya
07040402435
08098456130

*KATIN MTN*
07065283730

Shaidar biya ta lambar.
[8/1, 9:34 PM] Billy S Fari: *GONAR SHARRI...!*

*ƳAN TAGWAYE BIYAR*
(Batch C)

NA

*BILLY S FARI*💎
Da
*HAJJA CE*👈
Arewabook@billysfari

Page 10..

"Mommyn Jannat babu abinda nake buƙata a gareki sama da kulawar da kike bani, wannan kaɗai ya wadatar dani domin duk abinda zanyi miki wajibina ne nayi miki, but akwai alfarma ɗaya da nake son roƙonki sai dai bana so kiyi tunanin ko don zan yimiki waɗannan abubuwan ne zan roƙeki ita...." Ɗan yatsa Hajja Maimoon ta ɗora a saman labɓansa tun kafin yaƙarasa rufe bakinsa, cike da kulawa ta riƙo hannunsa tana matsawa a hankali tare da kallonsa tana narkewa haɗe da cewa.

"Ka fadi abinda kake so kai tsaye ina tabbatar maka da zanyi maka ba tare da ɓacin rai ba ko musanta maka ba, faɗamun meye Ya Habiby?" Taƙare zancen tana kallon cikin idanuwansa. Murmushi yai haɗe da ɗago hannunta dake riƙe da nasa ya sumbata sannan ya kalleta yace,

"Ina so kada kisake ɗakko zancen gold ɗinki daya ɓata, Please kibar zancen nan ya wuce kada ya zama wata damuwa tunda Allah zai baki wanda yafishi kin ji ko?" Ya faɗa yana nuna mata son abar zancen akan fuskarsa. Sai da tayi murmushi tare da shigewa jikinsa tace,

"Shikenan Ya Habiby bazan sake ɗakko zancen ba in sha Allahu." Hajja Maimoon tafaɗa ba don ranta ya so hakan ba tana ƙara jin tsanar Jauhar acikin zuciyarta. A cewar ta ba dan ta ɗauke gold ɗin ba idan ta haɗasa da wanda Dady zai saya mata yanzu ba ƙaramar kaddara zata tara ba, gashi ta janyo mata asarar da batasan ranar maidata ba koda kuwa kullum zata samu ƙarin gold don ta riga ta rasa wancan ɗin da ba ƙananan kuɗi ne dashi ba. Tana wannan tunanin taji yai hugging ɗinta duka yana cewa.

"Thank you so much Madam. Ya jikin ƴar taki?" Sai da Hajja Maimoon ta sake shigewa cikin jikinsa sannan tace,

"Taji sauƙi." Har zai tambayi jikin Jauhar ɗin sai ya tuna ba lallai hakan yayi mata daɗi ba, dan haka ya kama bakinsa yayi shiru ya shiga ƙoƙarin rage kayan jikinsa Hajja Maimoon na taimaka masa.

Alhaji Sha'aban Sada na kammala shiryawa cikin kaya marasa nauyi da suka karɓi jikinsa sosai suka nufo palour shida ita, duka yaran na kwance saman kujerun palourn suna kallo Jannat ce kaɗai ke zaune riƙe da wayar Mommy tana buga game, tana ganin Daddyn nasu ta taso tayo wajensa yasa hannu ya rungumeta yana kallonta cike da kulawa. Cike da sakalci take rungume hannunsa tana kwantar da kanta.

"Dady sannu da dawowa." Suhana da Suhaila suka faɗa atare, cike da jin daɗin ganin su ya amsa hankalinsa nakan Jannat ɗin yana tambayarta ya jikin nata ita kuma tana sake shigewa jikinsa cike da shagwaɓa take amsa masa da taji sauki. Da haka suka ƙarasa wajen dinning da Jauhar ke sake gyarawa saboda basu jima da kammala lunch ba. Cikin girmamawa kan Jauhar a ƙasa ta gaishesa tana ƙoƙarin barin wajen saboda mugun kallon da Mommy ke wurga mata, sai taji Daddyn ya dakatar da ita yana tambayarta.

"Ya jikin naki?"

"Naji sauki Dady."

"ALLAH yaƙara sauƙi." Yafaɗa yana basar da zancen ba tare daya bi takan Mommy data juyo tana kallonsa ba na jin tambayar da yai wa Jauhar. Ita fa sam bata son duk wani abu mai kama da tausayi ko kuma kulawa ya dinga ta'allaƙa da Jauhar bare har ta sameshi acikin gidan, so takeyi ko yaushe Jauhar ta kasance cikin kunci da baƙin ciki kamar yadda ta zamo silar shigarta cikinsu a lokutan baya. Da wannan tunanin ta shiga zuba masa abinci yaci, yana kammalawa yace ta shiga ta dakko mayafinta suje yana jiranta a waje.

"Dady zan je nima." Jannat tafaɗa har lokacin hankalinta na akan game ɗin da take bugawa. Hannun da Hajja Maimoon ta miƙawa Jannat ɗin ne yasa Jannat ta miƙe mata nata Hajja Maimoon ɗin tana cewa,

"Oya taso muje ki sauya kayan jikinki." Jannat tamiƙa mata hannun suka wuce Dady ya bisu da kallo cike da so dan idan ka gansu tamkar Hajja Maimoon ɗin ce ta haifeta, wannan na daga cikin dalilan dake sa a kullum yake ƙara jin kaunar Hajja Maimoon tare da hauhawar matsayinta a cikin zuciyarsa yanda ta ɗauki ƴaƴasa tamkar ita ta haifesu.

---

"Wai lafiya ka samu waje ka zauna kana faman cika ina yi maka magana ka ƙyaleni? Meke faruwa ne Irfaan?" Hajiya ta faɗa tana tsaresa da idanuwa, jin yai shiru bai amsa mata ba yasa takira Inna Deeje mai aikinta tace takawo masa ruwa, ba'a jima ba sai gata ta dawo ɗauke da ɗan ƙaramin tray ta ɗoro gorar ruwa mai sanyi da cup data wanko ta ajiye masa agabansa,

"Ɗauki ruwa kasha." Hajiya ta faɗa tana ba Irfaan ɗin umurni. Sai da yai kamar bai jita ba kafin ya ɗauki ruwan ya tsiyaya yasha, ya dire cup ɗin lokaci ɗaya tare da nauyayyen numfashin dake nuni da zuciyarsa daskare take da ɓacin rai. A karo na biyu Hajiya ta sake jeho masa

tambayar da tayi masa a farko da take cike da son jin amsar ta, dan yanda tasan halayyar ɗan nata da dabi'unsa ba ƙaramin abu bane ke jefasa a irin wannan yanayin damuwa da kuma ɓacin ran ba.

"Hajiya wai meyasa sam babu ɗigon tausayin yarinyar can a zuciyar Hajja Maimoon, me yasa take wulakantata da ƙasƙantar da ita haka? bayan Allah ya ɗaukaka ɗan Adam ya kuma darajasa? Shin ita ba mutum bace ko kuma ita ta zaɓawa kanta rayuwa a yadda take? Duk da itace ta zo da ita gidan a ganina be daje ana treeting yarinyar nan haka ba." Nauyayyar ajiyar zuciya Hajiya ta sauke dan bata ɗauka damuwar ɗan nata akan wannan matsalar bace da ita kanta ta jima tana cimata tuwo a ƙwarya, kawai ba yadda zatayi ne tunda tare ta gansu da yarinyar. Amma sam bata jin daɗin yadda ake kawo mata labarin irin wahalhalun da yarinyar ke sha da tsangwamar da akeyi mata a gidan ɗan nata. Kallonsa tayi tace,

"Bansan dalili ko hujjar da tasa Hajiya Maimuna take yin hakan ba bayan ita tazo da yarinyar nan gidan, meke faruwa ne halan?" Nan fa Irfaan ya kwashe komai ya sanar da Hajiya har yana ƙarawa da cewa.

"Hajiya nafahimci so takeyi kowa ya guji yarinyar nan ya cutar da ita kamar yadda takeyi, sai dai ni bazan taɓa yin hakan ba saboda har cikin zuciyata nake jin tausayin yarinyar nan. Kuma wallahil azhim Hajiya tayi duk abinda ta yi bazan fasa taimakon Jauhar ba da dukkanin karfina da kuma dukiyata ba sai dai tayi min duk sharrin dataga zata iya ni kuma zan ɗauka kuma zan jure har lokacin da Allah zai kawowa Jauhar mafitar tafiya daga wannan kangin bautar da takeyi. Ni wallahi Yaya ne ma har mamaki yake bani akan abubuwan da akewa yarinyar nan agaban idanuwansa amma baya cewa komai. Bansan yaushe zuciyarsa takoma haka ba!" Hajiya ta sauke numfashi, tabbas abun babu daɗi, gashi ita kam duk abinda zai taɓa mutuncin Alhaji Sha'aban bata son shi, dalilin da yasa kullum gidan ta sai an sauke tukunyar abincin sadaka da niyar Allah ubangiji ya ƙare mata shi ya kuma ci gaba da rufa masa asiri duniya da lahira. Bata taɓa sanar da kowa dalilin yin girke-girken da take sawa ayi ba daga ita sai Allah. Ajiyar zuciya ta sauke tare da faɗin.

"Allah ya kyauta, ita kuma Jauhar ɗin Allah yai mata mafita ta alkairi, ni wannan abun duk laifin iyayenta nake gani aciki, bazan hanaka taimakonta ba amma kariƙa yin taka tsantsan tunda bata so, kuma ta fika kusanci da iyayan yarinyar." Jin Hajiya ta karfafa masa guiwa yasa yaji nutsuwa ta fara saukar masa yace,

"To Hajiya amma fa indai ta sake yimin sharri wallahi ajiye girman Yaya zanyi nafaɗa mata ba daɗi tunda zuciyarta ba imani da tausayi, yarinya ƙarama ki zauna kina azabtar da ita ko da me hakan zai rageta..?" Duk suka yi shiru Hajiya ta kasa cewa komai. Haka Irfaan yai ta magana Hajiya na kallonsa tana son gano wani abu tattare dashi akan yarinyar har ya gama faɗan ya tashi ya fita.

---

Kasuwar Rimi Alhaji Sha'aban Sada ya nufa yai parking a bakin wani katafaren store na

Muhammad gold accessories. Tare suka buɗe murfin motar suka fito yana gaba Hajja Maimoon na biye dashi a baya riƙe da hannun Jannat, juyowa yai bayan sun shiga ciki yace ta duba ta zaɓi duk sarkar data yi mata ta dai-dai adadin kuɗin waccan da aka ɗauke mata. Nan take Hajja Maimoon ta saki murmushi ta shiga duba sarkokin gwalagwalan dake wajen. Sai da ta kusan zagaye ko'ina can ta hango wacce tayi dai-dai da zabinta sannan ta nuna tace ita take so Alhaji Sha'aban yace a ɗakko mata ba tare daya damu da sanin ko nawa take ba har sai da aka ɗakko. Sosai Hajja Maimoon ta girgiza da jin adadin kudin sarkar dan sun kusa ninka na sarkar ta da aka sace sau uku, amma ga mamakinta ko tsayawa tayawa baiyi ba ya fitar da kuɗin duka ya biya aka miƙo masa sarkar tare da reciept ɗin ya miƙa mata. Tsabar farin ciki ruɗewa Hajja Maimoon tayi ta rungumeshi a wajen tana zuba masa godiya dan ko a mafarki bata sa ran zata mallaki sarka mai tsada irinta ba, hannun Jannat ta kama suka fice shi kuma ya tsaya wajen ya duba wata sarkar gold ɗin da zata dace da mahaifiyarsa ya siya ya jefa cikin aljihunsa.

A can waje kuwa Hajja Maimoon ƙawarta takira tana sanar mata haɗe da shaida mata sarkartata da aka dauke har tana faɗa mata tsadar wacce Alhaji Sha'aban ya siya mata ɗin yanzu. Kasancewar tana cikin farin ciki har sanar da ita irin ribar da taci da wannan sabuwar. Sosai aminiyarta ta tayata murna tare da sake ɗora ta akan hanyar da zata ribatu da kuɗin Alhaji Sha'aban Sada ɗin tunda baya iya bayarwa sai da dalili. Tana hango shi yafito tayi saurin yin sallama da ita tana cewa sai takirata zasu ƙarasa magana idan takoma gida. Daga nan kuma wajen shakatawa suka nufa suka ɗan zazzagayo dan Alhaji Sha'aban mutum ne mai son wayewa da kuma burge iyali. Bayan sun kammala suka nufi hanyar komawa gida, nan yake yimata zancen a ina take son yin business ɗinta? A online ko kuma a gida? Murmushi ta saki haɗe da cewa,

"Gaskiya bana son business a gida, online kuma ai kaga kamar kafa ne da zan tallata kayan, in son samu ne kawai shago zan kama a zuba kayan aciki ina sayarwa ko ya ka gani?" Shiru yai dan har ga Allah duk abinda zai janyo tawayar samun kulawarta gareshi baya so, kuma gashi yana son ya kyautata mata kamar yadda take kyautata masa shi da yaransa.

"Ya Habiby ya naji kayi shiru? I think is better da azo ana cika maka gida, kare da doki wasu ma su cuce mu ta hanyar zuwa gidan da zasu yi." Juyowa yai ya kalleta kafin yaci gaba da tukin yake cewa.

"Wannan ni ba matsalata bace indai zanci gaba da samun kulawarki, kin sani bana son kinayin nisa dani inba dole ba shiyasa zancen shagon nan bai kwanta mani ba."

"Oh God! Ya Habiby hakan fa bazai canza komai ba a kulawar da nake baka, I promise you that." Tayi maganar cikin kashe murya tana wani mammatsa hannunsa cike da salon son shawo kansa. Sake juyowa yai yana kallonta yace,

"Are you sure?." Bata iya amsa masa ba saboda ta shagaltu wajen yimasa wani irin fitinannen kallo daya kusa dakatar da bugawar zuciyarsa sai dai ta ɗaga masa kai alamun

"Eh".

Take Alhaji Sha'aban Sada yaji jikinsa ya mutu ya samu daƙyar suka ƙaraso gida suka nufi sashensa kai tsaye. Jannat kuma ta kwashi kayan kwalam ɗin daya siya musu ita da ƴan uwanta ta wuce musu dashi.

A takaice duk da yadda lokacin magriba ya soma karatowa sai da Hajja Maimoon ta jefasa duniyar da suka farantawa junansu haɗe da samawa kansu natsuwa. Bayan yafito wanka yace tayi magana da ƙawarta da zata turo mata kayan ta turo mata account zai tura mata adadin kuɗin da zata zabi duk abinda take so, ya kuma ce akwai shaguna acan farkon titi kafin a shigo unguwarsu da ake talla zai kama mata guda biyu sai a haɗe a sake gyara mata su kafin kayan su iso. Hajja Maimoon taji daɗi sai taji darajarta ta sake girmama, addu'a sosai tayita masa har da kwallarta ta farin cikin ganin mafarkanta sun fara tabbata, sannan atake takira ƙawar tata tace ta turo mata account ɗinta, ba'a jima ba ta turo mata taba Alhaji Sha'aban ɗin shi kuma atake awajen ya tura mata kuɗin yace tafara gwadawa dasu, idan yaga kasuwar ta karɓeta to zai ƙara mata wasu sannan ya mike ya nufi masallaci yana cemata daga can zai biya gidan Hajiya ya gaisheta. Har mota ta rakosa tana yi masa adawo lafiya sannan takoma ciki zuciyarta cike fal da farin ciki tana ganin auran ta da Alhaji Sha'aban nasararta ne kuma matakin daukakarta ne.

---

Tunda ya doso ƙofar gidan annurin dake kan fuskarsa ya soma gushewa har ya ƙaraso wajen ganin ƙanwar tasa Husnah tsaye da wani agefen gidansu. Tsaye yai yana ƙarewa yaron kallo tun daga sama har ƙasa, sanye yake da gajeren wando iya guiwa, sai riga armless mara hannuwa wuyansa sanye da wata kafceciyar sarƙa ƴar Chaina. idanuwansa ne suka sauka akan kunnen Guy ɗin daya sanye da ɗan kunne tamkar mace sai kansa daya sha wani irin aski na Bobby, acikin mintuna biyu kacal yaƙare masa kallon da ya gama tabbatar masa da cewa gaba ɗaya yaron ba musulmi bane, ransa ne ya sake ɓaci lokacin da idanuwansa suka sauka akan takalman dake ƙafafuwansa wasu irin kafta-kafta farare irin canvas ɗin nan na gayu dake ji da kansu. Rai aɓace Zain yai parking mashin ɗinsa a ƙofar gida ya sauko ya nufo wajen da suke tsaye sun shagalta da aikawa juna wani irin kallon soyayya. Wata uwar tsawa ya dakawa Husnah da tasa tayi wata irin zabura yace ta wuce cikin gida. Baki sake Zain yake bin yaron da kallo lokacin daya miƙo masa hannu cikin girmamawa yana cewa,

"Assalamu alaikum, Yaya barka da dawowa." Me hakan ke nufi? Kenan wannan yaron yana nufin shi musulmi ne yake cikin irin wannan shigar da ba ta da banbanci data ƙabilu? Daƙyar ya iya buɗe baki ya amsa masa sallamar da yai masa yana cewa,

"Ko menene tsakanika da ƙanwata ka rabu da ita saboda karatu zatayi, a mutunce nake faɗa maka hakan kafin akai ga ɓacin rai tsakanina dakai idan nakuma ganinka a ƙofar gidan nan, babu kai babu ita kana jina ko?" Zain yaƙare maganar haɗe da kama kunnensa ɗaya alamun jan kunne sannan ya juya rai aɓace ya wuce cikin gidansu. Saurayin kuma mai suna Iliya ya bishi da kallo cike da mamaki kafin yaja tsaki yace,

"Wannan kwafsa min zai dinga yi kenan? Ahhh lallai za'a kwashi uwar watsi indai akan Huscy ne. Kai..! Lallai ma gayen nan, wato duk wannan gayun nawa dana kwaso dan na burge yarinyar nan sai da ya yimun bakin cikin yin hira da ita. Mtssss! wallahi ni da Huscybaby mutu karaba dan bakin ciki kawai. Zaka gane waye ILLiyasmarter na rantse da Allah kuwa." Daga haka yaja kafafuwansa da daƙyar yake ɗaga su yana jefawa irin tafiyar ƴan iskan nan saboda nauyin takalmin. ILIYA ɗan nan cikin garin su ne acan kauyen dake gabansu, ya jima yana son Husnah tun tana jss 3 amma yadda yake ganin takunta irin na yaran masu kuɗi ƴan gayu yasa ya ɗauki alwashin zama gaye kafin ya tunkareta dan yasan hakan kaɗai zai sa ta saurararsa. Yayi nasara kuwa domin tun a ganin farko da Husnah taji yes zai yi daidai da wanda zata iya tsayawa.

Zain kuwa yana shiga gida Husnah na tsaye a ƙofar ɗaki ta cukuikuye hijabin ta na makarantar boko data dawo dan ta maraice takeyi tana faman haɗe rai, bai tsaya wata-wata ba yana shiga yayo kanta. Husnah kuwa da gudu ta ɓuya bayan mahaifiyarta dake kukkulle kayan yaji.

"Kai..kai wai lafiya Zain? Meye haka daga dawowarka zaka rufar min yarinya? Me kika yimasa ne?" Taƙare zancen tana juyowa wajen Husnah dake faman tura baki,

"Ba dake nake ba ko sai nabarshi yayi miki shegen duka?" Cike da son a kareta tace,

"Mama ni banyi mashi komai ba.." Kanta da ya yo ne yasa ta kasa karasa maganar, Mama tayi saurin tareshi. Cikin ɓacin rai yace,

"Mama da wani ɗan iskan saurayi na ganta fa a waje sunq tsaye kana ganinsa kaga Christian." Cike da jin haushi Husnah ta ɗago kai tana cewa.

"Ya Zain bafa Christian bane, sunansa Iliya kuma so na yakeyi." Da sauri Mama tace,

"To kaji amma zaka zo ka saukewa yarinya ɓacin rai, ai sai ka mayar da wukar tunda kaji masoyinta ne, ko kuma kana nufin bata kai munzalin tsayawa da saurayi ba?" Baki Zain ya saki jin abinda mahaifiyar tasa ke cewa kafin yace,

"Mama Husnah guda nawa ce da zata fara kule-kulen samar? kinga yaron kuwa? Na rantse kada kibari na sake ganinki dashi idan ba haka ba na lahira sai ya fiki jin daɗi." Cikin sauri Mama tace dashi.

"Toh sannu ubanta, nace sannu isasshe gawurtacce, idan bata kula samari ba taya kake so ta zabo mijin aurenta? Ko kai zata aura? Nifa bana son haka tunda ba kamata kayi tana yin dabi'u marasa kyau ba ka ƙyaleta ta kula duk wanda yazo wajenta, ta haka zata tantance mijin aure tunda ba zama zatayi muna kallonta ba..." Wani irin haushi ya sake kama Zain yana kallan Mama yama rasa ta yadda zai suffanta mata yadda Iliyan yake. Rai a ɓace ya nufi ɗakinsa yana jin zuciyarsa na masa zafi, wai ace wannan guy ɗin ne zai nemi ƙanwarsa saboda ance ciwon

makanta ya kama su. Idan har yana numfashi bazai bar ILIYA tare da jininsa ba.....

#A heart touching story
#Gonar Sharri..
#Hajja ce
#Billy s Fari
#Ƴan Tagwaye

*ƳAN TAGWAYE BIYAR*

*GONAR SHARRI*
Billy S Fari & Hajja ce

*IDANIYAR RUWA*
(Mai wuyar toshewa)
Ayusher Muhd & Jeeddah Aliyu

*WATA ALAƘA*
Zee Bawa & Stylish bch

*BISHIYAR TSIYA*
(Wanda bai jiba bai gani ba ke girbar ki)
Umm Ashgar & Sadiya Dan.

*TSARIN ALLAH*
(Ba mai iya canzawa)
Asmy b Aliyu & Nana Diso

*ZAI IYA BIYAN*
GUDA 1 akan 500
GUDA 2 akan 800
GUDA 3 akan 1200
GUDA 4 akan 1600
GUDA 5 akan 2000

*BANK ACCOUNT*
8098456130
Opay digital services
Shaidar biya
07040402435 ko
08098456130

*KATIN MTN*
07065283730
Shaidar biya ta lambar.
[8/1, 9:34 PM] Billy S Fari: *GONAR SHARRI...!*

*ƳAN TAGWAYE BIYAR*
(Batch C)

NA

*BILLY S FARI*💎
Da
*HAJJA CE*👈
Arewabook@billysfari

Page 11..

Da yake yau tana cikin farin ciki gabaki ɗaya ta manta da wata Jauhar a cikin gidan, su Suhaila ta tarar a parlour suna ta cin kayan kwalam ɗin da Jannat tazo musu dashi wanda ko tunanin ajiyewa Jauhar basu yi ba, dama ita tsakanin ta da irin abubuwan sai idan sun rage taje gyara gurin idan taji abu ya bata sha'awa koya burgeta sai ta ɗauka taci idan na ci ne, idan kuma na sha ne shima ta tsotse ta maida mugun yawu. Dukkansu kallonta sukeyi ganin farin ciki yaki gushewa akan fuskarta yasa Suhaila gyara zama tana murmushi take cewa.

"Mommy sai farin ciki kike yi ko ƙanwa za'a yiwa Baby Jay?" Duk da kasancewar kalmar tayi matukar nauyi da ya kamata ace Hajja Maimoon ta yiwa Suhaila magana akai, sai kawai Hajja Maimoon ɗin tayi dariya kasancewar farin cikin da take ciki bata kawo wani abu na ɓacin rai a lokacin bare har ta tsawatar tana cewa.

"No... No.. No Suhaila! Ni ai kun isheni hakan nan ba sai an sake kawo wani babyn ba. Ku tayani murna zan fara business kamar yadda kuka san cewa dama tun da nazo ina yinsa. Kunsan ƴar matsala na samu wacce tasa dole na ajiye komai. Kuma wannan karon ba a gida kawai zanyi ba Daddyn ku zai kama min shago a can bakin titi." Gabaki ɗayansu suka tayata murna wanda hakan ya sake farantawa Hajja Maimoon zuciya tana sake jin yaran a cikin zuciyarta.

———

Tunda ya nufi layin gidan mutane suke ɗaga masa hannu yana yi musu horn alamar amsawa fuskarsa kunshe da murmushi. Yana isa wajan gate ya yi parking bai shiga da motar ba kasancewar ba daɗewa zai yi a ciki ba. Har Alhaji Sha'aban ya shiga parlorn Hajiyarsu mutanan dake shawagi a gidan basu dena gaishe shi ba. Zaune ya tarar dasu tana inda take zama tayi sallah yayin da Irfaan ke kwance cikin 3seater ya ɗora laptop a saman cikin sa yana aiki a ciki.

Maryam ƙanwarsu wacce ta kasance auta a wajan Hajiya tana zaune wajan center table ta ɗora handouts da alama assignment takeyi, shigowarsa yasa har Hajiya dake dama fura cikin ƙoƙo sai da ta dawo da hankalinta wajansa, sosai take jinsa a ranta haka kuma bata haɗashi da kowa a kaf cikin yaranta, kauna take masa wacce ita kanta idan aka ce ta faɗi irinta ba zata iya bayyanawa ba saboda mutum ne shi da yake bata matsayinta na uwa a gareshi fiye da tunani.

"Hajiya sannu da aiki." Ta amsa masa,

"Yauwa sannu da shigowa. Maimakon kayi kwanciyarka ka huta shine sai da ka taso kazo har nan?" Murmushi yayi yace,

"Hajiya ai nazo naga lafiyarki, idan na kwanta banzo ba tunani zantayi ina jin babu daɗi."

"Yaya sannu da zuwa." Maryam ta faɗa tana karkaɗa biron hannunta.

"Yauwa Auta kina ganin Hajiya na aiki baki tayata ba ko?" Cikin sauri Maryam tace.

"Yaya wallahi cewa tayi in bar mata zatayi wai ban iya dama furar yadda takeso ba." Ta faɗa tana maida idanunta kan takardun ta.

"Eh naji, amma da ta faɗi hakan maimakon kizo kiga yadda takeso ɗin ki koya shine kika barta tana yi." Irfaan dake kwance ne ya tashi zaune yana cewa.

"Yaya barka da zuwa." Yana magana yana haɗe rai tamkar wanda basa zaman lafiya.

"Yauwa Irfaan." Alhaji Sha'aban ya furta yana kallon yanayinsa, duk da cewar yawan tambaya akan abinda ba'a nemi ya sani ba baya daga cikin al'amuransa. Sai dai a yanayin ɗaya ga ƙanin nasa yasa shi son jin ko meye damuwarsa.

"Naga kamar kana cikin ɓacin rai, lafiya dai ko?" Irfaan ya sake tsuke fuska yana janyo wayarsa dake gefensa yace.

"Ba komai." Hajiya najin su tayi murmushi jin abinda Irfaan yace. Dama zaiyi wahala ya iya gayawa Yayan nasu abinda yake damunsa domin suna masa kallon uba ne dan shine tsaye akan su. Hajiya tasan duk masifar da Irfaan yayi akan matsalar Jauhar da yake cewa harda laifin Alhaji Sha'aban tasan ko da wasa ba zai iya rufe ido ya yi a gabansa ba. Kallon Maryam Hajiya tayi tace.

"Zoki ɗakko kofi na zubawa Yayanku fura da nono yasha." Da sauri Alhaji Sha'aban yace.

"A'a Hajiya kisha abarki." Maryam jin yace abarshi yasa ta koma ta zauna, Hajiya ta kalleta.

"Ke kuma daga yace insha abuna shine kika fasa ɗakkowa? Yanzu fa naji ya yi miki faɗa akan

kulawa da abubuwa. Tashi ki ɗakko ai ba mai yawa zan zuba maka ba."

"Nima fa nace zan sha." Cewar Irfaan jin ba'a ce a taho da nashi kofin ba.

"Kai da kace sai mai ayaba da kwakwa a ciki? Meye kuma na canza shawara?" Alhaji Sha'aban yace,

"Kishi ne da alama." Gabaki ɗaya sukayi dariya. Kofuna uku Maryam ta dire tana durƙushewa a gaban Hajiya tare da cewa.

"Kawo na zuba mana." Da sauri Alhaji Sha'aban ya nufi wajan, karɓar ƙoƙon ya yi tare da cewa,

"Kawo nasan wayo kika shirya yiwa Hajiya ta." Duk suka sake yin dariya ya zubawa kowa a cikin kofi shima ya zuba ƴar kaɗan dan ma kartaga bai shaba taji babu daɗi shi yasa ya zuba. Sai da ya fara miƙa mata wacce zata sha sannan ya miƙe ya koma kan kujera. Irfaan ya karɓi tashi a hannun Maryam ya nufi wajan fridge, ƙanƙara da madarar freshyo ya zuba a ciki sannan ya koma inda ya taso ya zauna.

"Wai meke faruwa tsakanin Maimuna da yarinyar nan da take mata aiki?" Hajiya ta jefo maganar wacce sai da Alhaji Sha'aban yaji ta har cikin zuciyarsa dan bai taɓa tunanin zatayi masa ita ba. Irfaan yai saurin tashi zai bar gurin dan bai shirya yin wannan maganar da Yayansa ba.

"Dawo ka zauna Irfaan ai da kai za'a yi maganar." Cike da wata irin kunya ya koma duk da yana jin zuciyarsa tana karfafa shi akan karya ƙi yin abinda yake ganin mafuta ce a wajan Jauhar. Kamar marar gaskiya haka ya koma ya zauna yana jujjuya spoon ɗin hannunsa yama kasa shan furar yadda ya kamata.

"Hajiya wani abun ne ya faru? Daga gidan nake amma banji ance da matsala ba." Hajiya bata ce komai ba sai kallon inda Irfaan yake da tayi tana jiran ya yi bayani. Dariya ce ta kwace mata ganin ko inda suke zaune Irfaan ɗin be kalla ba dan haka Hajiya ta daure tare da cewa.

"Sanar masa abinda ya faru Irfaan." Cike da jin nauyi dan baisan a yadda Alhaji Sha'aban ɗin zai ɗauki maganar da zai yi ba. Da kyar Irfaan ya daure jin da yayi shi ake jira ya yi bayani, ya daure yace.

"Yaya kamar dai yadda kasani ne, ni wallahi kawai bana son ana cin zalin yarinyar nan saboda duk abinda ya sameta a gidan Yayana ne. Bana son naga ana musguna mata kuma wai a gidanka Yaya kai da kake mutum mai tausayi akan komai..."

"Please kayi min bayani sosai meke faruwa a gidan nawa?" Alhaji Sha'aban ya katse shi dan ya matsu yaji. Murya Irfaan ya sanyaya tare da sake yin ƙasa da kanshi yace.

"Jauhar koda ta kasance ƴar aiki a gidanka, sam bai dace ana yi mata wasu abubuwan ba. Yaya kaga kai ne kace mu tafi da yarinyar nan asibiti amma wallahi karkaga da yadda suka yadda ta shiga motar nan, munje asibitin ma aka rubuta magunguna amma haka Aunty Maimoon tace ba zata siya dana Jauhar ɗin ba tasa aka bada na Jannat kaɗai. Duk da haka Yaya na fito na siyawa Jauhar ɗin magani da kuɗi na sai na haɗa da wata ƴar riga nace tayi amfani dasu dan naga a yadda take rayuwa kuma wai a gidan ka Yaya. Shine Auntyn ta kwace kayan harda cewa wai...." Da sauri Alhaji Sha'aban ya katse shi dan yanaji a ransa maganar karshen babu alkairi a cikinta kuma yasan itace mafi munin ji a duk maganganun da yake ji daga bakin ƙanin nasa. Shi kansa yafi su jin rashin daɗin yadda ake yiwa yarinyar, ya yi kuma iya yinsa wajan nunar da Maimoon hakan ba daidai bane amma ta nuna masa cewa tun daga wajan iyayenta komai yake faruwa, ta kuma tabbatar masa da cewa idan har ta bari Jauhar ta samu kwanciyar hankali toh tabbas ita kuma zata kasance cikin damuwa. A lokacin ya hango tsantsar haushi, bakin ciki da kuma damuwa akan fuskarta wanda ya tabbatar da har ranta take jin haushin cewa da ya yi ta kula da yarinyar.

"Wai kana sane ake yiwa yarinyar nan haka? Kulawarta yana kanka fa yanzu ba wai dan tana mai aiki ba kayi shiru ana mata ba daidai ba. Kuma ita kaɗai ce ake samun matsalar nan ko masu gadi sun fita jin daɗi da kwanciyar hankali ita da take mace mai ƙananun shekaru. Idan ba zaku kula da ita ba ya kamata ku maidawa iyayenta abarsu suyi yadda zasuyi da ita, bana son zalunci ban kuma koya muku shi ba, haka zalika bance ku bari ayi ba." Shiru Alhaji Sha'aban ya yi yana jin damuwa a cikin zuciyarsa, shi kam besan yadda zai yi da matsalar nan ba harga Allah, amma saboda ya kwantar musu da hankali tunda dai sun shiga damuwar ne saboda shi dan haka cikin taushin murya yake cewa.

"Insha Allahu za'a gyara Hajiya, ni nafi ganin laifin iyayen Jauhar saboda tun lokacin da nake neman auran Maimoon tare suke kuma babu abinda ya canza na game da yadda suke rayuwa da ita. Naso yiwa mahaifin Maimoon magana amma ya nuna min cewa gwara abarta a wajanta yafi mutunci akansu su riƙe ta."

"Kasan ɗan kauye kuma da muguwar kafiya, ana nuna masa gabas yana cewa yamma yafi. Duk da haka kayi ƙoƙarin ganin an sassautawa yarinyar, haka duk sanda Maryam taje gidanka sai tayi min ƙorafin yadda take ganin yarinyar, kuma wai da kazantar nan take yi muku girki ku cinye." Alhaji Sha'aban dai ya yi shiru baice komai ba dan shi kansa abun nan yana bashi haushi yadda Jauhar take rayuwa dasu cikin rashin daraja. Ganin Hajiya tasa baki yasa Irfaan yaji hankalinsa ya ɗan kwanta, sannan yaji karfin guiwar samun damar taimakawa Jauhar ɗin. Sun taɓa hira sosai kafin yasa hannu cikin aljihu ya zaro sarƙa da ɗankunnen da ya siyawa Hajiyan, ya miƙe tare da isa wajanta ya durƙusa har ƙasa ya saka mata a cikin tafin hannunta. Kallon hannun Hajiya tayi kafin ta kalleshi da sauri tana cewa.

"Na menene wannan?" Cike da soyayya yace.

"Naki ne Hajiya." Kallon hannun ta sake yi tana jin zuciyarta na karyewa, ta kalleshi kamar zatayi kuka dan muryarta har rawa takeyi kafin tace.

"Me yasa kake san wahalar da kanka? Haka kawai kaje ka kashe kuɗinka maimakon kasasu cikin kasuwancin ka shine zaka siyo min zinari? Ina dasu fa wajan guda nawa ma amma kaje ka sake siyo min." Murmushi ya yi tare da miƙewa tsaye yana cewa.

"Haba Hajiya, duk wani abu da zan miki koma bayan abinda kika yi min ne, ko shagon zinari na kawo miki Hajiya ban isa na biyaki ba bare dan ma siyo miki wannan. Allah ya kara miki lafiya da nisan kwana domin ke ɗin garkuwa ne a garemu." Maryam ce ta taho da gudu, karɓar ƴankunnayen tayi tana jujjuyawa kafin ta narke fuska tana turo baki take faɗin.

"Toh Yaya nifa?" Ya kalleta tare da faɗin.

"Ohhh haɗa kanki kike yi da Hajiyata?" Sai da ta sake shagwaɓewa tana noƙe kafaɗa tace.

"Ni da nake ƴan mata ai ni zaka dinga kashewa kuɗi Yaya, Hajiya fa tana dasu da yawa."

"Ki bari idan kasuwa ta sake yin kyau sai na bawa Irfaan kuje a siya miki." Alhaji Sha'aban ya faɗa yana kallonta.

"Yaya kasuwa fa tana kyau, ko addu'ar da Hajiya keyi maka kaɗai ta isa tasa kasuwancinka habɓaka bare mutane da bakinsu baya gajiya wajan yi maka addu'o'i. Kawai nidai Yaya ka ce zaka tura masa kuɗin." Maryam ta faɗa tare da langaɓe kai. Sai da ya saki murmushi yace.

"Shikenan Irfaan zan tura maka sai kuje tare ta siyo." Farin ciki ya kama Maryam ta shiga murna tana yi masa addu'a Hajiya kuma na sake sanya masa albarka. Sallama ya yi musu inda Irfaan ya tashi yabi bayansa sukaje har bakin motarsa.

"Kayi amfani da Atm ɗina na wajanka Sai kuje a siyawa Maryam ɗin, ina so a siya kayan abinci a kaiwa Kawu Ibrahim karka manta dan Allah Irfaan." Cike da girmamawa Irfaan ɗin ya amsa daga nan Alhaji Sha'aban ya shiga motarsa yaja yabar unguwar.

---

Tsaki ya dinga saki ba ƙaƙƙautawa, banda zafi babu abinda zuciyarsa keyi, yaso Mama ta barshi ya faffallawa Husnah mari ko zata farka daga nannauyan baccin da takeyi na ganinta da Ilyasmater dan shi a ganinsa mafarki kawai takeyi shi yasa har ta tsaya tana sauraransa harda cewa wai saurayinta ne. A hankali ya zare rigar jikinsa yaje ya sagaleta yana sake jin wani ɓacin rai a ransa. Jikinsa babu kwari ya shiga ɓalle belt ɗin dake ɗaure a ƙugunsa ya kasa cire hotan guy ɗin nan a cikin idanunsa dama zuciyarsa. Ba irin mazan da yake son ƙannansa su dinga kulawa bane, yana da wani irin buri akan ƙannansa dan haka ne ma yake da mugun taka tsantsan akan tsare mutunci da kuma ƙimarsa dan kar yaje shima a yiwa wata a cikin ƙannansa. Jeans ɗin jikinsa ya cire ya rage daga shi sai gajeran wanda da black singlet, Wanka yake son ya yi sai dai baya son sake komawa cikin gidan. Ɗakinsa yabi da kallo yana jin takaicin rashin bathroom da babu a ciki. Da kyar ya iya karfafa zuciyarsa ya janyo jallabiyarsa

da yake shiga wanka da ita ya sanya bayan ya cire singlet ɗin jikin nashi. Kwandan wankansa ya ɗauka sannan ya fito tare da janyo ƙofar ya shiga cikin gidan. Cikin sa'a ya tarar da Husnah tana tarar ruwa a fanfo bataji motsinsa ba sai ji tayi kawai an sakar mata rankwashi a tsakiyar kanta, kafin ta ɗago taji yana cewa.

"Sakarai kawai, wannan gayen meye abun burgewa tare dashi? Idan na sake ganinki dashi sai na miki shegen duka a gidan nan, bazan bari ki janyo mana surutun mutane ba." Yana kaiwa nan ya ɗauke bokitin ruwan da ta tara ya shige toilet ya barta. Husnah ta saki kuka tana rugawa cikin parlorn Mama da gudu kamar wacce aka biyo.

"Mama kinga Yaya Zain ko?" Cewar Husnah tana dafe da tsakiyar kanta.

"Kai innalillahi Wainna ilaihir raji'un wai dama bekyale ki ba da nace babu ruwansa?"

"Kuma har cewa ya yi idan na sake kula saurayi sai ya min shegen duka." Husnah ta faɗa tana sake rushewa da kuka.

"Ina jin dai auran ku zai yi, banda haka banga dalilin da zai sa yaron nan ya dinga takura muku ba dan kun kula samari, bari ya fito zai sameni gwara ya yi min bayani naji idan ya yi shirin auran ku ne sai naji dalili." Ta ƙarasa maganar tana ɗaga murya yadda Zain ɗin zai jiyo.

Rufe bakinta keda wuya sai ga Abba ya shigo. "Haba! Dawa kike wannan faɗa ake jin muryarki har ƙofar gida?" Yafaɗa yana miƙawa Husnah dake yimasa sannu da zuwa ledar dake hannunsa.

"Sannu da dawo." Itama Mama tafaɗa cikin ɗan ɓacin rai tana miƙewa daga kwance da take Husnah kuma ta karbi ledar da yake miƙo mata ta nufi kitchen da ita. "Ni da waye banda Zain kuwa yabi duk ya takurawa yarinyar nan sai kace ba ƙanwarsa ba." Sai da Abba ya zauna saman kujera sannan ya amsa sannu da Mama tayi masa yana cewa.

"In banda abunki meye laifi idan ya tsawatar mata tunda yayanta ne? Ai hakan shine dai-dai tashi ki je ki kawo mani ruwa." Yaƙare zancen haɗe da cire hular kansa ya ɗora saman hannun kujera.

Mama bata ce komai ba taje ta kawo masa abincinsa da ruwa ta ajiye masa agabansa sannan ta zuba masa ya soma ci. Bayan ya kammala ta tattare wajen ta kwashe kayan takai kitchen ta dawo. Nan ta shiga labarta masa abinda ke faruwa ba tare data tuna da halin mijin nata ba da ba goyon bayanta zaiyi ba akan wannan, dan in dai akan tarbiyar yaransa ce a tsaye yake sosai. Sauke lumfashi yai cike da mamaki yana kallonta kafin yace.

"Ina tunanin Alhamdulillah girma yazo kin sauya daga Halimar dana sani ada kin koma wata kamilalliyar Halima uwa da zata cigaba da tayani ba 'ya'yana tarbiyya idan bana kusa ashe har yau akwai sauran rina a kaba? Yanzu fisabilillahi wannan dan iskan yaro Iliya da naji ya ma

sauya sunansa ya koma Iliyasmaster tsabar rashin ji ko ke kika ganta tsaye dashi baza ki koreta ki hanata sake tsayawa dashi ba? To bari kiji in faɗa maki ba Zain ba wlh koni na sake samun labarin angata tsaye da wannan ɗan iskan yaro lalatacce sai na ɓaɓɓallata kuma kema saina saɓa maki dan bazan lamunci wannan shashancin ba acikin gidana." Ya ƙare maganar cikin faɗa haɗe da ɗaukar hularsa ya maida akai ya fice daga gidan dan an kira sallar magrib, da kallo tabishi bata iya cewa komai ba saboda ranta aɓace yake itama akan ƙa'idojin nan nashi da yake kira tarbiyya dake hanata rawar gaban hantsi ita da yaranta...

#A heart touching story
#Gonar Sharri
#Billy s Fari
#Hajja ce 👈
#Ƴan Tagwaye

*ƳAN TAGWAYE BIYAR*

*GONAR SHARRI*
Billy S Fari & Hajja ce

*IDANIYAR RUWA*
(Mai wuyar toshewa)
Ayusher Muhd & Jeeddah Aliyu

*WATA ALAƘA*
Zee Bawa & Stylish bch

*BISHIYAR TSIYA*
(Wanda bai jiba bai gani ba ke girbar ki)
Umm Ashgar & Sadiya Dan.

*TSARIN ALLAH*
(Ba mai iya canzawa)
Asmy b Aliyu & Nana Diso

*ZAI IYA BIYAN*
GUDA 1 akan 500
GUDA 2 akan 800
GUDA 3 akan 1200
GUDA 4 akan 1600

GUDA 5 akan 2000

*BANK ACCOUNT*
8098456130
Opay digital services
Shaidar biya
07040402435
08098456130

*KATIN MTN*
07065283730
Shaidar biya ta lambar.
[8/1, 9:34 PM] Billy S Fari: *GONAR SHARRI...!*

*ƳAN TAGWAYE BIYAR*
(Batch C)

NA

*BILLY S FARI*💎
Da
*HAJJA CE*👈
Arewabook@billysfari

*Assalamu alaikum*

_Ina masu son ayi masu Logo ko flyer, E-book cover's ko stickers, invitation card ko kuma invitation vedio domin ƙawata kasuwancinku da janyo hankulan customers ɗinku? To ku matso kusa ga S fari graphic design sun shirya tsaf domin yimaku abinda zai zo daidai da ra'ayinku bisa farashi mai sauƙi._

Sai ku tuntuɓemu ta
CALL OR WATSAPP
07040402435/07081675855.

Mungode.

Page 12..

Ɗaya daga cikin ƙananun shagon Alhaji Sha'aban Irfaan ɗin yaje ya kwaso duk wani abu da ya sani na daga kayan abinci kafin ya nufi gidan kawun nasu. Sai da Irfaan ɗin yasa almajirai suka sauke masa kayan abincin dake makare a boot ɗin motar suka shiga dashi ciki sannan yabi bayansu. Anan cikin zauren gidan ya iskosa zaune tare da almajiransa yana biya masu karatu.

Gefe ya samu ya tsaya haɗe da fiddo wayarsa yana latsawa har sai da su kawun suka kammala almajiran suka tashi suka tafi, jefa wayarsa Irfaan ya yi cikin aljihu ya ƙarasa bisa tabarmar ya zauna cike da girmamawa yana gaida kawu Ibrahim ɗin dake tattare littafan gaban nasa waje ɗaya yana mayarwa gefe. Fuskar kawu Ibrahim a sake ya ɗago kai tare da miƙa masa hannu sukayi musabiha yana amsa gaisuwar da ya yi masa yana ɗorawa da cewa.

"Sannu da ƙoƙari malam Irfaan ya mahaifiyar taku da ƴan uwan naka?"

"Duk suna lafiya Kawu sunce na gaisheka sosai, ga saƙonan inji Yaya yace akawo maka."

"Masha Allah, agaida Alhaji Sha'aban, ubangiji Allah yai masa albarka ya jiƙan mahaifinku. Yadda kuke kula dani tamkar ni na haifeku Allah ya kula da zuri'arku gabaki ɗaya. Nagode nagode sosai Allah ya saka da alkhairi kaima Allah ya yi maka albarka."

"Amin ya rabbi kawu."

"Taso mushiga ciki kasha ruwa kafin kawuce." Kawu Ibrahim ya faɗa yana miƙewa haɗe da gyara babbar rigarsa sannan ya yi gaba zuwa ciki. Ba yadda Irfaan ya iya dole ya miƙe yabi bayanshi suka shiga ciki.

Zaune take tana wanke kwanuka Umma na jiranta zata kwashe abinci saboda bata jima da dawowa wajen haddar Alqur'ani da suke tasowa ba bayan sallar magriba. Sallamar mahaifin nata daya shigo yana ƙwalawa Umma kira yasa ta ɗago kai, karaf sukayi ido biyu da masoyin nata da ya kafeta da idanuwa, dan tunda Irfaan yake da ita bai taɓa zuwa gidan ya iskota cikin irin wannan shigar ba ta riga da skert, da yake wuyan rigar na da ɗan faɗi zaka iya hango tudun albarkatun ƙirjinta da take dasu masha Allah. Da su Irfaan yai tozali lokacin dayake shigowa, hakan yasa yakasa ɗauke idanuwansa akanta har sai data lura da hakan ta shiga ƴan kame-kame. Murmushi Irfaan ya sakar mata ta sadda kanta ƙasa cike da jin kunya shi kuma yaƙarasa ciki ya zauna saman tabarmar da Umma ta shimfiɗa masa suka shiga gaisawa da ita tana tambayarsa ya Hajiya take.

Ganin haka yasa Ayusher ta miƙe ta kwashe kwanonin ta nufi kitchen kirjinta na bugawa ta shiga kwashe abincin kafin Umma tazo.

"Tashi kije ku gaisa da Yayanki sai ki kai masa ruwa na ƙarasa kwashe abincin sai kizo ki ɗaukar masa nashi ki kai masa." Ayusher taji mahaifiyarta ta data shigo kitchen ɗin yanzu tafaɗa tana ƙoƙarin karɓar abun kwashe abincin a hannunta. Ɗaki Ayusher tafara shiga ta sanyo hijab ɗinta haɗe da dakko ruwan leda guda biyu masu sanyi ta ɗoro akan plate ta nufo wajensu. gabansa ta ajiye plate ɗin ruwan ta zauna, ceke da natsuwa take cewa.

"Ya Irfaan sannu da zuwa, ina wuni?"

Daidai nan aka aiko yaro ana yiwa kawu Ibrahim sallama awaje dan haka ya miƙe yafice daga

gidan ya basu waje. Da idanuwa Irfaan ya bita yana ƙara jin ƙaunarta na ratsa masa zuciya, kunya da natsuwa na ɗaya daga cikin abubuwan dake sashi yake ƙara jin sonta akoda yaushe. Ɗan lumfasawa yai sannan ya amsa mata da cewa.

"Lafiya kalau Ayusher har an taso daga wajen haddar?"

"Eh, ya Hajiya da Ya Maryam da wajensu Suhana?"

"Kowa lafiya kalau." Daga haka shiru ya ratsa tsakaninsu na mintuna sakamakon ruwan da Irfaan ya ɗauka yana sha,

"Alhamdulillah." Yafaɗa yana ajiye sauran ruwan a plate, miƙewa tayi da zimmar zuwa ta karɓo masa abincin kamar yadda Ummanta ta buƙata yai saurin dakatar da ita.

"Ina zuwa kuma bayan ko lafiyata baki tambaya ba?" Murmushi ta saki kafin tace,

"Ai naga lafiyarki ƙalau shiyasa ban tambayeka ba, bari nazo Umma tace na karɓo maka abinci."

"A'a dawo ki zauna alhamdulillah a ƙoshe nake."

"Wane irin ƙoshe kuma Irfaan ga abinci angama, ke Ayusher je ki dauko masa kinji ko?" Suka ji muryar Umma tafaɗa daga tsakar gidan. Kallonsa tayi ta sakar mashi murmushi tana ɗage kafaɗa alamun ba ruwanta, 'yar hararar wasa Irfaan ɗin ya aika mata da ita tabar wajen tana dariya.

Tuwon shinkafa ne da miyar agushi wacce tasha tantakwashin naman rago da man shanu, Ayusher takawo masa agabansa tayi masa saving da kanta yaci suna ɗan taɓa fira, dan suna ɗaukar gidan su Ayusher ɗin tamkar gidansu kasancewar da mahaifinta da mahaifinsa uwa ɗaya uba ɗaya suke, kuma duk da rashin wadatarsu sosai basu taɓa nuna ƙyanƙyami ko kuma ƙyamarsu ba idan sun zo gidan. Hakan yasa Irfaan ya saki jiki ya ɗan ci abincin kaɗan yace ya koshi saboda da gaske yakeyi akoshe yake, kawai baya son yiwa Umma gardama ne yaki ci taji ba daɗi.

Kwashe kayan Ayusher ta sake yi sannan ta dawo ta tadda shi har ya miƙe yana yiwa Umma sallama tana yimasa godiya haɗe da sanya masa albarka shi da Yayan nasa, ta kuma ce idan yaje yayi masu godiya sosai wajen Alhaji Sha'aban da Hajiya. Har zaure Ayusher ta rakashi kafin tace,

"Toh Ya Irfaan Allah ya kiyaye ya tsare hanya, ina gaida su Hajiya."

"Amin 'yan matana, amma sakonki kije da kanki." Ya faɗa cike da son sanya ta magana,

"Kai Ya Irfaan! Nice fa?" Ta faɗa tana langaɓe kai.

"Eh ai nasan ke ɗin ce, kin girma tubarkallah kamar ba ƴar yarinyar da nake goyawa ba, ina zuwa zan sanar da Yaya yazo ayi magana da Kawu abani aurenki in huta da hadiyar yawu." Irfaan ya faɗa cike da tsokana yana murmushi. Ayusher tasa tafin hannayenta ta rufe fuskarta haɗe da barin wajen aguje dan ba ƙaramar kunya kalaman nasa suka sakar mata ba. Irfaan yasa dariya yana kallonta har ta shige ciki sannan ya juya yafice daga cikin gidan. A bakin ƙofar gidan sukayi karo da Kawu Ibrahim wanda har bakon nasa ya tafi zai shigo gidan. Irfaan ya ɗan rissina yana cemasa zai wuce.

"Toh ka gaida mahaifiyar taku sosai Nagode Allah yai maku albarka." Kawu Ibrahim yafaɗa yana miƙa masa hannu suka sake yin musabiha sannan Irfaan ya shiga motarsa ya tayar ya wuce.

---

Cikin sati ɗaya duka kayan da Hajja Maimoon tayi odar suka iso tasa aka kawo mata su har gida aka baje su a nan tsakiyar palourn ƙasa ta watsesu ɗaya bayan ɗaya tana lissafa komai ta gani idan ya iso dai-dai kafin akai su shago. Suhaila ke taimaka mata wajen haɗa lissafin yayin da Suhana da Jannat ke gyara mata kayan suna haɗa su waje ɗaya. Bayan tagama haɗa komai tace kowacensu ta zaɓi abinda takeso kafin akwashi kayan anjima akai shago. Jauhar dake rakuɓe gefe taji kamar itama abata damar ɗaukar abunda take so da ta ɗauki wata ƴar ƙaramar jaka data hango mai kyau data burgeta, fannin dogayen riguna da ƙananan kaya ne kawai bata damu dasu ba balle har taga abinda ya burgeta, haka ma takalma da mayafan kala-kala da turarukkan ƙamshi irin masu tsadar nan na waje duk hankalinta bai kai wajen ba, kyan jakar ne ya sake janta bayansu Suhaila sun zazzaɓi abubuwan da suke so tace.

"Mommy dan Allah na ɗauki waccan jakar..?"

Kafin taƙarasa rufe baki Hajja Maimoon ta jefeta da wani kwali da aka cire cikin wata jakar cikin ɓacin rai a tsawace tace,

"Me na gaya maki akan ganin yaran nan da abu kisa ran kema zaki mallaki irinsa, su sa'aninki ne ko an faɗa maki matsayinku ɗaya dasu? Tukuna ma bance kidena kirana Mommyn nan ba amma kika sake? rainani kikayi ko Jauhar?" Yadda ta dire maganar cikin wani karaji tana yowa kanta yasa Jauhar ɗin miƙewa da gudu tabar palourn ta zagaya ta can bayan kitchen.

"Ƙaramar mara kunyar yarinya da ki tsaya na nuna maki banbancin dake tsakanin waɗanda keda gatan mahaifi dake da baki da wata daraja ko gata awajen ubanki tunda har yakasa zuwa ya ɗaukeki agabana, shashasha kawai. Wannan da kike ganinsu, su ɗin ƴaƴan so ne kuma ƴan gatan iyayensu gaba da baya masu mutunci da daraja, kefa? Wane so iyayen naki keyi maki balle kisa ran zaki samu gatantawa irin tasu?" Hajja Maimoon ta ƙare maganar tana haɗa zufa saboda tsabar masifa duk da sanyin A.c dake tashi acikin palourn. Kallo Suhana da jikinta duk ya mutu ta bi Hajja Maimoon dashi ganin irin masifar da data balbali Jauhar da ita da irin maganganun da take faffaɗa mata tamkar mai yi da sa'arta, shin ina iyayen Jauhar ne? Me suka yiwa Mommy haka data tsani ƴarsu bata sonta? Shin basu san halin da take ciki bane ko

a'a da baza su zo su ɗauketa ba takoma hannunsu?. Tambayar data jefawa kanta kenan da a ƴan kwanakin nan take yawan yiwa kanta amma tarasa wanda zai amsa mata su, cikin sanyin murya tace,

"Mommy dan Allah kibata tunda tana.." Kasa ƙarasa maganar tayi ganin yadda Hajja Maimoon ta fizgo kai tana kallonta sai dai ta sadda kanta ƙasa tana cewa.

"Sorry Mommy."  Sannan tabar wajen. Suhaila da Jannat ko ɗauke kai sukayi suka kwashi kayan su suka haye sama dan ko ajininsu.

Daɓas Hajja Maimoon tafaɗa kan kujerar tana ɗage kanta da taji ya soma yi mata wani irin ciwo, wai yaushe tayi sanyin da har Jauhar tafara tunanin amfani da kayan kyale-kyali a rayuwarta? Yaushe mafarkanta suka nuna mata irin wannan rana zata taɓa zo mata bayan ita ɗin ba kowa bace acikin gidan? Lallai dole ta sake tashi tsaye ta nuna mata wutsiyar raƙumi tayi nesa da ƙasa. Da wannan tunanin ta jingina ajikin kujera haɗe da lumshe idanuwanta suka rufe tana laluben ko meye mafita.

Jauhar na zuwa bayan kitchen ta zube ƙasa ta haɗe kai da giwowinta waje ɗaya ta saka wani irin kuka jin kalaman da Hajja Maimoon ke jifanta dasu tana mai dana sanin tambayarta abinda take da yakinin cewa koda zata mutu bazata taɓa samu ba a wajenta. Gashi ta tada mata da fami a zuciyarta na son sanin inda iyayenta suka shiga suka barta a hannun matar da tafi ƙaunar mutuwa da ita. Shin kodai da gaske mahaifinta baya sonta shiyasa yabarta babu wata kulawa balle gata kamar yadda kowane ɗa ke samu agun iyayensa? Da haka bacci mai nauyi ya ɗauke ta awajen har akayi sallar la'asar ba tare data sani ba.

_Bayan kwana biyu_

Hajja Maimoon ce da tuni ta manta da abunda yafaru dan har an kwashe mata kayanta an kai mata shago angyara komai kamar yadda taba yaran da zasu riƙa tayata kula da shagon umurni, tana sakkowa daga upstairs cikin wata irin shiga ta alfarma su Suhaila na biye da ita sai ƙamshi suke zubawa kai da ka gansu kasan mutane ne masu alfarma. Fitowar Daddy kawai suke jira su wuce wajen gagarumin bikin data gayyaci kawayenta da mutanen arziki na buɗe katafaren shagon nata data sawa suna 'SUJASU COLLECTION' wanda tuni mutane sun hallara su kaɗai ake jira.

Da ɗan hanzari Dady yafito daga part ɗin nasa yana saƙala agogon hannunsa taƙarasa wajensa ta karɓa ta sanya masa. Zaman hular kansa ta gyara masa ya fito cas abunsa tamkar bai isa aje su Suhaila ba sai wani sheki yakeyi yana zuba nashi ƙamshin. Murmushi ta saki tana cewa.

"Ya Habiby anya zan yarda kaje wajen nan kuwa? Kaga kyan da kayi kuwa?" Side ɗinta ya kalla inda yaransa ke tsaye ta bayanta sun sha kyau suma kafin ya maido kallonsa gareta yace.

"Asalin kyan ai kece kikayi sai wani sheƙi kikeyi Mommyn Jannat." Ya yi maganar yana ɗaga mata gira, hakan yasa ta saki dariya tana gyara sarkarta ta gwal dake wuyanta da mayafinta tace,

"Allah Ya Habiby?" Yace,

"Eh mana muje kinsan mu ake jira." Yayi gaba Jannat ta ruga ta riƙe masa hannu, Hajja Maimoon kuwa ɗakin Jauhar ta leƙa ta ganta kwance, wani mugun takaici ya taso mata tasa ƙafa ta kai mata shuri tana cewa.

"Waya baki izinin zuwa ki kwanta? Tukunna ma wa kike so ya kula da gidan kafin mudawo?" Jauhar da zafin shurin da Hajja Maimoon tayi mata ya shiga jikinta ta tashi zaune tana shafa wajen tace.

"Kiyi haƙuri naga na kammala komai shine na ɗan kwanta." Da wani irin fushi tace da ita,

"Dallah rufamun baki kifice ki zauna daga bakin ƙofa kafin mudawo, kuma karki sake mudawo mu tadda wani abu ya ɓata a gidan nan, idan har haka ta faru sai na lahira ya fiki jin daɗi." Tana kaiwa nan ta juya tafice daga ɗakin. Jauhar tamiƙe a kasalance ta biyo bayanta ta zauna daga bakin ƙofar shiga cikin gidan dan tuni motarsu tafice daga gidan. Baba Bello maigadi ta hango yana kicaniyar rufe gate da a yanzu keyi masa nauyi musamman wajen rufewa duk da kasancewar gate ɗin mai tayu ne da turashi kawai akeyi saboda manyan ta data cin masa. Da gudu ta taso ta dafa masa suka ƙarara rufe gate ɗin tana cewa.

"Sannu Baba Bello." Ya amsa mata da cewa.

"Yawwa Jauhar ba dake aka tafi ba?" Zaro idanuwa tayi tana rufe bakinta haɗe da cewa.

"Baba Bello karufa mani asiri kar Hajiya taji ta datse maka harshe! Ina ni ina zuwa irin wannan taron manya na masu kuɗi?." Murmushi Baba Bello yai haɗe da cewa.

"Jauhar kenan! Ai wannan ba halin Hajiya bane balle ta aikata akaina, kece dai nake mamakin irin takurawa da tsangwamar da takeyi maki, na kuma rasa dalilin da yasa bazata sallameki ba ta sauya wata mai aikin, ko kina yimata wani laifi da bata so ne?" Cikin sauri Jauhar tace,

"A'a Baba Bello ni ko dana tashi wajenta cikin wannan hantarar da takura na ganni, bansan laifin dana yimata ba take tsangwama min haka tun ina ƙanƙanuwata." Ya tausaya mata musamman yadda yaga tana shirin yin kuka yace.

"Kiyita hakuri komai zai wuce in sha Allahu." Ya faɗa cike da tausayinta dan ba wanda bai san kalar ukubar da take fuskanta wajen Hajja Maimoon ɗin ba.

SUJASU COLLECTION

Tunda sukaje wajan ya sake ɗinkewa, manyan mata ne da ƴan gayu masu ji da kansu ta tara. Ganin yadda aka cika dan batayi zaton za'a zo har haka ba, ya sanya taji wani irin girman kai ya sake shigarta. Suka gaggaisa da kaɗan daga cikin bakin kafin cikin isa da tinƙaho Hajja Maimoon ɗin tayi nasarar buɗe katafaren shagon nata da taimakon Alhaji Sha'aban dake gefenta tare da ƴaƴansa, sai kuma Hajiya da Irfaan da Maryam da suma sun samu hallarta wajen taron duk da Hajja Maimoon ɗin bata so hakan ba. Murna aka shiga tayata ana tafi da hannuwa kafin mutane su shiga cikin shagon su zazzagaya suna yaba kyan kayan da aka zuba a ciki da tsadar su, ba abunda ya tafi da zuciyar Alhaji Sha'aban Sada sai yadda ta tsara shagon da kuma sunan data saka mashi wato (SUJASU COLLECTION) dake ɗauke da farkon sunayen 'ƴaƴan nasa wato Suhaila, Jannat da kuma Suhana. Daga ciki kuma kowane ɓangare tayi amfani da sunayen yaran inda ɓangaren takalma da handbags aka rubuta 'Suhana shoe's and bags fashion design'. A ɓangaren jallabiyoyi da mayafai kuma aka rubuta, 'Jannat Italy and Arabian gowns.' Ɓangaren turarukka kuma nan aka sa 'Suhaila perfumes'. Hatta Hajiya wannan abun da Hajja Maimoon tayi ya matuƙar burgeta sosai dan tsakaninta da jikokin nata tasan soyayya takeyi masu ta gaskiya ba cuta ba cutarwa. Hakan yasa nan take tafitar da kuɗi ta sayi wani turare mai kyau da tsada tana cewa.

"Nice zan fara saka albarka a wannan shagon naki Maimunatu Allah ya sanya alkhairi ya buɗa maki kasuwa kuma yasa albarka aciki." Hajja Maimoon tayi dariya cike da makirci ganin Alhaji Sha'aban Sada na tsaye wajen tace,

"A'a Hajiya ai bama karɓi kuɗinki ba duk wannan addu'a da kikayi mana da sanya albarka ai ta ishe mu." Ta ɗauki turaren hadda wani takara ta miƙawa Maryam tace ta riƙewa Hajiyan. A kasan zuciyarta kuwa tsine mata takeyi yafi dubu tana hango asarar da taja mata ta makudan kudaɗen da zata karɓar a turarukkan dan Exclusive turarene na manyan mata da Hajiyoyi. Kamar Alhaji Sha'aban yasan meke ranta yace,

"Nima dai bazan fita ba ban sanya na saka albarka ta ba, saboda haka Maryam keda su Suhana ku shiga ku zaɓo duk abinda kuke so." Duk irin yadda taji yace zai siya, sai da taji har lokacin ranta bai sakko ba na daga kyautar da ta yiwa Hajiya. Kaya suka ɗakko masu kyau da tsada musamman Maryam dan su Suhaila turarukka kawai suka ɗauka, da yake akwai kuɗin komai a rubuce Alhaji Sha'aban baice uffan ba yaje yai making payments duka har na turarukkan da aka sanyawa Hajiyarsa. Haka kuwa akayi Irfaan yaje yayi payment sannan ya cire kudinsa ya zagaya ya ɗakko dogayen riguna guda biyu da hand bag da takalmi ɗaya da turare yaje wajen Hajja Maimoon ya ajiye yana cewa,

"Tunda babu irin namu kayan na maza bari muma musa albarka musayawa kannenmu." Ba kunya Hajja Maimoon tayi dariya ta karɓi kuɗin tana mikawa cikin yaranta ayi payment tare da cewa,

"Thanks Irfaan, haka muke so na gida su riƙa supporting kasuwancin mu." Dan a tsammaninta Maryam ya siyawa kayan. Baice komai ba ya koma gefe har sai da Hajiya tace a maida ita gida

saboda lokacin ɗora abincin sadaka ya yi, duk da akwai masu yi takan bada umarnin yin wasu abubuwan.

Sai da kowa ya watse a shagon sai ɗaiɗaiku masu zuwa sayayya sannan Alhaji Sha'aban Sada ya kwashi yaransa suka wuce gida, haka ma Hajiya dasu Maryam Irfaan ya kasu suka wuce gida. Yana ajiyesu ya juyo ya nufi gidan Yayan nasa da ledar kayan daya siya...

#A heart touching story
#Gonar Sharri..
#Hajja ce
#Billy s Fari
#Ƴan Tagwaye

*ƳAN TAGWAYE BIYAR*

*GONAR SHARRI*
Billy S Fari & Hajja ce

*IDANIYAR RUWA*
(Mai wuyar toshewa)
Ayusher Muhd & Jeeddah Aliyu

*WATA ALAKA*
Zee Bawa & Stylish bch

*BISHIYAR TSIYA*
(Wanda bai jiba bai gani ba ke girbar ki)
Umm Ashgar & Sadiya Dan.

*TSARIN ALLAH*
(Ba mai iya canzawa)
Asmy b Aliyu & Nana Diso

*ZAI IYA BIYAN*
GUDA 1 akan 500
GUDA 2 akan 800
GUDA 3 akan 1200
GUDA 4 akan 1600
GUDA 5 akan 2000

*BANK ACCOUNT*

8098456130
Opay digital services
Shaidar biya
07040402435
08098456130

*KATIN MTN*
07065283730
Shaidar biya ta lambar.
[8/1, 9:34 PM] Billy S Fari: *GONAR SHARRI...!*

*ƳAN TAGWAYE BIYAR*
(Batch C)

NA

*BILLY S FARI*💎
Da
*HAJJA CE*👈
Arewabooks@billysfari

Page 13..

Yana ƙoƙarin tura kan motarsa cikin gidan, yayin da Alhaji Sha'aban Sada na kawowa zai fita campany dan yana ajiye su Suhaila aka kirasa aka ce yayi baƙi masu matukar muhimmanci. Reverse Irfaan ɗin yai har sai da Yayan nashi ya fito zai wuce sukayi clashing Alhaji Sha'aban Sada ya tsaya ya sauke glass ɗin gefensa yana cewa.

"Yauwa Irfaan ka zauna da yaran nan haka baƙi zasu zo yiwa Hajiya Maimoon murna kafin nadawo ba jimawa zanyi ba, bana son barinsu gidan su kaɗai kasan yanayin rayuwar yanzu sai a hankali sam bani da wata natsuwa akan barinsu cikin gidan ba wani babba. Kaga Baba Bello shekaru sun miƙa balle nasa ran babu wata matsala idan na barsu tare." Irfaan dake riƙe da steering motarsa yana sauraren Yayan nasa yace.

"Shikenan Yaya babu damuwa sai ka dawo." Horn Alhaji Sha'aban Sada yai masa alamar amsawa yana maida glass ɗin motarsa ya wuce shi kuma Irfaan ya tura hancin tasa motar ya shiga ciki ya samu waje yayi parking. Tsaye ya yi yana kallon yadda Baba Bello mai gadi keta ƙoƙarin rufe gate ɗin har Allah ya taimake sa ya rufe yana faman sauke numfashi ɗaya bayan ɗaya sai kace wanda yayi wani aikin wahala, dan gate ɗin turoshi kawai za'a yi ya rufe kansa ba tare da ansha wahala ba. Kai Irfaan ya girgiza cike da tausayinshi yana sake fahimtar maganar da Yayan nasa ya gama yimasa yanzu akan tsufan Baba Bellon da yake tunanin sam bazai iya bawa yaransa kulawar data dace ba idan buƙatar hakan ta taso. Har ya nufi cikin gidan sai ya tuna da saƙon daya kawo shi gidan, dan haka ya koma ya buɗe motar ya ɗakko sannan ya

wuce ciki.

Sallama yai abakin ƙofar shiga palourn haɗe dayin tsaye yana kallon Jauhar dake goge-goge, kammala girkinta kenan na dare tafito tana sake gyara gidan dan hakan al'adarta ce kullum safe da maraice sai ta share ko'ina kuma ta goge duk wani abu dake cikin parlorn. Kallo yabi palourn dashi yaga ba kowa sai ita kaɗai dake faman aiki. Wata sallamar ya sakeyi dan da alama bata ji ta farkon ba da yayi tare da ƙarasa shiga cikin palourn ya faɗa kan ɗayar kujerar yana cewa.

"Sannu da aiki Jauhar duk ina yaran gidan ne?" Jauhar da jin muryar sallamarsa tasa ta juyowa riƙe da ƙyallen da take goge-gogen tace,

"Sunu da zuwa Uncle, Ina wuni?" Tayi maganar tana sinne kanta ƙasa cike da jin kunyarsa tunowa da kayan da ya siyo mata kwanaki.

"Lafiya ƙalau Jauhar, kin dai warke ko?" Ta sunkuyar da kai tana faɗin,

"Eh." Tafaɗa tana ajiye ƙyallen da take goge-gogen dashi ta nufi kitchen dan takawo masa ruwa. Dakatar da ita yai yana tashi zaune daga ɗan kishingiɗa da yai a jikin kujerar yace.

"Zo Jauhar ina zaki je?"

"Ruwa zan kawo maka." Ta bashi amsa ba tare data bari sun haɗa idanuwa ba duk da yadda yake kallonta, shi har ga Allah mamakin yadda suke iya cin abincin da Jauhar ke girka masu yakeyi saboda yanayin kayan jikinta da zai iya rantsewa tana kwana bakwai bata wankesu ba balle kuma ayi batun sauyawa. Ya sauke wani nauyayyar numfashi tare da ɗaukar ledar dake gefen ƙafafuwansa yana cewa.

"Zoki karɓa." Ta ɗago kai ta kalli ledar da yake miƙo mata. Ƙofar shigowa palourn ta ƙalla sannan ta girgiza masa kai tana cewa.

"A'a Uncle Mommy kasheni zatayi idan na karɓa, wancan ma.." Sai kuma tayi shiru haɗe da rufe bakinta tana kallon stairs cike da tsoro dan kada ɗaya daga cikin su Suhaila sufito su jita. Haɗe rai Irfaan yai yana kallonta yace.

"Ta karɓe ko?" Bata iya bashi amsa ba ta sake kallon stairs ɗin, ya taso ya iso gabanta yana cewa.

"Karɓi wannan bazata karɓar ba in sha Allah saboda a wajenta na siya miki. Ko da bazaki saka ba kifito kiyi ƙoƙarin sauyawa idan kikayi wanka da kuma idan zakiyi sallah, dan bana tunanin ubangiji na karɓar sallarki acikin wannan shigar Jauhar."

"Ai bana yin sallar ma." Jauhar ta tsinci kanta da faɗar hakan ba tare data sani ba, zaro idanuwa Irfaan yai yana haɗe gira jin abinda ta faɗa.

"Me kikace Jauhar?" Ya faɗa cike da mamaki yana kallonta, sadda kanta tayi ƙasa tana ɗan ja da baya ganin yadda fuskarsa ta sauya dan a tsammaninta zai iya kai mata duka. Jin ya sake jeho mata tambayar rai a ɗan ɓaci yasa tace,

"Bana yin sallah Uncle ban iya ba!."

"Ban gane baki iya ba Jauhar, bakyayi ne saboda wani dalilin ko kowa bakyayi gaba ɗaya." Irfaan yai maganar cikin ɗan sassauta murya ganin yadda take ja da baya saboda ta tsorata da yanayin yadda yakeyi mata magana.

"Ban iya ba Uncle Mommy bata koya mun ba."

"A islamiya fa?" Ya tambayeta with so much shock,

"Ban taɓa zuwa ba." Itama ta bashi amsa cikin sanyin jiki.

"Innalillahi wa'inna ilaihirrajiun, Jauhar bakiga ƙawayenki nayi bane? Ko bakya ganin Mommyn nayi da sauran mutanen da kike rayuwa zagaye dasu? sallah fa Jauhar? Baki san sallah itace cikon  musulunci gaba ɗaya ba?." Irfaan yai maganar cike da tashin hankali da tausayin Jauhar idanuwansa cike da ƙwalla." Ganin haka yasa jikin Jauhar ɗin ya mutu ta duƙa agabansa tana cewa,

"Uncle kayi hakuri Mommy bata bari na, ina kwantata yadda sukeyi, amma dana fara ma zakaji ta kwala min kira, ko ta shigo taga ina yi sai tace, kinibibin banza me na iya banda na dinga daukarwa kaina zunubi. Uncle zan fara yin sallah daga yau, kuma idan an kirani bazan amsa ba sai na gama. Banda ƙawaye shiyasa ban koya daga wajensu ba, Mommy dasu Aunty Suhaila kuma bana fahimtar abinda sukeyi ko sunayi ina gani, na dai san sallah sukeyi kamar yadda naji sunanta abakin mutane." Jiki a sanyaye Irfaan ya kalleta yana cewa.

"Tashi kije idan kin gama aikin kin zan nemeki." Yafaɗa yana sake miƙa mata ledar dan gaba ɗaya kansa ya kulle da jin wannan sabon al-amari acikin rayuwar Jauhar da bai taɓa zato ko tsammani ba, yana bukatar tunani mai zurfi domin nema mata mafita acikin rayuwarta kafin ta lalace. Karɓar ledar Jauhar tayi haɗe dayi masa godiya sannan ta ɗauke ƙyallen da ta gama goge-goge ta wuce ɗakinta saboda ta kammala aikinta gaba ɗaya.

Irfaan kuwa kallo yabi upstairs ɗin da ɗakunan su Suhaila suke dashi yana jin wata irin damuwa a ransa, ya buɗe baki kenan da niyar kiran Suhana ya ji ankira sallar magariba sai kawai yasa kai yafice daga cikin parlorn. Anan bakin fanfon dake laƙe a jikin katangar dake jikin ɗakin Baba Bello mai gadi ya tsaya yai alwala ya shiga Masallacin dake cikin gidan Baba Bello ya jasu jam'i sukayi sallah.

---

Gidan Kawu Ibrahim yana zaune sun idar da sallah yana ta kwararawa Alhaji Sha'aban Sada

addu'a domin ya kasa mantawa da tarin alkairansa. Ayusher ƴah ce tilo a wajan Kawu Ibrahim ɗin, ita kaɗai Allah ya bashi aduniya, suna matuƙar sonta shi da Ummanta irin son da baki bazai iya faɗa ba. Hakan ne kuma yasa ta taso cikin kulawa da gatantawa dai-dai karfinsu, sai dai duk da haka basu bari son da sukeyi mata ya rufe masu idanuwa ba sun kasa bata tarbiyya, kama daga ilimin boko har na Arabia dan tsaye suke akanta tun tana ƙaramar har zuwa yanzu data kammala secondry ta shiga jami'a kuma take kan yin haddarta ta alƙur'ani da yanzu ta haddace hizif arba'in, Ayusher yarinya ce mai natsuwa sosai da kuma alkunya da rashin son hayani, hakan yasa tunda ta taso ba tada wasu ƙawaye in ba ƙawarta Khadija ba da kusan halayensu suka zo ɗaya. Kyakkyawace sosai mai matsakaicin tsawo kuma tana da hasken fata data gado wajen mahaifinta. Sun yi matuƙar shakuwa da Irfaan tun suna ƙanana kafin daga bisani shakuwarsu ta juye takoma soyayya tare da yiwa juna alkawarin aure bayan ta kammala karatunta, wanda sai alokacin suka ɗauki alwashin zasu bayyanawa iyayensu soyayyar dake tsakaninsu dan har yanzu kowa ɗauka yakeyi shakuwa ce kawai. Wannan dalilin yasa kuma Ayusher bata saurarar kowa duk da irin tarin samarin dake kawo mata hari, wasu ma sai dai su biyo ta hanyar mahaifinta idan yayi mata magana sai tace ita karatune gabanta sai ta kammala, da yake mahaifin nata shima yafi bukatar hakan sai kawai ya ƙyaleta ya basu haƙuri. Wannan shine.

---

Bayan su Irfaan sun kammala sallah awaje ya tsaya wajen Baba Bello ya ciro wayar ya kira Ayusher suka sha firarsu da ita har aka kira sallar isha'i sannan ya yi mata sallama ya shiga masallaci sukayi sallah. Yana fitowa ya koma cikin gidan ya tadda yaran gaba ɗaya sun sauko palour sun zauna suna kallo, Jannat kuma na haɗa homework ɗinta da batayi ba.

"Uncle Irfaan Ina wuni." Duk suka faɗa ya amsa masu fuskarsa a sake yana cewa.

"Ɗazu na shigo ban taddaku ba sai Jauhar na samu tana aiki, in ce dai ba baccin yamma kukayi ba." Yafaɗa yana zaunawa kusa da Jannat haɗe da gyara mata wasu errors da har ya hango tayi wajen calculation saboda hankalinta data raba biyu rabi wajen kallo rabi kuma wajen homework ɗin. Suhana ce ta amsa masa da, "Wallahi Uncle wani irin bacci ne ya ɗauke mu da muka dawo mu duka saboda gidan ya zama empty."

"Saboda Momynku bata nan ko?" Irfaan ya faɗa yana kallon suhana

"Exactly Uncle Irfaan wallahi gidan duk ba daɗi." Suhaila dake kwance tafaɗa tana miƙewa zaune da ɗan damuwa ɗauke a fuskarta. Murmushi ya saki haɗe da cewa,

"Ai kuwa sai ku fara sabawa tun yanzu tunda Momynku kuɗi take so."

Muryar Dady ce ta katse firar daya shigo hannunsa riƙe da ledoji. Suhaila ce ta miƙe ta karɓi ledojin hannunsa haɗe da yi masa sannu da zuwa tana ƙwalawa Jauhar kira suma su Suhana da Jannat suka miƙe suna yi masa sannu da dawowa.

"Sannu da dawowa Yaya." Irfaan ya faɗa yana miƙewa saboda dama ɗaya daga cikin shi da

Mommyn yake jira su dawo ya wuce gida.

Daidai lokacin Jauhar data fito wanka tana gwada ɗaya daga cikin rigunan da Irfaan ɗin ya saya mata ta saka har da handbag ɗin da takalmin tana jujjuyawa cike da farin ciki, tana san gayu, tana san abu mai kyau sai dai anyi mata shamaki da samun duk abinda zai sakata farin ciki. Can kuma sai ta jiyo muryar Suhaila na ƙwala mata kira, bata tsaya wata-wata ba ta fito da sauri cikin ruɗewa ba tare data tsaya cire komai ba ta nufo cikin palourn saboda sanin halin Suhaila da tayi har tana gurɗewa tana faɗuwa saboda rashin iya tafiya da takalman da batayi ba. Zaro idanuwa duk sukayi suna kallonta mayafin abayar ya rufe mata fuska sai kiciniyar yadda zata buɗe fuskar tata takeyi gata sagale da jaka. Da kyar ta iya fito da fuskar daga cikin vail ɗin, yadda ta zaro idanuwa tana fiƙifiki dasu haɗe da kallon mutanan wajan tamkar mara gaskiya yasa Suhana ta kwashe da dariya, Irfaan ma murmushi yai yana kallon yadda ta saƙala jakar da takalman kaɗai da ya isa yasa ƙasan bata saba saka irin kayan ba. Jannat data buɗe baki tace.

"Sata kika yiwa Mommy? ba tace bazata baki ba?" Rai aɗan ɓace Irfan yace,

"Wane irin shirme ne haka kike yi Jannat? Ba sata Jauhar tayi ba ni ne na saya mata na kawo mata." Yai maganar saunding so very angry.

"Uncle ka siya mata? Wannan yarinyar zaka siyowa kayan nan? Hmmm!" Suhaila tafaɗa tana taɓe baki cike da takaicin Uncle Irfaan ɗin ta ajiye mata ledojin agabanta ta haye sama abunta. Daddy kam da kallo yabi Jauhar data kwashi ledojin ta wuce kitchen dasu kafin ya maido hankalinsa ga Irfaan yace,

"Har zaka tafi kenan bazaka tsaya kaci abinci ba?" Girgiza kai kawai yai tare da sake kallon gefen kitchen ɗin sannan ya yiwa Yayan nasa sai da safe ya wuce. Ajiyar zuciya Daddy ya sauke ya wuce part ɗinsa, da kansa ya haɗa ruwan wankansa bayan ya rage kayan jikinsa. Sai a lokacin yaji ƙarar shigowar motar Mommy ta dawo. Kai tsaye ɗakinta ta wuce dan agajiye take tafara shiga ta watso ruwa tayi sallar isha'i da batayi ba sannan ta wuce ɗakin su Su haila. Da gudu Jannat ta taso tana yi mata oyoyo tayi hugging ɗinta tana cewa.

"Daughter bakiyi bacci ba? Kinci abinci kuwa?"

"Eh Mommy yau gidan so boring da bakya nan." Jannat tayi maganar tana sake shigewa jikinta tamkar wadda ta daɗe bata ganta ba. Ta bayanta taji Suhaila da Suhana sun rungumota suma suna cewa,

"Welcome home Mommy we missed you." Ta shafo fuskokinsu da hannuwanta atare tana murmushi tace.

"I missed you too yarana, Ina fatan ba wata matsala kunci abinci ko?"

"Eh Mommy." Suka faɗa atare suna breaking hug ɗin tare da komawa kan gadajensu. kayansu da suka zubar a tsakiyar palourn ta shiga tattarawa tana kwashe su takai washing mashin sannan ta dawo tana cewa.

"Oya akwai school gobe kun sani ya kamata ku kwanta da wuri, bari naje gun Dadynku." Taƙarasa zancen tana ficewa tare da ja masu ƙofar. Hajja Maimoon na sakkowa Dady nafitowa dan yunwa yake ji,

"Sorry Ya Habibi wallahi customers suka riƙeni. I can't believe yadda aka samu kasuwa yau daga buɗe shagon nan." Taƙarsa maganar tana janyo masa kujerar dining da suka nufa, murmushi ya saki yana cewa.

"Masha Allah abu yayi kyau Allah yaƙaro kasuwa, ina fatan ba wani abu wurin yayi miki sosai ko?"

"Ai ina faɗa maka wajen nan is extremely good, yau ɗinnan da aka buɗesa har anyi cinaki over 1.5million, gaskiya alhamdulillah mun shiga kasuwar nan da hannun dama." Tayi maganar tare da jawo kujera ta zauna itama, tana kai hannu zata fara saving ɗinsu wayarta tayi ƙara, duba kiran tayi taga wata customer ce da tazo ɗazu sukayi maganar tana son turarukkan ƙamari zata siya, ba shiri ta miƙe tana ƙwalawa Jauhar data soma bacci kira sannan ta ɗaga wayar takai a kunne, da gudu Jauhar da bata san da dawowarta ba ta iso wajen ta zube ƙasa tana cewa.

"Sannu da dawowa Hajiya gani." Ɗan janye wayar tayi daga kunnenta tana cewa.

"Ki zubawa Daddy abinci, Ya Habiby ina zuwa customer ce." Ta wuce abunta zuwa ɗakinta tana ci gaba da wayar ba tare data tsaya saurar abinda zai ce ba. Da kallon mamaki Alhaji Sha'aban Sada ya bita har ta haye sama kafin ya sauke ajiyar zuciya yana kallon Jauhar data ɗauki plate da serving spoon tana cewa.

"Alhaji me zan zuba maka?" Mamaki ne shima a saman fuskarsa, kayan ɗazu ne a jikinta, kalmar Jannat ta dawo masa cikin kwakwalwarsa dan haka yace,
*ƳAN TAGWAYE BIYAR*

*GONAR SHARRI*
Billy S Fari & Hajja ce

*IDANIYAR RUWA*
(Mai wuyar toshewa)
Ayusher Muhd & Jeeddah Aliyu

*WATA ALAƘA*
Zee Bawa & Stylish bch

*BISHIYAR TSIYA*
(Wanda bai jiba bai gani ba ke girbar ki)
Umm Ashgar & Sadiya Dan.

*TSARIN ALLAH*
(Ba mai iya canzawa)
Asmy b Aliyu & Nana Diso

*ZAI IYA BIYAN*
GUDA 1 akan 500
GUDA 2 akan 800
GUDA 3 akan 1200
GUDA 4 akan 1600
GUDA 5 akan 2000

*BANK ACCOUNT*
8098456130
Opay digital services
Shaidar biya
07040402435
08098456130

*KATIN MTN*
07065283730
Shaidar biya ta lambar.

#A heart touching story
#Gonar Sharri..
#Hajja ce
#Billy s Fari
#Ƴan Tagwaye
[8/1, 9:34 PM] Billy S Fari: *GONAR SHARRI...!*

*ƳAN TAGWAYE BIYAR*
(Batch C)

NA

*BILLY S FARI*💎
Da
*HAJJA CE*👈
Arewabooks@billysfari

Page 14..

"Ina kika samu wannan kayan?" Jauhar tayi saurin kallon jikinta, bata kalli fuskar Alhaji Sha'aban ɗin ba dan sai take ganin kamar shima bai yadda cewa Uncle Irfaan ne ya bata ba tunda ai a gabansa Irfaan ɗin ya faɗi cewa shine ya kawo mata. Jin tayi shiru yasa yaji kamar tambayar ce bata fahimta ba, yadda jikinta yake rawa yasa tausayin ta ya kama shi, plate ɗin da ta ɗakko zata zuba masa ya janyo tare da cewa.

"Barshi Jauhar jeki kwanta." Ganin yana ƙoƙarin zubawa da kanshi yasa tayi saurin durƙushewa a gabansa tana sake waigawa ta kalli hanyar da Hajja Maimoon tabi, bakinta yana kyarma take masa magiya.

"Kayi haƙuri Alhaji wallahi Uncle Irfaan ya bani kayan ɗazu, sannan dan Allah ka kawo na zuba kar Hajiya taga bani na zuba ma ba." Karo na babu adadi da tausayin yadda yaga duk ta firgice ya dirar masa cikin zuciya. Cike da nutsuwa irin tasa da Allah ya wadata shi da ita yake girgiza kai yana faɗin.

"Irfaan ya kyauta sosai, sannan karki damu dan na zuba da kaina ai ni nace ki barshi. Oya koma ɗakin ki kiyi kwanciyarki dare ya yi, kinci abinci dai ko?" Ya tambayeta cike da son gyara kulawarsa da baya bata a da har sai da aka lurar dashi. Cike da mamakin yanayin da ya yi furucin Jauhar ta kalleshi. A cikin jikinsa yaji cewa kallansa ake domin da ya tambayeta sai kawai ya maida hankalinsa wajan zuba abinda yake da buƙata. Kallansa ya mayar saitin inda yake jin idon a jikinsa, yadda yaga Jauhar ɗin tana ware ido yasa shi saurin yin magana.

"Ya akai?" Ta sauke ido dan bata iya kallansa saboda yana da mugun kwarjini. Muryarta tana rawa tace.

"Alhaji naci."

"Masha Allah toh kije kiyi kwanciyarki Allah ya huta gajiya Allah yai miki albarka." Jauhar ta durkusa tana amsawa dan ba ƙaramin daɗi addu'ar tashi tayi mata ba, shine mutumin da yake yi mata wannan daddaɗar addu'a sai kuma idan Hajiya tazo wacce idan ba wani babban abu bane ya faru a gidan bata cika zuwa cikinsa ba. Ɗaki ta koma tana shiga kwanciya tayi akan carpet ɗin dake shimfiɗe a ciki wanda shine ya zamar mata kamar katifa da take kwanciya tayi bacci. Sai da ya kusan kammalawa Hajja Maimoon ta karaso inda yake tana jan kujera ta zauna. Dube-dube ta shiga yi ko zata hango Jauhar amma ba ita ba labarin ta. Kira ta shiga kwala mata Alhaji Sha'aban ya dakatar da ita.

"Me kuma zatayi?" Mamakin tambayar tashi tasa Hajja Maimoon kallon cikin idanunsa.

"Idan abinci za'a zuba miki madam kina dani a kusa meye na kiran yarinya?" Nan da nan farin ciki ya kamata tayi ƙasa da kanta cike da nuna kunya tana janyo boul, karɓa yayi da kansa ya

zuba mata fresh milk ɗin a ciki sannan ya zuba mata cornflakes ɗin cikin extra boul dan ya lura shi tafi bukata a gurin. Suna ci suna hira har ta kammala suka mike zasu wuce ɗaki ta shiga kwalawa Jauhar kira dan tazo ta gyara wajan. Alhaji Sha'aban yana riƙe da hannunta yace,

"Me zatayi?"

"Ya Habiby tazo ta kwashe kayan ta gyara wajen ko?"

"Ki bari idan Allah ya tashe mu gobe sai tayi mana abinda tana nan ba wani guri zata je ba." Ɓata rai tayi tace,

"Yanzu Ya Habiby haka za'a bar gurin nan har sai da safe? Haba Ya Habiby sai kace gidan ƙazama? Tana nan fa meye amfaninta a gidan nan?" Ya ɗan sanyaya murya yana janyota cikin jikinsa dan harga Allah baya son a taso yarinyar nan yanzu tunda har shine yace taje ta kwanta. Hajja Maimoon kuwa ta sake haɗe rai dan tunda taga yana wani matseta cikin jikinsa tasan lallaɓata zaiyi ta haƙura tabar Jauhar zuwa safiya, ita kuma tana jin tamkar idan ta barta zuciyarta ƙonewa zatayi dan bata farin ciki idan taga Jauhar na hutawa ko tana samun walwala a gidan.

"Pls.. Nasan gobe tana idar da sallar asubahi zata fito ta gyara, yanzu dai kam kiyi hakuri ki kyaleta." Ganin da gaske hanawa zai yi sai kawai ta zare hannunta daga cikin nasa ta janye jikinta fuskar nan tata a matukar haɗe tace.

"Gaskiya Ya Habiby idan har na bar yarinyar nan bata gyara gurin nan ba shikenan haka zata dawo kazanta sai wacce batayi niyar yi ba. Kabar ni da ita kawai Allah sai tayi aikin nan." Kallon yadda ta kafe tana yi masa gaddama yake ya ji abun yai matukar ɓata masa rai, a tunaninsa duk abinda yace mata ya kamata ta dinga yi babu jayayya koda ranta baya so kamar yadda shima yake hakura da wasu abubuwan koda ba dai-dai bane dan gujewa ɓaci ransa, amma ya lura sam bata tunanin hakan, takan yi masa kafiya musamman idan abun ya shafi Jauhar takan nuna masa bai isa ba itace wacce take da iko da ita. Ransa a ɗan ɓace da yake ba saba bari ya yi ɓacin rai ya yi tasiri a zuciyarsa ba ya sauke nauyayyen numfashi yana ambaton Allah abakinsa. kallanta da idanunsa yai cike da san nuna matsayinsa na mijinta agareta yake cewa.

"Me kike nufi kenan? ban isa nace ga abinda za'a yi ba kiyi ne ko?" Cikin rashin nuna damuwa da sauyawar da fuskarsa tayi Hajja Maimoon ta kawar da fuska tana sake haɗe rai.

"Kizo ki wuce muje bana san kuma yin magana akan wannan." Zuciyar Hajja Maimoon ta shiga yin zafi tana wani irin tururi ji takeyi tamkar ana ƙara garwashi. Idan har Jauhar tayi kwanan farin ciki a gidan nan tabbas ba sunanta Maimuna ba dan kuwa abu ne da bazai yiwu ba indai har tana cikin gidan. Yayi taku biyu yaji alamar bata biyo shi ba, hakan yasa shi juyowa ya ganta tsaye ta kafe idanunta akan ɗakin da Jauhar ke ciki hannayenta naɗe a ƙirji. Ransa ya sake ɓaci ya hango tsantsar raina shi da Maimoon tayi wanda besan ya kai har haka ba.

"Ya yi kyau." Haka kawai Alhaji Sha'aban Sada ya faɗa kawai ya wuce bai bi ta kanta ba.

Ganin ya wuce ita kuma ta nufi ɗakin Jauhar ba tare data fasa yin abinda zuciyarta take umartar ta ba. Tana shiga ta tarar da Jauhar ɗin kwance ta saki baki tana ta sharara bacci dan tun lokacin da Alhaji Sha'aban ya umarce ta da taje ta kwanta tana shiga ɗakin kwanciya tayi dan ba ƙaramin bacci ne ke damunta ba, dalilin da yasa ko kiran Hajja Maimoon bata jiyo ba duk kuwa da cewa ko bacci takeyi sai ta dinga jin kiran matar nan. Kallanta kawai Hajja Maimoon keyi cike da tsabar mamaki, abubuwa da yawa suka sanyata ta yi cak wajan kasa tashin Jauhar ɗin. Kayan jikinta, da kuma yadda take ta sauke minshari da alama baccin ya yi masifar yi mata daɗi. Toilet ɗin cikin ɗakin ta shiga da niyar ɗebe ruwa ta watsa mata wani irin hamami ya doki hancin Hajja Maimoon tayo baya tana jin tamkar zatayi amai. Cikin sauri ta fito daga ɗakin, kai tsaye ta nufi kitchen ta buɗe fridge. Ruwa ta ciro gora guda a freezer ta juye shi cikin wata roba ta sake ɗakko wani ta juyo sannan ta nufi ɗakin Jauhar kamar zata tashi sama dan sauri. Tana zuwa ta saita robar a saitin fuskar Jauhar kawai ta sheƙa mata ruwan sanyin nan duka.

"Wayyo Allah na na shiga uku na lalace." Jauhar ta faɗa a gigice tana mikewa tare da kai hannu tana neman abinda zai ceceta. Kafin ta gama dawowa daga cikin tashin hankalin data shiga ciki ne taji an shaƙota ana jijjigawa, Jauhar ta dinga ihu tana neman taimako can taji Hajja Maimoon ɗin na cewa.

"Ai dama nace ke kika ɗauke zinariya ta munafuka kika siyar, idan ba haka ba a gidan uban waye kika samu kudin siyar rigar nan?" Jin tambayar da takeyi mata ne yasa Jauhar da kyar ta iya janyo kalamai dan har lokacin Hajja Maimoon bata sakar mata wuyan ba tace.

"Uncle Ir.. Ir.. Faan.. ne.. Ya bani."

"Ohhhh! Irfaan ne ya sake siya miki ko? Dama kayan da ya siya a shago na munafikin ke ya siyawa da kuɗin zinariyata da kika bashi ya sayar?" Kai Jauhar ta shiga girgizawa alamun a'a dan har lokacin Hajja Maimoon bata iya sakinta ba. " Idan basu bane Jauhar to ki gaya min uban me kike yiwa yaron can yake yi miki wannan hidimar ko kuma nayi takakkiya muje wajan su Baffa wallahi ayi min iyaka dake dan ba zakisa bakin tarihin abun kunyar da ubanki ya yi ba ya maimatu acikin gidana ba. Dole ki gaya min uban me yake miki har yake jin daɗi yana siyo miki kayan da ni zan iya sakawa ko kuma su Jannat?" Tana kaiwa nan ta saketa tana jiran jin abinda Jauhar ɗin zata faɗa. Ita kuma banda tari babu abinda takeyi saboda wuyan ta da take jin kamar numfashinta zai tsaya. Gefe guda kuma kalaman Hajja Maimoon ne yake mata yawo na cewa zata kaita wajan su Baffa, toh kodai tace itace ta ɗauka? Tayi amfani da damar a kaita wajan su tace ba zata biyo ta ba shikenan ta kubuta daga hannun jarababbiyar matar nan.

"Zaki gaya min ko sai na kasheki a cikin ɗakin nan?" Hajja Maimoon ta faɗa cikin tsawa.

"Hajiya wallahi... Wallahi shine... Shine.. Ya..." Cikin zaro ido tun kafin Jauhar ɗin ta ƙarasa yin magana tace.

"Ya yi me?" A gigice Jauhar tace,

"Ya bani."

"Ohhh! kina nufin dai ba kudin zinari na ne da kika bashi ba?"

"Eh wallahi Hajiya ban ɗauka miki ba na rantse da Allah." Hannu takai ta fizgo Jauhar da karfi ta haɗe da jikin ginin dakin tana cewa.

"Toh taɓa miki jiki yakeyi ko?" Jauhar taji maganar a wani iri, cikin sauri tace.

"A'a Hajiya."

"Zaki gaya min ko sai na yankaki dan ubanki?"

"Wallahi Hajiya kinji na rantse miki Alkur'an baya taɓa ni, kawai yana bani kayan yake tafiya wallahi gaskiya nake gaya miki." Jin hakan yasa Hajja Maimoon ta taso ƙeyarta suka fito daga ɗakin tana cewa.

"Toh idan ma kin bari yana miki wani abun ke kika sani ba damuwata bace wallahi, sannan kina gama gyara wajan nan kije ki cire kayan nan ki ajiye min su zanzo na ɗauka ai ba kalarki bace ba dan sunfi karfin ubanki ma bare kuma ke banza a banza."

Ta ƙarasa maganar tana tura ta wajan dining area ɗin da karfi sannan ta wuce ɗakinta tana sakin tsaki da ƙarfi. Jauhar kuwa tana hawaye dafe da ƙasa dan turewar da aka yi mata sai da ya kaita ƙasan taels sauran kaɗan ta fasa goshi. Tana kuka tana kwashe kayan takai kitchen, ta rasa me yasa Hajja Maimoon ta zaɓi yin rayuwa da ita tun ƙanƙanuwa dan ta bautar da ita bisa wasu dalilai nata da batasan koma meye ba.

Tsab ta gyara gurin tayi wanke-wanke ta ajiye komai inda ya dace sannan ta koma ɗakin ta. Jikinta ta kalla yadda rigar ta amsheta duk da cewar ta ɗan yi mata yawa amma ba wani sosai ba. Kuka taji yazo mata ganin an rabata dasu akaro na biyu. kenan ba damar ta saka ɗayar rigar wacce ke cikin ledar duk da yadda ta burgeta! kenan har handbag ɗin da takalman duka Shikenan an rabata dasu? Bata san lokacin da ta durƙushe a kan carpet ɗin baccinta tare da fashewa da wani kukan mai bala'in taɓa zuciya.

---

Hajja Maimoon kuwa tana komawa ɗaki wardrobe ta nufa ta shiga nemo kayan da zata saka. Wata orange ɗin sleeping dress ta janyo sabuwa dal bata daɗe da siyan su ba, ta feshe su da turaruka masu masifar ƙamshi sannan ta zare kayan jikinta tasa na baccin. Wajan mirror ta nufa tana kallan fuskarta ta saki murmushi tuna shirin da tayiwa Habibyn nata na nuna godiya abisa farin cikin da ya sanyata. Idan ta tuna cinikin da tayi a yau kaɗai sai taji wani irin farin ciki yana mamaye ta. Jan baki ta goga tabi jikin mata da khumras masu daɗi sannan ta fito ta nufi ɗakin Alhaji Sha'aban Sada. Cike da nutsuwa tasa hannu akan handle ɗin ta murɗa ta shiga. Kwance

ta hango shi sai dai tasha mamaki ganin ko kallan ƙofar baiyi ba bare tasa ran zai miƙo mata hannunsa kamar yadda yake yi mata idan tazo.

Kan bed ɗin ta nufa ta hau still bai ko kalleta ba bare ya nuna yasan tazo ba. Mamaki ya kamata ta kwanta sai taga ya juya mata baya. Shi kuwa ransa ne ya ɓaci ganin yace tayi abu taki duk da cewa ba wai yau ne na farko ba, sai dai yau abin yafi bashi haushi saboda yana ganin kamar so takeyi ta nuna masa tafi karfinsa bai isa da gidansa ba. Kasa yi masa magana tayi dan tana jin wata irin izzah gani take idan har itama ta kulashi to ta ɓarar da ajinta matsayin ta na ƴa mace. Shi kuma kamar jira yake dama ta shigo kawai bacci ya ɗauke shi ya barta cike da masifaffan mamaki. Keyarsa kawai ta zubawa ido tama rasa uban me takeyi a wajan, ga wata irin kulawa da take buƙatar ya bata bawai na kwanciyar aure ba, a'a tana buƙatar ya rungumeta yana bata labari ko kuma nuna mata yadda take da muhimmanci a rayuwarsa kamar yadda ya saba akoda yaushe, hakan zai bata damar sake yimasa godiya da nuna masa jin dadin abinda ya yi mata yau na sake ɗaga darajarta acikin yan uwanta mata.

"Kenan hakan bazai faru ba?" Ta tambayi kanta.

"To me nayi masa?" Ta sake jefa ma kanta tambaya a karo na biyu tana jin zuciyarta tamkar ta fashe Dan tsabar takaici.

"Akan maganar ɗazu ta Jauhar shine yayi fushi dake." Taji zuciyarta tana sanar da ita. Cije lips tayi tana sake jin wani irin zafin Jauhar, lallai ma akanta ne mijinta yau ya juya mata baya? Allah ya kaimu gobe mai raba ni da ita sai Allah, Hajja Maimoon tafaɗa cikin zuciya tana juya kwanciyarta tare da kashe fitilar dakin ta kunna masu bed lamp...

#A heart touching story
#Gonar Sharri
#Billy s Fari
#Hajja ce
#Ƴan Tagwaye

*ƳAN TAGWAYE BIYAR*

*GONAR SHARRI*
Billy S Fari & Hajja ce

*IDANIYAR RUWA*
(Mai wuyar toshewa)
Ayusher Muhd & Jeeddah Aliyu

*WATA ALAƘA*
Zee Bawa & Stylish bch

*BISHIYAR TSIYA*
(Wanda bai jiba bai gani ba ke girbar ki)
Umm Ashgar & Sadiya Dan.

*TSARIN ALLAH*
(Ba mai iya canzawa)
Asmy b Aliyu & Nana Diso

*ZAI IYA BIYAN*
GUDA 1 akan 500
GUDA 2 akan 800
GUDA 3 akan 1200
GUDA 4 akan 1600
GUDA 5 akan 2000

*BANK ACCOUNT*
8098456130
Opay digital services
Shaidar biya
07040402435
08098456130

*KATIN MTN*
07065283730
Shaidar biya ta lambar.
[8/1, 9:34 PM] Billy S Fari: *GONAR SHARRI...!*

*ƳAN TAGWAYE BIYAR*
(Batch C)

NA

*BILLY S FARI*💎
Da
*HAJJA CE*👈
Arewabook@billysfari

Page 15..

Gabaki ɗaya bacci ya kauracewa Hajja Maimoon, yadda Ya Habiby ɗinta yai iskar kare da ita yafi komai bata haushi. Sai kusan tsakiyar dare ta samu da kyar tayi baccin shima cike da mafarkan Alhaji Sha'aban ɗin wai tana masa magana yana shareta, sanin wacece ita da take jin

duk duniya babu ɗa namiji da ya isa ya juya ta saboda tana ji da kyau tana kuma alfahari da wayewar da take da ita yasa ta basar bata ɗauki mafarkin abakin komai ba. Koda aka kira assalatu yasha mamaki da yaga still tana cikin ɗakin dan bai yi tsammanin kwananta a tare dashi ba duk da sanin muhimmancin da take bashi wasu lokutan. Toilet ya shiga yayo alwala, praymat ya shimfiɗa yayi nafila sannan ya zauna yaci gaba da tasbihi har aka kira asubahi ya fita zuwa masallaci. Yana dawowa har zai wuce sashensa yaji kamar shesshekar kuka. Dama da zai fita yaji hakan sai ya dauka kawai kunnensa ne. Ta inda yake jiyo alamun kukan ya dinga bi, ga mamakinsa sai yaga yana nufar ɗakin Jauhar. Da yake ba rufewa takeyi ba hakan ya bashi damar ɗaga labulen ya leƙa idanunsa suka sauka akanta tana ta kuka.

"Subahanallahi Jauhar lafiya?" Ya tambaya yana kallonta bayan ya ƙarasa ciki. Kamar wacce take jiran a kulata kawai ta sake sakin wani kukan gabaki ɗaya.

"Meyake damunki?"

"Wajan Babana nake so." Tausayinta ya sake kamashi, yana sake kallanta yake faɗin.

"Zanso hakan ta kasance Jauhar, shin kinsan gidan Baban naki?" Ta girgiza masa kai a hankali tamkar wata marar laka a jiki.

"Toh yanzu ya kenan tunda baki sani ba? Kiyi hakuri kinji zuwa gari ya waye sai muji yadda za'a yi."

"Za'a yi me Alhaji?" Sukaji muryar Hajja Maimoon daga bayansu tsaye tafaɗa cikin isa da gadara. Jauhar da tun shigowarsa tayi masa kallo ɗaya ta maida kanta cikin ƙafafuwanta tana jin muryar Hajja Maimoon bata san lokacin da ta ganta a tsaye ba. Rawa jikinta ya hau yi tana neman ɓoyewa a bayansa. Cike da dakewa yace,

"Gidan iyayenta zata koma, in sha Allah gobe zan bada kuɗin mai a maida ita in yaso ma samu wata mai aikin." Wani malalacin kallo Maimoon ta sakarwa Jauhar ɗin. A fili kuma taja numfashi tare da yin taku uku tana naɗe hannayenta a ƙirji take cewa

"Ka tambayeta tasansu ko tasan inda suke? Duk wani abu da kake gani ina yimata wallahi gatanta ta nakeyi akansu, dan haka kayi haƙuri Alhaji babu inda Jauhar zataje dan bata da gurin zuwa wanda za'a riƙe ta kamar yadda nakeyi mata. Idan kuma tasan ina zata samu gidan uban nata sai ta faɗa maka." Hajja Maimoon taƙare zancen tana kafewasa da idanuwa. Ganin ya ɗauke idanuwansa ya mayar akan Jauhar ya sata sakin wani malalacin murmushi kafin ta haɗe fuska tana kallon Jauhar ɗin tace,

"Bari kiji in gaya miki Jauhar, zamanki tare da ni shine rufin asirinki dan Uban naki da kike kira ɗan iska ne, ɗan shaye-shaye ne kuma mahaukaci da bashi da wata daraja, shi yasa ma ba wanda yasan duniyar da ya shiga ya janyo ƙaddara ta tilasta ni rayuwa dake waje ɗaya. Dan haka ni ɗin da kika raina nice rufin asirinki kuma mafi girman matsayi tunda har na amince na

riƙe ki tun yarintarki har girmanki."

"Amma kuma ina mahaifiyarta take? Sai a kai mata ita in har shi ba'a san inda yake ba." Alhaji Sha'aban Sada ya tambaya dan yafi son yaga yarinyar tabar gidan ta samu inda za'a kula da ita.

"Ta mutu." Hajja Maimoon ta faɗa babu alamar tausayawa. Jauhar najin haka ta fashe da kuka tana faɗin.

"Wayyo Allah wayyo Mommy na shiga uku zan mutu wayyo Allah...." Jauhar ta faɗa tana faɗuwa ƙasa ta shiga yin birgima kamar wata ƴar goye. Ganin hakan yasake ƙular da Maimoon ta nufeta zata janyota yai saurin tarewa yana masifa.

"Meye haka ne Maimoon?!" Jin kalar tsawar da yai mata sai da ta firgita, kallansa take kamar idanunta zasu fita taji yace.

"Karki kuskura ki doketa ina wajan nan, yarinyar nan ko jaka ce kika siyo a kasuwa ya dace ki kyautata mata, ballantana kuma amana ce ita a gurinki bai dace kina treeting nata haka ba."

Tsabar gaskiyar da ta yiwa Hajja Maimoon yawa juyawa kawai tayi fuuu..ta bar wajen, dan a wannan gaɓar ta tabbatar idan tace zata buɗe baki tayi magana to baza tayi masu daɗi ba. Ɗakinta ta wuce kai tsaye tana mai nadamar rikon Jauhar a hannunta gashi tana nema ta haddasa fitina tsakaninta da mijinta, farin cikin ta, mai share mata hawayenta. Alhaji Sha'aban kuwa duƙawa yai saitin fuskar Jauhar cikin sigar rarrashi yake yi mata magana.

"Ya isa haka kiyi shiru, in Sha Allahu zaki koma gun iyayenki kiyi shiru haka kada kanki yai ciwo kin ji ko?" Yaƙare maganar yana ƙoƙarin kai hannunsa ya goge mata hawayen da suka jiƙa mata fuska. Saurin miƙewa tayi zaune da kanta tana share hawayen tace.

"Nagode Alhaji." Sai alokacin ya fahimci me yake ƙoƙarin yi ya damƙe hannunsa tare da miƙewa tsaye yana sauke ajiyar zuciya sannan ya juya yabar ɗakin. Jiki ba ƙwari Jauhar itaka tamiƙe ta nufi kitchen wajen haɗa breakfast dan kar wani bala'in Hajja Maimoon ɗin ya sake hawa kanta. Shigarta kitchen keda wuya ta isko Suhana aciki har ta ɗora ruwan zafi tana fere Irish taji wani tashin hankali ya sake ziyarto ta, da sauri taƙarasa cikin kitchen ɗin hannunta na kakkarwa take cewa.

"Dan Allah kiyi haƙuri Aunty Suhana ki kawo na ƙarasa aikin nan kar Mommy tafito ta sameki." Suhana ta juyo tana kallonta murmushi ɗauke akan fuskarta tace,

"Ba abinda zai faru ki bari naci gaba kije kiyi sallah idan kin fito sai mu ƙarasa tare." Tsaye Jauhar tayi takasa motsawa dan ita kam ƙara ta ƙarasa girkin nan da taje yin wata sallah tunda ba iyawa tayi ba, bata ma san muhimmancinta bare tasan wajibi ce a kanta ko ba wajibi bane, burinta kawai kar ta jawowa kanta duka a banza.

"Jauhar me kike tunani?" Suhana ta tambaya. Jin shiru yasa ta ce.

"Dake fa nake magana." Suhana ta faɗa tana ɗan taɓa ta ganin ko motsawa batayi daga inda take ba. Karkace kai Jauhar tayi kamar zatayi kuka haɗe da cewa,

"Ni dai kibarni kawai nayi ya fimun yin sallar nan Aunty Suhana." Zaro idanuwa Suhana tayi kafin tace.

"Wal'iya zubillah! Jauhar akwai abunda yafi sallah aduniyar nan dama? Ashe da gaskiyar Uncle Irfaan daya faɗa mani cewa bakya sallah?" Suhana ta tsureta da idanuwa tana neman sake tabbatar da zancen uncle ɗin nata daya kirata a waya jiya ya sanar da ita cewa Jauhar bata yin sallah tace bata iya ba, dan haka tayi ƙoƙari ta taimaka mata tasan meye sallah dama yadda akeyinta kafin ya yi tunani wane irin taimako zai bata ta wannan ɓangaren. Kai Jauhar ta shiga sosawa cike da tsoro tace,

"Aunty Suhana akwai aikin da yafi na Hajiya? Ku aikin ku zuwa makaranta, bakiga yadda kuke sauri ba idan kuna da jarababben malami?" Tsoro da mamaki ya kama Suhana jin kalaman Jauhar. Ganin yadda Suhana take kallonta yasa Jauhar saurin juyawa ta nufi wajan kettle dan taga alamar Suhana ba zata fahimci abinda take nufi ba.

"Jauhar bakiga yadda muke sallah ba?" Tace,

"Ina gani wata ran."

"Amma ya akai kika ce bakya yi." Jauhar da sanyin jiki tace,

"Toh Hajiya bata sani ba, tace kuma idan ba itace tayi abu ba nayi sai ta kasheni."

"Ai kuwa dole kiyi sallah Jauhar." Cewar Suhana cikin takaici. Jin yadda Suhana tayi furucicin a kaurare yasa Jauhar tsorata dan haka tace,

"Toh bari naje nayi sallar sai na dawo".

"Ya zakiyi idan kin je?" Suhana tafaɗa tana maida hankalinta ga fere Irish ɗin da takeyi amma kunnuwanta na wajen Jauhar ɗin tana sauraren amsar da zata bata.

"Zan sa hijabi na sai na tsaya na duka na zauna nasa goshina akasa sai na sallame". Dariya ce ta kusan kwacewa Suhana jin bayanin sallar Jauhar, amma sanin da tayi ba zancen da za'a ɗauka da wasa bane yasa ta juyo tana ɗan haɗe rai tace.

"Jauhar ba haka ake yin sallah ba, kije ki samu ruwa mai kyau ki fara zuwa kiyi tsarki sannan sai kiyi alwala, kin iya alwala ai ko?" Jauhar ta girgiza mata kai alamun a'a, iska Suhana ta

furzar ta baki kafin taci gaba da cewa.

"Akwai aiki kenan gaban mu." Sannan ta juya ta tsame irish ɗin daga cikin ruwa ta ja hannun Jauhar suka nufi toilet ɗin ɗakinta, ganin yanayin toilet din yasa ta dawo baya tana cewa.

"Muje ta can baya." Ta nufi bayan kitchen da yake akwai fanfo a wajen, cikin tsanake ta fara nunawa Jauhar yadda ake alwala tana yimata bayani a saukake yadda kwakwalwar ta zata iya dauka. Bayan ta kammala tace tazo tayi itama ba laifi tayi sai dai akwai ƴan gyare-gyaren da tayi mata. Daga nan ta tambayeta sau nawa ake dungurawa dan tasan dungure taga sunayi. Nan Suhana ta gaya mata sallar asuba raka'a biyu ce saboda taga anayi sai dai bata tabbatar da kowacce adadi nawa ake yi ba.

Sai da tayi mata bayani a gurguje saboda har karfe shida tayi sannan ta koma kitchen ta barta tayi sallar. Ba'a jima ba Jauhar ta dawo har ta kammala tare da gaida Suhana ɗin ta amsa mata da lafiya ƙalau sannan ta kama mata aikin sukaci gaba tana yi tana tambayarta wasu abubuwan da suka shafi ibadarta da kuma addini. A nan Suhana ta tabbatar da bayan rayuwar talauci da Jauhar ke ciki har da jahilci na damunta sosai, dan bata san komai ba a ɓangaren addini balle kuma boko.

Ƙarfe bakwai na bugawa sun kammala komai. Lokacin Hajja Maimoon ta sauko tana waya cikin wata ƙawatacciyar doguwar riga ta yane kanta da mayafinta fuskarta ɗauke da wani ƙaton parado daya rufe kusan rabin fuskarta, kasancewarta farar mace kyakkyawa ajin farko yasa tafito tamkar wata balarabiya dan tayi matuƙar kyau sosai. Suhaila da Jannat ne bayanta cikin shirin su na zuwa school Jannat na riƙe da school bag ɗinta. Yadda fuskarta take a ɗaure ba wasa yasa tayi masu kwarjinin da bayan gaisuwa babu wacce ta iya cewa komai har sai da ta kalli Jannat tace.

"Call your Dady kifaɗa masa breakfast is ready?" Dama haka takeyi idan sun samu misunderstanding tsakaninsu komai sai dai ta aika yaran, Alhaji Sha'aban dake zaune yana aiki da system ɗinsa yaji anyi masa knocking, tambayawa yai Jannat tace itace tare da faɗin sakon Mommyn tasu. Wani takaici ya taso mashi dan ba tun yau ba yasha faɗa mata tadena saka mashi yaransa cikin faɗansu idan suna yi.

"Kice ina kiranta." Shine amsar daya bawa Jannat taje ta sanar da ita cewa Daddy na kiranta. Ba dan ranta yaso ba ta mike ta nufi ɗakin. Da kallo ya bita ganinta cikin shiri da irin kwalliyar data chaɓa. Danne ɓacin ran dake cikin zuciyarsa yayi kafin yace.

"Wannan ya zama last warning tsakanina dake da zaki kuma turo yarana kirana, idan har kina jin faduwa ce wajenki kizo kiyi min magana saboda mun samu matsala to ko meye kibarsa bana buƙata". Hajja Maimoon bata ce komai ba har ya dasa aya. Ganin sosai ransa ya ɓaci yasa ta ɗan sassauta fushinta haɗe da cewa.

"Am sorry." A takaice tana dauke kai gefe, ba tare daya kalleta ba ya maida hankalinsa ga

system ɗin dake gabansa yana cewa.

"Ki hada mani ruwan wanka." Da sauri ta ce,

"Time is going Ya Habiby, bana so yarana suyi late kuma customer na jirana a shago zan basu kaya asa a mota delivery ne to Abuja, gashi to 8 kuma tun 6:30 suke jirana, zan turo Jauhar ta haɗa maka duk abinda kake buƙata ta kuma gyara maka ɗakin, breakfast ɗinka kuma yana dining." Ta kare zancen haɗe da juyawa ta fice daga ɗakin. Da kallo ya bita dan duk a zatonsa wasa takeyi, bai sha mamaki ba sai da yaji sallamar Jauhar a bakin kofar palournsa.

"What?" Yafaɗa da ɗan karfi yana miƙewa tare da zuro jalabiyarsa ya nufi palourn.

"Alhaji ina kwana?" Jauhar tafaɗa tana ɗan russunawa, idanuwansa akanta yana kallon yadda take ɗari-ɗari dashi, da alama bisa dole tazo ɗakin don bata taɓa takawa ko gefen da part ɗin nasa yake ba. Sake binta ya yi da kallo ya ganta da kayan nan na gado, eh na gado mana dan ko ɓata tayi sai mutane su gano ta saboda tsabar tafi sanya su. Kamar ya yi shiru sai kuma yace.

"Me yasa kika cire doguwar rigar da Irfaan ya siya miki?" Kirjin Jauhar ya buga, zuciyarta ta karye saboda ita kanta bata son ana tuna mata kayan saboda tana ganin samu sannan taga rashi duk a guri guda.

"Hajiya ta kwace su." Dafe goshi ya yi yana jin takaici, besan me Maimoon take ji ba idan tana ganin Jauhar a haka. Cikin danne fushinsa da yake sake nuna ɓacin ransa akan Maimoon ɗin yake yace,

"Ya akayi?" Ya tambayeta yana tsare ta da kyawawan idanunsa da suka koma kalar ɓacin rai,

"Hajiya ce tace nazo na gyara maka sashenka kuma na haɗa maka ruwan wan.." Tun kafin taƙarasa ya dakatar da ita yana runtse idanuwa, abinda ya gujewa kenan shi yasa bai amince da buɗewa Hajja Maimoon shago ba amma ta nuna masa ai ba wata matsala, gashi tun ba'a je ko'ina ba komai na shirin sauyawa tsakaninsu.

"Kije kawai Jauhar, ina ita Hajiyar?"

"Sun fita."

"OKay Kije nagode." Alhaji Sha'aban yafaɗa tare da juyawa ya koma ciki. Zauniya yayi saman gadonsa ya dafe kansa cike da mamakin Hajja Maimoon dako a mafarki aka ce masa zata aikata hakan bazai yarda ba...

---

Kimanin awanni biyu cif suka ɗaukesa kafin ya kammala duk wani shiri nasa har lokacin

mamakin Hajja Maimoon na cike a zuciyarsa. Abinci ma ko da ya fito ya samu Jauhar tsaye gefen dining table tamkar wata soja tana jiran ƙarasowarsa kamar yadda Hajja Maimoon ɗin ta gargaɗeta, kasa zaunawa ya yi yaci, kallo ɗaya yaiwa gefen da Jauhar ɗin take ya ɗauke kai ya miƙi hanyar ficewa daga cikin palourn, cike da tashin hankali Jauhar da taga haka ta rugo ƙiris kaɗan ta bangajesa ta sha gabansa tana haɗe hannayenta tamkar mai riƙon gafara take cewa.

"Alhaji ga abincin karin kumallonka can Hajiya ta haɗa maka duk abinda zaka buƙata, ta kuma umurce ni dana tabbatar kaci kafin kafita bata son ka zauna da yunwa, dan Allah karufa mani asiri kazo kaci kar na shiga uku idan tagano bakaci ba." Jauhar taƙare maganar tana duƙawa agabansa cikin tsantsan tashin hankali haɗe da neman duka alfarmarsa.

Kallon yadda gaba ɗaya tafita hayyacinta yai yana sake mamakin rainin hankali irin na Hajja Maimoon, shi zata bada wannan umurnin akansa sai kace wani ƙaramin yaro? Ya tambayi kansa zuciyarsa na sake kawowa a wuya duk da fushin zuciya ba nasa bane amma yau Hajja Maimoon ta kaishi bango. Kwallar da Alhaji Sha'aban Sada ya hango na shirin sauko mata yasa ya ɗan ji zuciyarsa ta karye, dan tsaf Hajja Maimoon zata iya bin diddigi ta gano yaci abincin ko bai ci ba saboda ta kama Jauhar ɗin da laifin da zata iya mugun hukuntata da ɗaya daga cikin nau'ukan azabar da take bata.

"Mike Jauhar bana so kina ɗaga hankalinki irin haka sai na riƙa jin kamar nima ina zaluntarki, nayi latti sosai zuwa wajen aiki bazan iya tsayawa cin abincin nan ba, amma ke ki ɗauka ki canye kin ji ko?"

Yana gama maganar ya raɓa ta gefenta ya fice ba tare daya sake bata damar yin magana ba, tamkar Jauhar tayi kuka haka ta ji na rashin tsayawar Alhaji yaci abincin, ko ba komai a karan kanta zata so yaci abincin kafin yafita duba da irin taimakon da yayi mata tsakanin jiya da yau.

_"Banda isasshen lokacin ɓatawa na tsaya yimaki bayanin abinda zakiyi, ki tabbatar kin gyarawa Alhaji ɗakinsa idan yafita haka kuma ga breakfast ɗinsa na haɗa masa abinda yake so, bana so kibari yafita da yunwa dan zai iya wucewa idan yafito ya tarar har munci namu mun tafi, ki kasance kusa yadda duk abinda zai buƙata ba sai yayi da kansa ba, hakan zai sa na duba kaso ɗaya daga cikin laifukan ki naga ko zan iya sassauta maki hukuncinsa, ki kula nafaɗa maki kada yafita da yunwa!"_

Kalaman Hajja Maimoon kenan suka dawo mata a kunnuwa lokacin da take bata umurni cike da gargaɗi da kuma jan kunne kafin ta fita. Hakan yasa tayi saurin miƙewa ta nufi kitchen ta janyo wani lunch box ta nufi wajen dining ta zuge zip ɗinta ta kwashe kaf kayan da Hajja Maimoon ɗin ta shirya masa da tasan yana so ta saka aciki ta zuge sannan ta nufi hanyar fita palourn har tana haɗawa da dan gudu ta samu ta isa kafin ya wuce. Cikin Sa'a ta samesa tsaye yana magana da Baba Bello ta ja can gefe ta tsaya tana jiran su kammala. Taku daya Alhaji Sha'aban Sada yai bayan gama maganarsa da Baba Bello Jauhar tabi bayansa har ya shiga mota ya tayar haɗe da ɗan juyowa ganinta a gefensa.

"Jauhar akwai wani abune?" Ya tambaya fuskarsa ba walwala yana kallonta. Sai data dukar da kanta ƙasa sannan ta miƙa masa lunch box ɗin tana cewa.

"Kayi hakuri Alhaji ba wai naƙi bin umurnin ka bane, ka tafi da abincin sai kaci acan dan Allah." Yafi second biyar yana kallonta kafin yace.

"Shikenan saka mani a seat ɗin baya nagode." Cike da jin daɗi Jauhar ta ɗago fuska cikin farin ciki jin ya amince zai tafi da abincin tana jin ta samu natsuwa ta kuma kubuta daga tuhumar Hajja Maimoon da kuma mummunan hukuncinta da za ta yimata idan tasan da rashin karyawar Alhaji kafin yafita. Wanda hakan yasa shima Alhaji Sha'aban ɗin ya amince ya karɓi abincin dan ya fahimci shi kaɗai zai sa hankalin Jauhar ya kwanta. Yana kallon yadda ta sauke ajiyar zuciya kafin ta buɗe murfin motar ta baya ta sanya abincin ta rufe tana cewa.

"Alhaji Allah ya tsare." Sannan ya tada motar ya fice dan tuni Baba Bello ya samu ya buɗe masa gate ɗin. Cike da farin ciki kamar yadda Jauhar ta saba kwana biyu taje ta taya Baba Bello rufe gate ɗin suka rufe tana cewa.

"Baba Bello sannu bari naje na kawo maka abincin ka, ina ga har da rashin cin abinci sosai yasa gate ɗin nan ke nuna maka fin ƙarfi." Taƙare zancen tana dariya amma sai taga jikin Baba Bello ɗin a sanyaye yaje ya nemi gu ya zauna ba tare daya kulata ba. Hakan yasa taji jikinta yai sanyi, taƙarasa kusa dashi walwalar fuskarta na gushewa tace.

"Baba Bello lafiya?" Ta jefo masa tambayar cike da kulawa kasancewar yana ɗaya daga cikin mutanen dake saurin gano damuwarta kuma su bata magana, sai daya ɗauke hawayen da suka zubo masa sannan yace.

"Alhaji ne ya sallameni daga aikin nan Jauhar." Dariya tayi tana cewa,

"To meye na damuwa Baba Bello? Kana bukatar kaje ka zauna ka hutu yanzu bawai kaci gaba da wannan aikin karfin ba da yakusa gagararka. Ranar fa naji Uncle Irfaan yace tun waccan Hajiyar kake gidannan, sama da shekaru kenan ai wallahi kaje ka hutu kawai."

"Bazaki gane ba Jauhar, ba sallamar ce damuwata ba dan yanzu haka yace zai bani isasshin kuɗi naja jari naje nayi duk sana'ar da nake so, ina jin damuwa ne rabuwar da zanyi da mutanen kirki na gidannan, wallahi koda babu albashi zan iya ci gaba da yiwa Alhaji gadi saboda mutumin kirki ne da yasan hakkin ɗan Adam kuma yake ƙoƙarin ganin ya kyautata masa a koda yaushe. Ina da ɗa ɗaya tilo da zai iya zuwa ya maye gurbina acikin gidannan saboda muci gaba da samun rufin asiri, amma tsoro nake ji na kawosa yazo ya tabkawa Alhaji shirme shi da iyalinsa, saboda rashin jinsa." Jauhar dake jin ina ma ace itace zata bar gidan nan yau! Da ƙilan har kukan farin ciki sai tayi. Ta ɗago kai ta kalli Baba Bello wanda har ta soma jin kewarsa tun yanzu tace.

"In dai yana da ƙarfin yin aikin Baba Bello kayi hakuri ka sanar da alhajin sai ka kawosa kada

suje su nemi wani a waje." Ta faɗa jiki a sanyaye,

"Ai nafaɗa masa Jauhar kuma ya amince, damuwata yanzu kar shi yaron yaƙi amincewa saboda ɗan yau ka haifesa baka haifi halinsa ba, ɗan zaman banzar nan da karyace-karyacen da yake faman yi duk zai daina indai har ya amince." Cikin sanyin jiki tace.

"Ka samu ka lallaɓashi Baba sai kaga ya amince."

"Shikenan Jauhar Allah yai miki mafita kema, an jima kafin mutanen gidan su dawo zan je na zo dashi Allah yasa ya amince."

"Amin Baba, Bari naje nakawo maka abincinka." Ta miƙe jikinta duk a sanyaye taje ta kawo masa abincin dan tabbas zatayi kewar Baba Bello itama ba kaɗan ba.....

*ƳAN TAGWAYE BIYAR*

*GONAR SHARRI*
Billy S Fari & Hajja ce

*IDANIYAR RUWA*
(Mai wuyar toshewa)
Ayusher Muhd & Jeeddah Aliyu

*WATA ALAƘA*
Zee Bawa & Stylish bch

*BISHIYAR TSIYA*
(Wanda bai jiba bai gani ba ke girbar ki)
Umm Ashgar & Sadiya Dan.

*TSARIN ALLAH*
(Ba mai iya canzawa)
Asmy b Aliyu & Nana Diso

*ZAI IYA BIYAN*
GUDA 1 akan 500
GUDA 2 akan 800
GUDA 3 akan 1200
GUDA 4 akan 1600
GUDA 5 akan 2000

*BANK ACCOUNT*

8098456130
Opay digital services
Shaidar biya 08098456130

*KATIN MTN*
07065283730
Shaidar biya ta lambar.

#A heart touching story
#Gonar Sharri
#Billy s Fari
#Hajja ce
#Ƴan Tagwaye
[8/1, 9:34 PM] Billy S Fari: *GONAR SHARRI...!*

*PAID BOOK*
*ƳAN TAGWAYE BIYAR*
(Batch C)

NA

*BILLY S FARI*💎
Da
*HAJJA CE*👈

Page 16..

_Bayan kwana biyu_

Abubuwa da dama suka faru  musamman tsakanin Alhaji Sha'aban Sada da Hajja Maimoon data ɗauki ragamar komai na gidanta ta damƙa a hannun Jauhar, ita kuma ta maida gabaɗaya hankalinta ga business ɗinta da ahalin yanzu shagon nata na daya daga cikin shaguna lamba ɗaya da ake ji dasu kuma suke tashe a garin Saboda ingancin kayanta da kuma kyansu, *SUJASU COLLECTION* duk inda kaje shi zaka ji ana faɗa wajen kawo kayan da suka dace daidai da zamani da kuma manya-manyan masu kuɗi dake ji da kansu, wanda yanzu haka direct Hajja Maimoon take odar kayanta daga kasashe daban-daban ba tare data karɓa wajen kowa ba ko kuma tayi haɗin guiwa, gashin kanta take ci da kanta saboda irin cinakin da take samu a kowace rana. Sai hakan yasa ba tada wani lokacin kanta balle kuma na mijinta dan ko yaushe cikin waya da lissafi take, su kansu yaran saboda rashin zamanta gida ya janyo indai ba school tofa suna can tare da ita shago, sai abun ya fara damun Alhaji Sha'aban dan haka zai dawo gida ba kowa sai Jauhar, itace zata yimasa duk wani abu da yake buƙata dan hatta ruwan

wanka ita take haɗa masa yanzun koda Hajja Maimoon ɗin na gida, gyaran ɗakinsa da wanke undies ɗinsa, zuba mashi abinci yaci da gyaran kayansa duk ya koma kanta, wani lokacin har tausayi take bashi amma saboda yana bukatar ayi masa duka wuɗannan abubuwan yake hankurewa yabarta tayi tunda wacce yakamata tayi ɗin batayi ba kuma hakan bai dameta ba.

A ɓangare ɗaya kuma rashin zaman gidan Hajja Maimoon ɗin ya yiwa Irfaan daɗi sosai, sai yake samun isasshen lokacin da yake zaunawa da Jauhar ya karantar da ita addininta dai-dai gwargwado tare da faɗa mata yadda zata riƙa kulawa da tsabtar jikinta dan sai da ita za'a karbi ibadunta, ganin haka yasa Alhaji Sha'aban ya yi magana da Irfaan akan sanya Jauhar islamiya cikin awannin da Hajja Maimoon ɗin bata nan. Hakan yai matukar yiwa Irfaan daɗi yaje ya sanarwar da Hajiya shawarar da suka yanke shi da ƴaƴan nasa, shiru tayi kamar tana nazarin wani abu kafin tayi masu addu'a haɗe da sanya masu albarka tana mai alfahari dasu ko bayan ranta.

Haka Irfaan ya sake zuwa ya ɗebowa Jauhar wasu kayan sai dai ba masu tsada ba da zata riƙa sauyawa ba tare daya damu da wuɗan can daya siya mata ba Hajja Maimoon ta karɓe, ranar data fara saka ɗaya daga cikin kayan baki Irfaan ya saki yana kallonta, Jauhar kyakkyawa ce sosai irin Black beauty sai dai bakar wahala da rashin sutura mai kyau yasa ba'a fahimtar hakan. Wani irin sanyi Irfaan yaji a ransa na ganinta haka musamman farincikin dake dauke akan fuskarta sai murmushi takeyi na jin sabon sauyi a tattare da ita, kasa banbancewa irfaan yai shin da kyan nata da murmushinta wanne yafi tafiyar masa da zuciya? Murmushi ya sakar mata yasa taje ta ɗoro hijabinta akai sannan tazo ta zauna suka fara karatun boko daya fara koya mata shima kafin mutanen gidan su dawo dan yau ma su Jannat nacan tare da Hajja Maimoon ɗin.

Duk wannan abun dake faruwa Hajja Maimoon bata sani ba dan babu abinda ya sauyawa daga biyayyar da Jauhar keyi mata da kuma tsoronta da take ji. Abu daya ta lura dashi sauyin suturar da Jauhar ta samu, wanda tana fara masifa akai Alhaji Sha'aban ya dakatar da ita ta hanyar cewa lallai idan bazata iya bashi kulawar da yake buƙata ba tofa bazai zauna da yarinyar da ita ke kula da cinsa da shan sa da komai nasa ba da ƙazanta, ko dai ta bashi lokacinta ta dawo yimasa duk wani abu da yake dolenta, ko kuma tabar Jauhar dayi masa amma ba'a cikin ƙazanta ba ko kuma ta sallami Jauhar ta dauko wata mai aikin dake da tsabta, amma shi ya gaji bazai jurewa cin abinci da kazantar da Jauhar keda ita ba. Dole Hajja Maimoon tabar zancen dan cikin zaɓi uku ɗin ɗaya bata sam bata jin akwai ɗaya da zata iya karɓa, dama-dama ma taci gaba da zama da Jauhar ɗin a haka tunda ba zaman gidan takeyi ba akan ta koreta ko kuma ta dauko wata mai aikin da bata sani ba tazo ta wargaza mata farinciki ko ta rabata da mijinta. Jauhar kuwa tasan ko a mafarki tsakaninta da mijinta sai kallo.

(Anya Hajja Maimoon! Muje zuwa. Hajja ce da Billy s fari suka faɗa suna sake gyara zamansu).

---

Kusan mintuna goma kenan dattijon nayi masa magana amma yaƙi koda ɗago kai ya kallesa sai wani rangaji da kai yakeyi yana magana can ciki-ciki.

"Iliya dakai fa nake magana wai har sai yaushe zakayi hankali kasan ciwon kanka, kaje ka nanewa yarinya duk da kashe ɗin da ake buga maka amma kaki fita harkarta so kakeyi ka janyo mani masifa, wannan wace irin rayuwace ance kaje kayi aiki ka ƙi sai dauko mani magana kakeyi agari."

"Babcy bafa Iliya ba, Iliyasmaster zaka ce, kuma da kake zancen Huscybaby wallahi baka san irin ƙaunar da nake yi mata ba shiyasa kake cewa na rabu da ita, to naji wa kake so na kula akaf faɗin garin nan idan ba ita ba? Ka fadamun naji Babcy wace yarinya ce tazo dai-dai method ɗina da kuma equal ɗina? Na rantse Babcy ko kai ne a wannan shekarun nawa kaga Huscybaby sai ka kwaye mata, da kuma kake zancen aiki to wabillahillazi bazanyi tsaron gate ba full gaye dani, aiki sai kace gado ka wani ce sai nayi bayan haka nan tunda na tashi kake yinsa amma har yanzu bakayi arziki ba sai ma wane mokaɗewa da kayi tsabar wahala, a haka ma dan Alhajin na kyautata maka ne da yanzu kafi ɗan duƙushi mokadewa har ka son cin nani a wahala na kare kamar kai a matsayin mai gadi har tsawon rayuwata. Gaskiya Babcy na girmi gadi kawai ka bani kuɗi naje naja jari nima ko nayi arziƙi".

Girgiza kai Baba Bello ya yi da kwana biyu kenan da barowarsa wajen aikinsa bayan Alhaji Sha'aban yayi masa sallama mai tsoka tare da kawo wani mai gadin dan har lokacin Baba Bello mai gadi bai samu ya shawo kan Iliyasmaster ba yaje, amma Alhaji Sha'aban Sada yai masa alƙawarin duk lokacin da ɗan nasa yaji yana da sha'awar yin aikin to kai tsaye ya turoshi ba damuwa sai su rikayin duty shi da maigadin da aka kawo yanzu,

"Allah ya shiryeka Iliyasu, ni ba wani master dana sani Iliya na yanka maka da ragon sunan ka shashasha. Da kuma kake zancen kai baza kayi gadi ba mantawa kayi ne dashi na reneka har ka girma ka kawo wannan matsayin da kake jin kai ka girmi gadi? Ni shine rufin asirina kuma yayi mani sutura Alhamdulillah, ya rage naka kayi tunani kaje ka kama aikin nan tun wuri bai kure maka ba ko kaci gaba da zaman banza ana lissafaka acikin ɓata gari da basu san ciwon kansu ba. Husnah kuwa indai a haka zaka zauna daga ni har yan uwana babu wanda zai je ya nema maka aurenta tunda baka san ciwon kanka ba." Baba Bello yai maganar haɗe da miƙewa yabar gidan yana mai nemawa ɗan nasa shiriya da ƙasa ta jima da rufe fuskar mahaifiyarsa, matarsa kuma ba saurararta Iliyas keyi ba balle ta tama shi yimasa faɗa.

Iliyasmaster kuwa sai daya tsaya ya yiwa matar mahaifin nasa surutu da tunda mahaifinsa keyi masa magana bata ce komai ba amma duk da haka bata tsira ba sai cewa yakeyi duk ita ke zuga mahaifinsa ke zuwa yana yimasa faɗa. Nan ma bata tanka shi ba har ya gaji yaja ƙafafuwansa dake saye da takalman da suka zame masa tamkar na karfe yafita.

Bai zame ko ina ba sai anguwar su Husnah, cikin Sa'a ya hadu da ita ta dawo wajen yiwa Umma cefane zata ɗora girki rana dan har karfe sha biyu ta wuce. Washe baki yai haɗe da nufota yana wani jefa kafa tare da watse hannuwa irin na gayu yana kaiwa inda take ya shiga sosa kai irin na munafukai din nan yana cewa.

"Sai ni sai ke Huscybaby, kina shigo kwanar nan wani haske yazo ya dakar mani zuciya, anya

kaf garin nan akwai yarinyar da tayi kyanki da hasken fuskarki?" Dariya Husnah tayi tana kallonsa haɗe da cewa.

"Akwaisu mana ilyas kaine kawai baka ganinsu".

"Ahhhh! Ai ni dama bana son naga kowace mace idan ba keba, Huscybaby kin fa riga kin sace zuciya, duk abinda kike so zan yi maki duniya koda kuwa sama kika ce na hau na ciro maki wata!" Yaƙare zancen yana karɓar kayan hannunta ita kuma ta zaro idanuwa tana cewa,

"Allah Ilyas."

"Toh ko za'a gwada Huscybaby yanzu nafara zo maku da rana kafin dare yayi na dauko maki watan?"

"A'a a haka ma na yarda kana sona." Da haka sukaci gaba da tafiya Iliyasmaster sai tsarata yakeyi da karya kala-kala ita kuma tana hawa, dan ita kalaman ilyas kadai na tafiyar mata da zuciya tare da ƙara mata son sa, sai da suka iso ƙofar gida Iliyasmaster yaja ya tsaya haɗe dayin nildown yana miƙa mata ledar kayan daya riƙo mata. Karba tayi tayi masa godiya sannan ta nufi cikin gida, har ta kusa shigewa cikin ɗaga murya Iliyasmaster ya ware hannuwa irin yadda indiyawa keyi da ƙarfi yana cewa.

"I love youuu Huscybaby, ina san ki." Hakan yasa Husnah da taji saukar muryar tasa da karfi ba zato ba tsammani ta saki ledar kayan mutane data siyo ta runtuma da gudu cikin gida, ilyas na ganin ta saki kayan ta ruga sai shima ya shige gidan aguje yana ihu dan ya zata abun tsoro Husnah ta gani shiyasa ta guduwa, dan haka sai shima yabo bayanta dan ya tsira da kansa. Husnah na zuwa tsakar gida ta tadda Ummanta na shanya kaya a igiya take ta ɓuya tana sauke ajiyar zuciya.

"Ke lafiya?" Umma tafaɗa cike da mamaki, kafin ta bata amsa sai ga ilyas aguje yanayi yana faɗuwa shima  yake fadin.

"Wayyo Umma ɓoyemu." Tare da ƙoƙarin zuwa bayan Umman ya ɓuya, ihu Umma ta saka tana sallallami kafin tayi ƙarfin halin daka masa tsawa dan ta lura kamar bai da hankali.

"Kai ɗan gidan uban waye kai? me tayi maka ne zaka biyota har cikin gidansu? Sallallahu alaihi wasallam wane irin lalaci zan gani haka ni Bilkisu.?"

Sai alokacin Iliyasmaster ya dawo hayyacinsa yana zarar idanuwa yake kallon Umman haɗe da duƙawa ƙasa yace.

"Umma ina wuni? Nifa wallahi tsoro muka ji." Ya sake zaro mata idanuwansa a kanta. Juyawa Umma tayi tana maida kallonta ga Husnah tace,

"Waye shi?" Sai da ta ɗan turo baki sannan tace,

"Ilyas ne Umma baki ji wata ƙara daga waje ba yanzu? Shine fa naji tsoro na gudu." Taƙare maganar tana turo baki,

"Huscybaby ba wata ƙara ai ni ne nake ce maki i love You irin yadda indiyawa keyi." Ilyas master yafaɗa cike da dan jin kunyar Umma data saki baki tana kallonsu.

"Ok yadda indiyawa keyi ko? To jiranki." Umma tafaɗa tana sakin fuskarta haɗe da barin wajen, ilyas da sai aikawa Husnah da wani irin kallo yakeyi ko kunya kawai ya hango Umma ta nufi wajensa dauke da taɓarya. Ai aguje ya tashi ya fice daga gidan Umma na biye dashi tana cewa, "Ashe kai ƙaramin ɗan iskan yaro ne lalatacce, ai da ka tsaya kaga yadda zan dawo maka da hankalinka tunda na lura ba kada shi."

Sai data kai shi har ƙofar gida sannan ta juyo ta samu kayanta watse a tsakiyar zaure mangiɗa da manjan duk sun fashe kayan mutane kuma wajen gudu ilyasmaster ya tattakesu, ai kuwa cike da masifa ta koma cikin gidan tayo kan Husnah tana cewa.

"Ai wallahi baki isa ba maza jeki ki karɓo mani kudin kayan miyana da kuka yimani asara, banda lalaci husnah me zakiyi da wannan yaron da ko kansa bazai iya karewa ba balle ke, wannan ai sauro ne kika kwaso mani ba saurayi ba, dan haka na rantse jeki karbo mani kudina dan bazan dau wannan hasara da takaici ba."

Takoro itama Husnah ɗin daga gidan akan taje wajen ilyas master ya biyata kuɗin kayan miyanta ta kuma kasa ta tsare a tsakar gidan, Husnah na lekowa zatayi kanta ta sake korarta daga cikin gidan...

___

Yau ta kama Friday Hajja Maimoon Bata fita shago ba sai zuwa da marece saboda yanayin yinin ranar da bai cika tsawo ba, zaune take tana yiwa Jannat tsifar kai ita kuma tana latsar waya, kamar ance ta shiga contact sai ga lambar Zain data sakawa _Likita Zain_ ta gani, murmushi ta saki dan tun ranar ta manta da takarbi lambarsa sai yanzu, ɗago kai tayi ta kalli Mommy tana cewa.

"Mommy Dan Allah nakira?"

Ba tare da Hajja Maimoon ta damu da wanda zata kira ba ta amsa mata da eh tana cigaba da tsere mata kan.

Zain na zaune a office ɗin Dr Farouq da suka gama ganin patient tare yana ta mining na Notcoins da yakeyi wanda shine dalilin yawan latsar wayarsa da Abban nasu ya tsana in dai yana shi kaɗai sai ga kiran Jannat ya shigo.

Kasancewar baƙuwar number ce bai santa ba sai kawai yai minimizing yaci gaba da mining

ɗinsa da lambobin suka nuno million goma da dubu ɗari tara da hamsin da bakwai a screen ɗin wayar, wanda hakan ke nuni da tabbas yana gab da cimma burin da yake dashi akan wannnan crypto din na Notcoins shiyasa ya dage sosai haɗe da maida hankali dan ya cimma point ɗin da yake buƙata. Sake kira akayi a karo na uku wanda hakan yasa yai minimizing game din ya ɗaga kiran. Ji yai ta cikin wayar ance .

"Hello likita Zain." Ana dariya alamun mai kiran taji dadɗin ɗagawarsa, shiru yai jin muryar yarinya ce yana son tuna inda yasan muryar kawai yaji tace,

"Common likita Zain Jannat ce, the Mommy's doughter fa." Ta ƙara masa da sunan da yai mata yadda zai fahimta. Murmushi Zain ya saki tare da cewa.

"Mommy's doughter kece? Kina lafiya?"

"Lafiya kalau likita ya aiki?"

"Alhamdulillah ya jikin naki kin warke sosai ko?"

"Eh daga ranar nan sake jin ciwo ba asibiti ku nada kyau kun iya kula da marasa lafiya."

"Nagode ina ɗayar yar uwar taki? Itama taji sauƙi ta warke sosai?" Gefen kitchen Jannat ta kalla da Jauhar ke ciki tana haɗa lunch tace,

"Ni kadena kiranta yar uwata bamu da hadi da ita yar aikin mu ce."

"Allah ya baki hakuri tunda bakya so na tambayeki ita to kibata wayar sai naji ya jikinta." Jannat bata kawo komai a ranta ba ta ƙwalawa Jauhar kira tana turo baki, Hajja Maimoon kuwa tuni ta gama tsefe mata kan dama ta ɗaure ta koma akan system ɗinta da tasa Suhana takawo mata tana tura kayayyakin da take so akawo mata a next odar da tayi, shiyasa bata maida hankali ga abinda Jannat ɗin keyi ba har sai da taji tana cewa.

"Kiyi magana yana jinki kada ki tabawa Mommyna waya."

Dai-dai lokacin Irfaan ya shigo palourn da saƙo Alhaji Sha'aban Sada yasa ya kawo, daga Hajja Maimoon ɗin har Irfaan zuba idanuwa sukayi cike da mamaki suna jiran suji muryar wanda Jannat ke cewa Jauhar tayi magana dashi da tasa a handsfree, cikin kulawa Zain daya ciro wayar yana kallo yaga ana online har lokacin yace.

"Hello ƙawata ya jikin naki kin warke ko azo ayi maki allura."

Ya yi maganar cike da barkwanci kamar yadda ya saba ga marasa lafiyan da yake kula dasu. Jauhar na jin haka ta zaro idanuwa tana ɗan ja da baya, haka Irfaan cikin ɓacin rai yake kallon Jauhar ɗin yayin da Hajja Maimoon itama ta zaro idanuwa tare da miƙewa daga wajen zamanta

cike da wani matsanancin ɓacin rai daya bayyana ƙarara akan fuskarta ta nufo wajan...

_LAST FREE PAGES_

_*Hmmm..! Tirkashi! Yanzu fa labarin zai fara*_

_*Wacece Hajja Maimoon?*_

_*Wace alaƙa ce tsakaninta da Jauhar?*_

_*Shin ina iyayen Jauhar suke?*_

_*Menene dalilin da yasa Hajja Maimoon ke azabtar da Jauhar har take iƙirarin dole akayi mata tare da tirsasata zama da ita ɗin?*_

_*Shin Jauhar zata samu ƴantuwa daga ƙangi bautar da takeyi ko kuwa?*_

_*Ina labarin Irfaan? Shin zai iya zamema Jauhar bango ko kuwa?*_

_*Menene matsayin Zain a cikin labarin nan?*_

_*Ilyasmaster zai auri Husnah ko kuwa? Meye matsayinsa a labarin?*_

_*Shin ina dangin su Hajja Maimoon suke? Meyasa basa zuwa inda take ne? Ko ita Hajja Maimoon ɗin bata zuwa inda suke?*_

_*A ina suka haɗu da Alhaji Sha'aban, wace irin rawa yake shirin takawa acikin labarin nan?*_

*Abubuwa da yawa suna cikin labarin nan wanda zasu baku mamaki da al'ajabi. Mu kanmu munyi iya kokarin mu wajan tsifewa da kuma tacewa dan samun darasi a cikinsa. Bamuyi labarin nan da ka ba sai da mukayi bincike muma muka samu tarin ilimi a cikinsa. Karki bari karanta labarin GONAR SHARRI ya wuceki. Daku muke ko muce dakai muke mai son ƙara samun ilimi. GONAR SHARRI ya cika sunan nasa idan har kuka karanta daga farko har karshe*👌

*Domin samun duka waɗannan amsoshin kutaho muyi tafiyar atare ku masu karatu. Gamai son cigaban wannan littafin zai biya ₦500 kacal ta wannan account*
BANK ACCOUNT
8098456130
Opay digital services,
shedar biya ta  wannan number 07040402435 ko kuma a kira kai tsaye dan karin bayani, idan muka kammala rubuta complete document ɗin littafin zai koma ₦1000 in Sha Allah*

Mungode.

#A heart touching story
#Gonar Sharri
#Billy s Fari
#Hajja ce
#Ƴan Tagwaye